[7/17, 10:04 AM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE1️⃣_2️⃣*
...Gagarumin hadarin da yayi ma garin ƙawanya ne ya haɗe da duhun dare ya sake haddasa ma garin wani irin matsanan cin duhu mai matuƙar ban tsoro.

Mace ce yar kimanin shekaru  talatin da wani abu, amma sam yanayin jikin ta bai nuna shekarun ta sakamakon hutu daya ratsa jikin ta, Zaune take ita da HIBBA yarinya yar kimanin shekaru goma sha bakwai kallo suke ita da mahaifiyar ta ta.

Iskar da taji ya fara kaɗawane alamun ruwa zai sauko ya sake ɗaga hankalinta, gashi dai Abban hibba bai dawo gida ba ga kuma hadari da ke kara ɗaga mata hankali.

"Umma bacci nike ji nidai sai da safen ki."
Hibba ta fada tare da nufar ɗakin ta.

Wata ajiyar zuciya Haj Murya ta sauke, domin harga Allah tana matuƙar ƙaunar Hibba ɗiya ɗaya rak da suka mallaka, son da bata taba yima wata halitta ba, amma yanzu tsoron Hibba  take tamkar yadda take tsoron mutuwar ta, saukar ruwan ne da mugun ƙarfi ya sanya ta wata iriyar zabura ta miƙe tare da shiga dakinta ta haye gado tana waige_waige.

"Alhaji! Alhaji dan Allah kadawo, innalillahi wa'inna ilaihirrajiun, ka ƙi yarda dani kaƙi gasgata maganar da nike fada maka akan HIBBA."
```

Wutar ɗakin ce ta fara farfarniya.

Blanket ta bude tare da shigewa jiki na kyarma, taku taji an farayi alamun ana nufo inda take ga kuma ƙarar ruwan da ake sheƙawa da ta cika ɗakin.

Addu'a ma ta kasa zufa ce kawai ke tsiyaya a jikin ta ga wata kyarma da take tamkar gadon zai karye.

Cak taji komi ya lafa sai dai ruwan da ake shekawa har yanzu kamar da bakin kwarya.

Wani bacci taji yana fizgarta bata san lokacin da ta fara gyangyaɗi ba.

"HIBBA karki kasheni, kin manta nice na haifeki, ashe dama ɗiya zata iya kashe Mahaifiyar ta."?
Haj Murja ta karasa maganar tana kara shigema bangon ɗakin domin sun kawo inda babu yadda za'ayi ta gujema HIBBAH.

"Hahaha Umma! Bani da wani buri daya wuce inga na rabaki da rayuwarki, Umma abinda kika shuka shine zaki fara girba dole ki mutu, musha jininki."
HIBBA ta karasa maganar tare da  nufar mahaifiyar ta da wuƙa tsirara.

"Innalillahi wa'inna ilaihirrajiun."
Haj MURJA ta furta  domin mafarkin yau ya kazanta fiye da na baya.

"Alhaji kana ina yau har yanzu baka dawo ba."
Miƙewa tayi da nufin barin ɗakin.

Ƙafafunta aka wawura tare da bugata da bed side kanta ya bugu, tsabar ruɗewa da kwalwar ta tayi ƙokarin shigewa karƙarshin gado ta fara.

"Kul! Kika ce zaki guje mana."
Ta jiyo wata murya wadda ko tantama batayi muryar HIBBA ce, kanta dake mata wani matsanancin raɗaɗi ta ɗaga tare da kallon HIBBA dake zaune da wasu jajayan kaya ta juya mata baya.

"Hib...bba..."
Bakin Haj MURJA ya kasa ƙarasa sunan illa jikin ta dake kyarma.

Dariya aka kece da ita dakin ya ɗauki amsa kuwwa, garam! ƙofar ɗakin ta rufe kanta.

Juyowar da HIBBA zatayi Haj MURJA tayi arba da abinda bata taba gani ba, domin rabin fuskar HIBBA ya ru6e tsutsotsi ne ke fita suna cin naman fuskar ga wasu idanu kwala_kwala kaf suffar ta ta juye ta koma abin tsoro.

"Hahaha kin gama mafarki na yanzu kuma gani nazo maki a zahiri."
Cewar HIBBA cikin wata iriyar murya mara daɗin saurare.

"HIBBA mi nayi maki kike azabtar da rayuwata, kin manta ni nayi dakon cikin ki na haife ki nayi renonki har kika kawo lokacin nan kike ƙoƙarin kashe ni, mina aikata maki."?

"Ke ba abin tausayi bace Umma ko baki so sai na kashe ki sannan zani samu salama, babu wanda nike ji na tsana kamarki Umma, dan haka yanzu zaki bakunci Lahira."
Tana kaiwa nan ta shaƙi wuyan MURJA da hannu ɗaya tayi sama da ita.

Sai da ta tabbatar ta daina numfashi sannan ta sake ta tare da barkewa da mahaukaciyar dariya ta bace 6at.

Turo kofar yayi tare da yarfe jikinshi da ruwa yayima duka, cak! Ya tsaya ganin matar tashi baje tamkar gawa, a guje yayo kanta yana mai ambatar sunanta.

Ganin shuru yasa shi kwalama HIBBA kira, a guje tayi cikin dakin domin tasan wannan kiran da Mahaifinta ke mata bana lafiya bane.

HIBBA kam a rikici take jijjiga mahaifiyar ta tare da kiran sunan ta "Umma...

---

"Mama da Allah dan Girman Allah kada ki yanka mani hannu, Mama miyasa baki sona dan Allah in laifi nayi maki ki sanar dani in baki hakuri ki yafe mani dan Allah."
Cewar LUBNAH tana mai sanya ɗayan hannun ta tare da rufe gefen fuskar ta dake barazanar bayyana.

"LUBNA nina haifeki amma na tsaneki, bani sonki bani kaunar ki, tun lokacin dana ga halittar dake tattare dake, badan kada in kasan ce Uwa ta farko data data kashe diyar ta ba LUBNA da wukar nan a cikin ki zani caka maki ita kowa ya huta, na aikeki dibar ruwa kin fasa mani bokiti in ban yankeki ba yau raina bazai mani sanyi ba."
Cewar GAJE dake rike da wuƙa ta saka ɗiyarta a kona.

Dayan hannun ta tasa tare da dafe Rabin fuskarta dake rufe da kallabin dake kanta.
"Mama indai zakiji sanyi a ranki na yadda ki yi mani hukumci."
Ta karasa maganar tare da fashewa da kuka.

"Ko baki ce ba LUBNAH sai nayi maki hukunci."
Ta karasa maganar tare da yanka damtsen hannun LUBNA.

ƙara ta saki lokacin da taji kaifin wukar ya ratsa tsokarta ya rabata biyu.

"Gobe ma ki kara fasa mani bokiti, kuma maza ki dauki bokiti keje fanfo ki dauko mani ruwa."

LUBNA azabar da hannunta ke mata kasa tashi tayi hawaye suka ci gaba da zuba ta gefen fuskar ta inda bata rufe ba, da kyar ta mike tare da shigewa matsakaicin dakin nasu mai dauke da katifar kwanansu sai kuma wani miro da buhun nan kayan sawar su.

LUBNA ba zata haura shekaru sha bakwai a duniya ba, baka taba gane shin tana da kyau ko akasin haka domin kullum rabin fuskarta a rufe yafe da gyale.

Gaban miron taje ta tsaya tare da fashewa da kuka tayi wurgi da gyalen dake saman kanta nan fuskarta ta bayyana.

INNALILLAHI WA'INNA ILAIHIRRAJI'UN shine abinda na furta lokacin da nayi arba da fuskar LUBNA, Rabin fuskarta ta mata ce Rabi kuma fuskar namiji ce, a taƙaice dai fuskar ta an daga tsakiya an rabata bangare daya ta mace bangare daya kuma fuskar namiji ce.

Hannuwan ta biyu tasa tare da shafar fuskar tata tana mai fara wani sabon gunjin kuka.

"Ya Allah banyi butulci ba ina godiya da wannan halitta da ka yi ni da ita tun farkon   tashi na bansan daɗin uwa ba an haifemu mu biyu amma abokiyar tagwaici na kadai mahaifiyar mu ke nuna ma soyayya, uwata ta tsane ni mutanen gari sun tsaneni Allah nagode maka da wannan baiwa da kayi mani."
Ta kasa karasa maganar sakamakon wani kuka daya tokare ta.

Kallon miron take bangaren fuskar macen na zubda hawaye, bangare fuskar bamijin ce taga ta fara mata murmushi, wani sabon kukan ta sake fashewa dashi.

"LUBNA in na iske ki cikin dakin nan wallahi kashe ki ne kaɗai baniyi."
GAJE ta faɗa  daga waje.

Gyalenta ta maida tare da rufe rabin fuskar ta tare dayo waje, "ki fara share gidan nan kafin ki ɗebo ruwan"
GAJE  ta faɗa a tsawa ce.

Kasan cewar gidan na masu karamin ƙarfi ne tsakar gidan ko shafe babu sai jar kasa dake baje, daga bakin baranda kuma a shafe yake.

Tsintsiyar kwakwa ta dauka tare da fara sharrar gidan hawaye nabin rabin fuskarta.

Kammala sharar tayi da hannunta dake ɗigar jini domin har yanzu yankan da mahaifiyar ta tayi mata bai bar zafi ba, bokiti ta dauka tare da nufar Fanfon dake cikin unguwar su.

Tana fita yara suka fara kiranta Ruwa biyu suna shigewa gidajen su a guje.

Abokiyar tagwaicin ta ce ta hango suna tafe ita da ƙawayen ta.

"Kulu dan Allah ki amsa ki ɗebo mani ruwa hannu na bani iya wa."
Cewar LUBNA

Wani kallon wulakanci Kulu tayi ma Lubna.
"Ke dalla gafara ki bani wuri, har ni zaki kalla kice in ɗebo maki ruwa, to koda kina ganin tare

aka haife mu wallahi na tsane ki LUBNA, ke nifa ina ji a jikina zani iya kasheki kowa ya huta."
Kulu ta karasa maganar cike da nuna zallar ƙiyayya.

Sauran Ƙawayen KULU kecewa suka yi da dariya.
"Nikam Kulu, wai wannan yayar taki kodai mata maza ce? Ace mutum fuskarshi rabi ta mace rabi ta namiji."
Sake kecewa suka yi da dariya.

Wata hatsabibiya ce ta fara magana.
"Ke nifa Kulu duk da wannan halittar yayarki ce bazai hana mata rashin daraja ba."

Bangaje ta suka yi tare da barin ta nan kasa, ganin bata da mafita yasa ta mike dafe da hannun ta dake mata raɗaɗi.

A hankali tsokar jikinta ta rika haɗewa ciwon na haɗe kanshi, kallon hannun take domin hakan ba yau aka fara ba.

"Ba zani bari kowa ya taba sonki ba, duk wanda ya soki mutuwa ce hukuncin shi "
LUBNA taji an rada mata a kunne.

Kafin ta ƙarasa wurin fanfon haka yara suka rika janta suna kiran ta RUWA BIYU.

Inda sabo ta saba da ƙiyayyar da kowa ke nuna mata, amma ita ƙiyayyar da tafi damunta i ta ce wadda mahaifiyar ta ke nuna mata, tunda take bata taba samun soyayya ba daga mahaifiyar ta, makaranta ma kowa ya tsane ta, mahaifinta kaɗai kesonta

Zuwanta bakin fanfon tayi sa'a bata iske kowa ba, dan haka duƙawa tayi domin ɗibar ruwan,
"yar baƙa ruwa biyu"
Wani yaro ya faɗa tare da yin boll da bokitin da take ɗibar ruwa nan take ruwan ya bare shi kuma ya ruga a guje.

Kasan cewar yanayin fatar ta baka ce wadda ake kira black beauty, cike da damuwar wannan abu da kowa ke mata ta ɗauki bokitin tare da sake ɗora shi ta shiga buga monon.

Su Goga ne suka zo wucewa ta wurin monon kasan cewar inda take ba cukowar mutane.

"Kai! Goga kamar fa yarinyar can ce nike gani."
Ɗan taure ya faɗa cikin muryar yan daba.

"Ahh! Alƙur'an i ta ce, kai tsuntsu  daga sama gasasshe, Alafiya dai Goga ya kace ne."?

Wanda aka kira Goga ɗaga kai yayi tare da ƙare mata kallo, gefen 6aren fuskar ta da ta rufe ne yaji yana muraɗin ganin abinda ta rufe.
"Ku zo muje."
Goga ya faɗa tare da yin gaba.

Tsattsaye ta gansu gabanta sun kewaye ta, nan fa jikin ta ya hau ciri.
"Dan Allah kuyi hakuri, kuzo ku ɗiba ni na gama."

"Dillah gafara can, munafUka wannan lullu6in da kika yi zaki bude muga wace uwar ce kike rufewa."

"Innalilahi wa'inba ilaihirrajiun Baba kana ina."?
Ta karasa maganar tana mai ƙara sanya hannu tare da danne 6arin fuskar ta.

"Ah! Kajifa Goga wai Cus ɗinta take kira, izininka nike jira Goga yanzu in ƙaddamar mata."
Ɗan taure ya karasa maganar yana tangaɗi.

"Kubar munafuka yau sai ta bude wannan lullu6in munga mi take rufewa."
Goga ya faɗa tare da Sanya hannu ya fizge gyalen da ta rufe fuska.

Wata ƙara ta saki wadda ta haddasa masu faduwar gaba, ba shiri suka sanya hannayen su suka toshe kunnuwan su.

Kafin su yi wan kwakkwaran motsi ta zube ƙasa tayi ruf da ciki tana wani kurnani tamkar yunwatacciyar zakanya.

Burinsu dai kam bai cika ba domin dai LUBNA a ruf da ciki ta faɗi basu samu ganin fuskarta ba.

"Mu zaki yima akuyan ci, Oga mu ai munfita zama yan akuyoyi, ku jira ku gani."
Ɗan taure ya karasa maganar tare dayin inda taka kwance.

Ɗaga kafar da zaiyi sai ji suka yi an kece da dariya Mahaukaciyar dariya da ta haddasa ma wurin amsa kuwwa...

_Ina dai ƙara tuni, kibi littafin nan tun yanzu kada inyi nisa a rika pls daga farko_

*MEEN@T...✍🏻*
08133562798
[7/18, 6:19 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE 3️⃣4️⃣*
...Tun daga bakin Get babu abinda kaje ji face amon waƙa daya karaɗe ilahirin gidan, abinda zai baka mamaki shine yadda Volume ɗin waƙar yayi matuƙar yawa.

Hajiya Salima dake bacci sakamakon ciwon kan daya addabeta firgigit ta farka tare da nufar ɗakin ɗan nasu dan tana da tabbacin shine ummul aba'isin faruwar haka.
```

Turus! Taja ta tsaya jikin ta har ciri yake, lokaci ɗaya ciwon kan dayafi na ɗazu ya sake yi mata dirar mikiya.

Da sauri ta dafe kanta dake mata barazanar tarwatsewa, tare da jingina da bangon ɗakin sakamakon wani jiri da taji yana ɗibarta.

Ba komi bane ya haddasa mata haka face AL'AMEEN da ta gani tare da wasu kyawawan ƴan mata da basu da marasa da karuwai kusan su huɗu sun baje suna ta shan shisha, kayan jikin su kaɗai zaka kalla ka tabbatar da ko a cikin Karuwai to su sun shahara.

"Innalillahi wa'inna ilaihirrajiun, AL'AMEEN!."

Sunan shi data kira ne ya ankarar dasu cewar wani ya shigo, bata rai yayi domin har ga Allah in yana huta da bebs ɗinshi hatta wayar shi kashewa yake.

"Mom ya zaki shigo mana wuri babu Sallama, bayan ke kike kwaɓata akan indai na shiga wuri ba Sallam."
Ya ƙarasa maganar tare da shuno baki gama.

Cike da tsabar baƙin ciki Haj Salima taji wasu hawaye nabi fuskarta.

"AL'AMEEN mi kake son ka zama, yanzu har takai ka riƙa kawo mana mata cikin gida, AL'AMEEN kana so baƙin cikin ka ya kashemu kowa ya huta."?
Ta karasa maganar wani tuƙuƙin baƙin ciki na taso mata daga cikin zuciya.

Ƙasa da kai yayi yana gunguni, su kuma matan sunyu fiƙi_fiƙi da ido, "zaku fice daga gidan nan kosai na haɗaku da security."?
Cewar Hajiya Salima rai a matuƙar ɓace.

Sumi_sumi suka tattare kayansu tare da rabata suna wucewa sai wata daya da ta tsaya kusa da AL'AMEEN wadda daka kalli idon ta kasan ta shahara.

Kallon AL'AMEEN tayi tare dayin farrr da ido. "Baby sai mun haɗe muyi waya kawai."
Ta karasa maganar tare da jifar Mahaifiyar Al'ameen da mugun kallo tare da ficewa.

Binta yayi da kallo dumin duk cikin yan matan shi yana masifar ƙaunar LEEMCY saboda irin fararen matan nan ne da suka haɗa da bleaching har yellow fatar su keyi, shi ko a duniya farar mace duk yadda take mugun ƙaunar ta yake sabanin baƙar mace da yayima wata iriyar muguwar tsana duk kyawun ta kuma.

"AL'AMEEN!."
Mom ta kira sunan shi, "Ka iske ni ɗaki."

"Nifa fisabilillahi Mom bacci nike ji in na gama zaki ganni."

Bata tsaya saurarar wannan kayan takaici ba barin ɗakin tayi rai a matuƙar bace.

Bakin gadon ta ta zauna tare da fashewa da wani irin kuka mai tsuma zuciya.
"Ya Allah kana gani Allah kai ne sheda tun yana yaro tarbiyyar daka koyar damu mu tarbiyyanci yaran mu da ita muka tarbiyyance shi, Allah kai shedane bamu saki rayuwar AL'AMEEN sakaka kamar yadda masu kuɗi ke sakin yaran su ba, munyi iyakar yinmu iyakar ƙoƙarin mu, amma tun tasowar shi yaro ne dabai jin magana tarbiyyar da muke bashi tamkar bashi muke bawa ba, Ubangiji ka shirya mana mana AL'AMEEN domin shiriya taka ce, ya ALLAH mun ɗauki wannan jarabawa da kayi mana da hannu bibbiyu ba zamu yi butulci ba ALLAH  kai mai gafara ne ALLAH ka shirya mana shi dama sauran yara na Al'ummar musulmi."
Kukan daya ci ƙarfinta ne yasa ta kasa ƙarasa maganar.

Cike da tausayin matar tashi ya ji wasu siraran hawaye sunyi nasarar kubce mashi,  tun shugowar ta dakin yake bakin ƙofar tsaye, halinda take cike ne ya hana ta ganin shi.

Gefen gadon ya zauna tare da share mata hawaye, "Mu muka ma Ubangiji lamurranmu kada muyi garaje mU kasa cinye wannan jarabawa, Hajiya nasan kina haɗiyar gubar AL'AMEEN a cikin gidan nan, amma mu ƙara haƙuri tare da dagewa da addu'a, komi lokaci gareshi."

Jingina tayi da mijin nata da take kallon shi a matsayin Uwa da kuma uba agareta.
"Ni dakai ƙuruciyar mu mai kyau mukayi ba muyi abinda AL'AMEEN keyi ba, amma shi..."
Saurin rufe mata baki Alhaji yayi tare da girgiza mata kai.

"Mu ƙara haƙuri, komi lokaci ne, nasan ki da hakuri da kuma juriya."
Nan ya shiga rarrashin ta har ta daina kukan sai kuma ajiyar zuciya da take saukewa.
"Ya kamata ka tafi wurin Mariya kasan kwanan tane kasan halinta ka tafi kada tazo ta tayar msna da hankali."
Cewar Haj Salima.

Harga Allah Alhaji Sufyan yana matuƙar ƙaunar fiye da Mariya, Salima mace ce mara haƙuri hatsabibiya.

"Mar'atu saliha, kullu yaumun ina kara godiya da Ubangiji ya mallaka mani ke a matsayin mata, sam baki barina inyi rashin adalci a tsakaninku."
Murmushi tayi domin inda sabo ta saba da wannan yabo da mijinta ke mata.

Hajiya MARIYA dake la6e bakin ƙofa tana jin duk wata magana da suke wani murmushin mugunta ta saki.
"Dani kuke magana, ni in haifi mace a cikin gidan nan daga zuwan ki ki haifa namiji, fata shine AL'AMEEN ya ƙara lalacewa fiye da haka in so samu ne ma ya zama ajalinki."
Ta karasa maganar tare da barin wurin sakamakon tafiyar Alhaji da taji.

AL'AMEEN kuwa yana gama baccin shi wanka yaje yayi tare da shiryawa kota kan Mom dake jiran shi bai bi ba ya dauki key ɗin motar shi tare da fitowa, saurin yin baya tayi ganin sun kusa yin karo da juna.

"Kee!"
Ya furta rai a bace.

Hannu ya daga tare da zabga mata wani lafiyayyan mari da yayi sanadin ɗaukewar ganin ta na wicin gadi, ruɗewa tayi tare da faduwa kasa.

"Hanne ni zaki kusa bankewa kin taho kai sama kamar tunkiya, bana ce kada ki sake in ƙara haɗa hanya dake ba, banza bakar mace kazama dake in kika sake na sake hada hanya dake jikin ki ne zai gaya maki."
Ya karasa maganar tare dayin Boll da ita yayi gaba

Inda sabo Hanne mai yima hajiya Salima hidima ta saba da halin shi.

Abinda zai baku mamaki shine fatar jikin AL'AMEEN ba fara bace baƙace irin ta mahaifin shi domin bai biyo mahaifiyar shi data kasan ce fara ba, amma minahikin ya tsani baƙar mace😎.

A fusace yaba motar wuta, da gudu mai gadi ya buɗe get dan yasan ba wuya yasha mari wurin ɗan masu gida, tamkar zai bi ta kan mai gadi haka ya fice da motar a guje.

---

..Duk wata dabara da taimako da ake ba mutum inya suma to Abban Hibba ya yima Hajiya Murja amma shuru kake ji.

Tun abun bai fara bashi tsoroba har yazo ya fara tayar mashi da hankali, saman gadon suka mai data.

"Kina ina wannan abun ya faru da mahaifiyarki."
Cewar Abban Hibba.

"Abba ina daki na, tun kafin tasowar hadari nayi bankwana da ita nata fi na kwanta, kiran da ka kwala mani ne nazo naga halinda take ciki."

A jiyar zuciya ya sauke domin harga Allah kwanan nan ya rasa gane kan Matar shi, ganin irin ruwan da ake tsulawa ne yasa bai kira likita ba ya jinkirta gari ya waye.

"ABBA ni bacci nike ji sai da safe."
Hibba tayi gaba ba tare da bi takan Mahaifiyar ta dake kwance batasan wanda ke kanta ba.

Cike da mamaki yake kallon abinda Hibba ta aikata, kasanceqar shi ɗan boko sai kuma wata zuciyar tace mashi lokacin bacci ba'a hadashi da komi."

Dan haka sai ya dena ganin laifin HIBBA, shi ya kwana kan Hajiya har gari ya waye bata farka ba.

Bayan dawowar shi masallaci yana zaune kusa da ita domin harya kira Family doctor.

A firgice ta farka tare da ƙanƙame shi, "Wallahi i ta ce, kashe ni zatayi Hibba ce, wayyo Allah na

nikam na shiga ukkuna."
Ta karasa maganar tare da sakin kuka.

"Ki natsu wace ce zata kashe ki."?

"HIBBA ce ita ce zata kashe ni ka taimake ni."

Sakaka ya tsaya yana kallon ta.
"Ya isheki."
Ya daka mata tsawa.

"Shin sau nawa zan gargaɗeki da ki ƙara jifan ɗiyata da wannan kalmar, shin kodai kwalwarki ta samu matsala ne, wani Aljani wani surutai can Hausawa ku kuka sanshi, mu maleriya muka sani kuma nasan ita ce ke damun ki, ga likita nan zai zo ya dubaki, ina mai kara gargaɗinki da kidai na jifar jinina da wannan kalmar can kuka san wasu aljanu."
Ya barta nan sake da baki.

Wasu sabbin hawaye taji suna bin fuskar ta.
"Yau ta fahimci abinda mahaifiyar ta ke nuna mata tun lokacin da mutane biyu suka fito neman auren ta, marigayiya mahaifiyar ta taso ta auri Bashir wanda ya kasance mai addini amma baida kuɗi, in da murja ta nace ita sai  Alhaji abdallah, ashe dama irin wannan ranar mahaifiyar ta ke hasko mata gashinan yama ki yadda akwai wata halitta wai ita alaja."
Ganin batada wata mafita yasa ta sauko daga saman gadon tare da fadawa toilet tayo alwalla tare da kabbara sallar asuba.

Gama Sallar tata keda wuya likita ya karaso har cikin ɗakin likitan ya shugo ya duba ta tare da yi mata VP nan yaga jinin ta ya hau.

Magunguna ya rubuta da za'a sawo mata tare da fatan samun lafiya, shigowar HIBBA ɗakin yasa Hajiya Murja daburbucewa ta rasa mike mata daɗi.

"Umma ya jikin."?

"Da..dada.. Da sauƙi."
Ta amsa murya na kyarma.

Ɗago kanda zata yi idanunsu suka haɗu, da sauri ta kauda kanta ganin HIBBA na mata murmushi ga wasu haƙora masu matuƙar tsini sun bayyana a bakinta.

Duk Hajiya Murja ta rasa sukuninta, ganin an kwana biyu babu abinda ya faru yasa ta fara sakin jiki da HIBBA.

Zaune take bakin gado tana char da wata babbar aminiyar ta, saman screen ɗinta ta kalla nan taga biyar da rabi na yamma lokacin sham maganinta yayi, lalace ya hanata motsawa ta ɗauki maganin dake bisa bedside, HIBBA ta fara ƙwalama kira tazo ta ɗauko mata.

"HIBBA zoki miƙo mani maganina lokaci yayi."

"To Umma taji an amsa mata."
Shigowa tayi sanye da wata bakar riga kai babu kallabi.

"Umma gani."
HIBBA ta faɗa.

"Ke bake Umma ke kira ba dani take."
Wata Hibba Sak tafito daga Toilet ɗin Hajiya Murja ta faɗa.

Wayar dake hannun Hajiya Murja Suɓucewa tayi cike da tashin hankali take kallon HIBBA data rabu gida biyu suna tsaye gaban ta.

"Aa duk ƙarya kuke nice nan Umma ke kira."
HIBBA cikon ta Ukku dake ƙokarin shigowa ɗakin ta faɗa.

Su duka HIBBA da suka rabu gida Uku garda suka farayi kowa na cewa ita ake kira.

Hibba ta farko cr tace
"Ku jira mu duka UMMA ke kira dan haka mu karasa wurin ta."

Gaba daya ukkun kecewa suka yi da dariya suka yi a tare suka haɗa baki "UMMA gamuuu...

---

...Tun bayan shigowar shi gidan har kawo yanzu da duhu ya fara baiga LUBNA ba.

"GAJE! ina yarinyar nan take har magriba tayi banga gilmawar ta ba."
Cewar Mahaifin su LUBNA.

Sai da tayi kamar ba zata tanka ba sannan ta buɗe baki a wulaƙance da nuna baka isa ba tace.
"Nifa kada ka isheni da tambaye_tambaye LUBNA na aiketa debo ruwa saboda tsabar ita ɗin shegiya ce har yanzu bata dawo ba."

"Ya isheki GAJE."
Ya faɗa a tsawa ce, duk da shi mutum ne mai matuƙar haƙuri amma yau Gaje ta kawo shi wuya.

"Allah wadarai hali irin naki, kina bani mamaki ɗiyar cikin ki kike kira shegiya, wa'iyazubillah, badan a gabana kika haifa su LUBNA ba tabbas da bazani yarda kece mahaifiyar ta ba, kin tsani diyar da ta kasan ce ta cikin kinki, halittar da tazo duniya da ita bayin kanta bane lokacin da zata zo duniya ba zabin halitta aka bata ba Allah shiya yi ta a haka amma kin kasa ganewa mutanen unguwa su nuna mata tsana da ƙiyayya kema ki nuna mata Gaje kiji tsoron Allah."

"Kaga in wa'azi kaje ji kaje gidan redio amna ni GAJE na tsani LUBNA na tsani in ganta a kusa dani, kai in takai ce maka magana so nike inga LUBNA tana wulaƙanta a rayuwa."

Tsabar bacin rai kasa magana yayi, face wani tuƙuƙi na bacin rai dake taso mashi.

Rikica! Sukaji faduwar wani abu, a guje yayo bakin ƙofar ganin LUBNA cikin wani hali zube a ƙasa.

"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un GAJE kinga abinda kika jaza mana ko ciwon ta ya tashi, kizo mu samu a sata ɗaki kafin ta rikice."

"Wallahi ta mutu bani da matsala, ke Kulu tashi muje ɗaki mu kulle in ta gama haukanta mu dawo."
Ɗaki suka shige suka kulle suka bar malam nan rike da LUBNA.

Idon ta na bangaren mace ne ya fara rufewa, a galabaice ta buɗe baki.
"Baba kai ma ka gudu ka sake ni kada in cutar dakai, dan Allah Baba ka gudu."
Ta fada bangaren fuskarta na namijin na fara canza launi.

"Ba zani barki ba, bani iya barin ki har abada koda zaki zama sanadin mutuwa ta, LUBNA ina tare dake nafiso duk wahalar da zakisha musha tare, Ina sonki a duk yadda kike."
Ya karasa maganar hawaye nabin fuskar shi.

Jikin tane ya saki lokaci ɗaya ta fara wata kyarma, facewa da kuka Baba yayi tare da kara ƙanƙame LUBNA tamkar za'a kwace mashi ita.

Farautan ta dake zaƙo_zako suka fara tsayi jikinta na malƙwashewa, ƙafafun ta kuwa harbe_harbe kawai take take ƙasar wurin ta hau tashi.

Miƙewa tayi zaune tare da far kartar mahaifin nata da akaifunta da suka yi zaƙo_zaƙo tana ƙoƙarin kwacewa.

Jiyo ihun LUBNA da makwafta keyi ya sasu shigewa gidaje tare da kullewa.

Jifa tayi da mahaifin nata kanshi ya bugu da wani bokiti, azabar da yake ji a jikin shi sam lokacin bata ita yake ba, fatan shi shine kada ta yi nasarar ficewa daga gidan nan.

Tana kubcewa kururuwa ta hauyi tare da fatali da duk wani abu da taci karo dashi tana ƙokarin barin gidan.

Da sauri ya tarbeta bakin shi dauke da addu'a ya samu ya riƙeta, wahalar duniya kuwa ya shata ranar jikinshi duk ciwukan da LUBNA ta ji mashi ne.

Addu'a takobin mumine cikin ikon Allah ji yayi LUBNA tayi laƙwas a jikin shi ta sume.

Hawaye yaji sun kubce mashi lokacin da ya haɗa ido ds bangaren fuskar ts namiji dake aika mashi da mugun kallo, addu'a ya tofa mashi tare da rufe mata rabin fuskarta ya ɗauketa ya kaita ɗaki.

Gefen ta yake sai lokacin ya lura da ciwukan da LUBNA taji mashi da kuma jinin da ke fita a jikinshi, "Ubangiji ga LUBNA nan kai ne mafi sani akan abinda ka boye na tattare da ita, Allah ka zama gatan ta aduk inda ta tsinci kanta."

Baiyi bacci ba domin gata dai bacci take amma sai dai yaji ta kece da dariya tana ƙoƙarin tashi, addu'a yake babu ƙaƙƙautawa.

Hatta sallar asuba yau cikin gida yayita kasan cewar jikin shi babu kwari.

Makwaftan su yaji sun fara ihun, fitowar da zai yi yaga an baje gawar su Goga da kuma Ɗan Taure wuyan su a karye idanu sun firfito waje....

*MEEN@RT...✍🏻*
[7/19, 3:17 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE5️⃣_6️⃣*
...maganar da bokan ya faɗa mashi ce ta sanya wani gumi wanke mashi fuska babu shiri ya cire hular dake saman kamshi ya hau firfita da ita.
```

Kallon garsaƙeƙen ƙaton bokan dake gaban shi yayi, "Boka a taimaka, wallahi ko labari ban tabajin yarinya mai irin wannan halittar ba dan Allah a taimaka."

"Rufe mani baki!."
Bokan ya daka mashi tsawa da wata mummunar murya.

"In kasan da Allah miya kawoka wurin, radda duk ka ƙara ambatar Allah a gabana, kodai jinin ka aljanu su tsotse shi ko kuma daga ranar ba zaka sake gani da idanun ka ba har abada."

Tamkar zai ma Bokan sujada haka ya durƙusa jiki na kyarma ya furta.
"Tuba nike."

"Maganar samo yarinya mai wannan halittar kuma, kada ka kuskura zabe ya taho ba tare da ka samota ba, muddun ka bari akayi shiga satin zabe bamu gudanar da aikin mu ba to ba shakka kana cikin matsala, bace mani da gani kada in sake ganin ka har sai an samo ta."

Da gudu_gudu Alhaji Lamaru ya baro bukkar Bokan, kafin ya kai inda ya baro  security nashi sai da ya sha baƙar wahala.

Yana shiga Motar ya Umurci driver ya wuce dashi gidan Alhaji Sufyan.

Yayi sa'a domin kuwa ya tarar dashi gida bai fita ba, nan aka gaisa irin ta abokan da suka daɗe basu haɗu ba.

"Yadai! Duk na ganka a rikice, lafiya kuwa."?
Cewar Alhaji Sufyan.

"Zaɓe ya taho ya kuwa ba zaka ganni a rikice ba, kai fa kaji daɗin ka kayi  gwamnan garin nan ba tare da ka sha wahala ba ka gama yanzu kuma kana bisa kujerar ɗan majalisa, ka huta bokan ka ya iya aiki, ni yanzu daga wurin Jikan oduduwa nike, ya umurce ni da samo abinda ko a mafarki ban taba ganin shi ba kai a duniyar nan ma babu shi."

Murmushin takaici mahaifin AL'AMEEN yayi, domin ya lura har yau LAMARU bai yarda kuma ya dogara ga Allah ba.

"Har gobe ina ƙara yi maka tuni, tunda nike ban taba zuwa gaban boka ko kuma malami ba dumin biyan wata buƙata ina kai kuka na ne ga Allah shike share mani hawaye na a koda yaushe, ashe har yau baka bar wannan mummunar ɗabi'ar taka ba tabin bokaye."

"Ai biyu na raba kafa ina sa malamai suyi addu'a ga kuma ta ƙarƙashin ƙasa da nike bi, kasan abun biyu ake rabawa."

Murmushi kawai Alhaji Sufyan yayi, domin yasan Alhaji Lamaru yayi nisa bai jin kira.

AL'AMEEN da dawowar shi kenan gaida mahaifan nashi yayi tare da nufar cikin gidan, yana sa kafarshi cikin falon yaci karo da Fadila dake zaune ta ɗora ƙafa ɗaya bisa daya tana kallon wani series, kasan cewar Falon gidan guda ɗaya ne sai kabi ta cikin shi kafin ka isa zuwa ga ɗakunan ta gaban ta yabi domin karasawa ɗakin shi.

"Mtsw! Su Balamu anyi asarar kunnuwa, wani kam yayi faɗuwar bakar tasa."
Maganar da Fadila ta fada ce ta dakatar dashi tare da juyowa.

"Kee! Dawa kike."
Ya fada rai a ɓace domin bai shiga harkar kowa cikin gidan.

"Da wanda ya tsargu nike, wai shin ni tsarar kace da zaka zo bisa kai na kana mani wasu banzayen tambayoyin ka."
Fadila ta ƙarasa maganar cike da rashin kunya.

Duk da kasan cewar ta i ta ce babba hakan bai hana AL'AMEEN daga hannu ya tsinka mata mari.

A fusace ta mike tare da dafe kumci tana masifa.
"Uwar ka ka mara, ka mari Salima, Allah ya isa na kuma wallahi banga abinda zai hana ni haɗaka da yan sanda ba."

Zafin Zagin da tayi mashi ne bai san lokacin da ya cire Belt ya shiga zuba mata shi ta ko ina.

Ihun Fadila ne ke tashi cikin gidan tana neman taimako, a guje su Hajiya suka fado cikin falon, ganin irin bugun da AL'AMEEN ke yima yayar shi yasa Hajiya Mariya yin kukan kura ta tinkari AL'AMEEN, da kyar suka kwaci fadila da yayi ma lilis.

"Kin haifi Annoba gashi nan ya addabi kowa, to wallahi bai daki banza ma domin yau shima a cell zai kwana, wama ya sani ko shaye_shayen shi yaje yayi ya zo ya sauke haukanshi kan diya ta, to ba zata sa6uba."
Hajiya Mariya ta karasa maganar cike da masifa.

Fashewa da kuka Mahaifiyar AL'AMEEN tayi tare da fizgo kwalar rigar shi ta dauke shi da wasu tagwayen maruka.

"kaga abinda ka ja mana ko."?
Ta karasa maganar cikin kuka mai tsuma zuciya.

Har tsakiyar kwalwarshi yaji marukan da tayi mashi, a fusace yayi boll wani jug nan take ya tarwatse, da ƙarfi ya fizgi ƙofar falon ya fice tare da shigewa mota yabar gidan cike da zallar bacin rai...

---

...Ganin HIBBA da suka rabu gida uku suna tun karo ta yasa ta mikewa a guje tayi falo, tare da kulle ƙofar falon tana sauke ajiyar zuciya.

Dafa kafaɗar ta taji anyi da wasu dogayen yan yatsu, jiki na ciri ta juyo domin ganin wane sabon bala'in ne ta tarar.

Hibba ce tsaye ta wage baki tana kyalkyata dariya, "kin ɗauka zaki guje mana ne? To ni na tarbe mana falo yadda in kin gudo in tarbe ki, kai ku shigo gata na tare."
HIBBA ta fada da ƙarfi.

Bango sauran HIBBA suka ratsa sai gasu cikin falon sun hade da cikon ta huɗun, kyalkyacewa sukayi da dariyar a tare cikin wata irin ƙazamar murya.

"Ba zaki iya guje mana ba."
Suka fada a tare.

Nan fa suka fara kasuwa kashi_kashi suna cika falon tare da nuna ta da hannu suna kecewa da dariya.

Ganin wannan bala'i

Jiki na kyarma ta nuna ta da yatsa "HIB...BAH."
tare da sulalewa kasa.

6at ta bace komi ya koma yadda yake.

Hasken daya kashe mata ido ne yasa tayi saurin maida idon ta ta rufe, a hankali duban ta yakai ga drip ɗin da aka sanya mata, DADDYN Hibba ne gefen ta ya kafe ta da ido domin jiran ta yaje ta farka yaji mike tayar mata da hankali har jinin ta ya hau haka.

"Sannu."
Daddyn Hibba ya fada tare da kafeta da ido.

Kai kawai ta ɗaya domin magana ma batason yi.

"Mike faruwa dake, mikika nema kika rasa da har zaki sama kanki damuwa jinin ki ya hau har haka."?
Cewar DADDYN HIBBA.

"Alhaji bani son gidan nan a canza mana wani dan Allah."
Ta fara murya na kyarma.

"Shine damuwarki kuma baki sanar dani ba, har kika bari jinin ki ya hau haka, ku fara shiri friday zamu koma sabon gida."
Ya karasa maganar tare da ficewa daga ɗakin.

Binshi tayi da kallo zuciyar ta na kuna, ba tada wata hanya da zata rage mata abinda take ji sai wannan domin a tunanin ta i ta ce mafita in sun koma wani gida kila aljanun jikin HIBBA su fita.

Bacci ta samu tayi har zuwa yammaci, wata shawara ta zo mata, wayar ta ta ɗauka tare da

kiran  Babbar aminiyar ta wato turai.

Ba'a dauki dogon lokaci ba sai ga Hajiya turai ta bayyana a gidan domin jin abinda yasa take mata kiran gaggawa.

"Yanzu ke da wannan abubuwan ke faruwa dake amma baki tashi neman magani ba kina nan zaune, in tambayeki Baba yasan da wannan maganar."?

"Bani so in tayarma da mahaifina hankali kinsan tun bayan rasuwar Hajiya har yau jikin shi babu daɗi."

"To a yanzu ba sai an jima ba ki shirya akwai wurin Malamin da zan kai ki."

"Turai yanzi fa magrib ta kusa."

"Ke dalla can wace magriba, kina tashi muje a kawar maki da matsalar ki ko kuma zaki zauna ne ki mutu a banza."?

Ko Alhaji bai sani ba ta kama hanya suka nufi gidan boka, domin dama shi rayuwar gogaggun yan boko yake tana da izinin zuwa duk inda take so ba tare da ta nemi izini a gareshi ba.

Wajen garine anyi nesa da mutane sosai suka shige cikin Bukkar.

Hajiya Turai ce ta budi baki da niyyar korama boka bayani.

"Kada ki wahakar da kanki, tun kafin kuzo an sanar dani komi, ɗiyarki na bincika tauraronta amma banga komi ba in takaice maki magana babu tauraron ta a jinsin mutune kuma banga ta a jinsin jinnu ba, tabbas a kwai wani boyayyan al'amari  dake tattare da ɗiyar ki, ku amshi wannan maganin a tabbatar an turara shi a yau, kada kuyi kuskuren barin ta taga wannan maganin,hhh in kuka bari ta ganshi kashin ku ya bushe."
Ya karasa maganar tare da jefa ma Hajiya MURJA.

Kuɗi suka zazzage a gabanshi tare dayin godiya suka dauki hanyar gida.

"Jikina yayi sanyi, wallahi tsoro nike ji."
Hajiya Murja ta fada da karyayyar murya.

"Ke fa a kwai ki da saurin karaya, miye na wani jin tsoro, muje ayi komi a gabana dan na lurabin nabarki tabbas sai kinyi kuskure."

Basu isa gidan ba sai gaf da Magriba duhu yayi, ba batun Sallah turaren suka ɗauko aka mai da shi cikin jikkar Turai.

Sai da suka tabbar Sun kulle ɗakin HIBBA kafin su dawo falo su ɗauko garwashin.

"Kai! Murja ke kika ɗauki maganin nan? Yanzu fa muka barshi a cikin jikkata mukaje mu ɗauko garwashi."
Turai ta ƙarasa maganar tare da kafe Murja da ido.

"Tare fa muka fita dake."

"Ga abinda kuke nema na kawo maku."
Hibba dake ratsowa ta cikin bango ta fada hannunta riƙe da maganin.

Tsabar firgita da suka yi wani guntun fitsari ne ya kubce ma Turai....

---

...Sanyin asuba da Kuma sassanyan ruwan da aka sheka mata ne ya sa ta mikewa a firgice tare da kiran sunan mahaifin nata.

"Ishasshiya basarakiya kin hakimce kina bacci, maza ki tashi ki ɗebo ruwa, ko wani kike tunanin zai ɗebo maki."
Gaje ta fada cike da masifa dake cinta.

Duk da jikin ta babu kwari, haka ta ɗauki ƙaton bokitin tayi waje, a guje ta dawo gidan tana haki, tuna abinda ya faru jiya dasu Goga.

Babane ya shigo gidan  ganin LUBNA yayi tsugune tana haki.

Ganin jikin mahaifin nata da raunuka ya tabbatar mata cewa jiya ciwon ta ya tashi.

Cikin kuka ta ƙarasa gaban mahaifin nata .

"Baba ka yafe mani nasan ni naji maka waɗannan ciwukan, mi ya sa ka tsaya a lokacin da hankalina ya gushe."

Zaunar da ita yayi domin yasan jikinta babu kwari, "ki kwantar da hankalinki, miya fiddaki waje bayan jikin ki babu kwari."

"Ruwa zani ɗeboma Mama."

"Ruwa!"
 ya maimata kalmar cike da zallar mamaki."

"Gaje! Gaje!!."

"Wai lafiya da sanyin safiyar nan kake kwala mani irin wannan kiran."
Gaje ta fada tare da tsayuwa bisa kanshi ƙerere.

"Yanzu tsabar baki da imani yarinyar nan bata lafiya amma kika aiketa ɗibar ruwa, ita Kulu aikin mi take a cikin gidan nan da bazaki aike ta taɗebo ba."?

"Kaga Malam ina fa ganin girman ka, ah to kada fa ta kaimu ga haka nida kai a cikin gidan nan, ita Lubna ba i ta bace babbab akan mi zani tayar da Kulu tana bacci alhali ga Lubna."

"Baza ni gajiya da fada maki kiji tsoron Allah ki haifi ɗiya amma ki rika nuna mata tsana, ko mi kika yi Gaje keda Allah."

"Yo dama ai dole ka fadi haka tunda ka ɗaure mata gindi a cikin gidan nan."
Ta karasa maganar tare da turo kallabi gaba.

"Baba!."
Lubna ta kira sunan.

"Baba Su Goje fa."?
Ta jefa mashi tambayar.

Cike da mamaki yake kallon ta "Miyasa kike tambayar su Goje, yanzu haka ana can ana shirya jana'izar su."

Wata zabura tayi tare dayin baya, "kada kace mani suma sun mutu, Innalillahi wa'inna ilahirraji'un."

"LUBNA ki kasan ce mai daukar kaddara a koda yaushe ke kuma taki kaddarar kenan, ki maida lamuranki ga Allah komi lokaci ne wata rana haƙurin da kikayi zai zama riba a gare ki."

Hawayen dake fuskarta ta share.
"Baba nagode insha Allah zanyi amfani da abinda ka fada mani."

"Allah yayi maki albarka."
Da Amin ta amsa tare da shigewa ɗaki ta faɗa bisa katifa ta cigaba da kuka mai ban tausayi.

Mirrow ɗin ɗakin ta nufa tare da yaye gyalen da ta rufe fuskar ta dashi, nan fuskarta ta bayyana, fashewa tayi da kuka tare da shafar fuskar ta.

Abinda zai baka mamaki bangaren fuskar macen shine ke kuka sa6anin bangaren fuskar namiji daya kasan ce dariya yake.

Ihun Gaje taji yi tana neman temako take tamkar zata tarwatsa dodan kunnen mutum, a guje Lubna ta zari mayafin ta tayo waje jin ihun da mahaifiyar tata keyi.

binda taga ya faru da Gaje ne yasa ta jin wani jiri namen kayar da ita, anya kuwa abinda idonta ya hasko mata gaskiya ne...

*MEEN@RT...✍🏻*
[7/22, 6:19 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine
```

ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE7️⃣8️⃣*
...Gudu yake tsalawa saman titin tankar zai tashi sama, ganin tuƙin gagancin da yake yasa mashina da motoci bashi hanya da sun ga ya nuho inda suke tare dayi mashi addu'ar shiriya.

Tsarewar Ubangiji ce kaɗai ta isar dashi gidan Bilal lafiya, ko ƙarasa kashe motar biyi ba ya fito tare da afkawa gidan.

Kamar yadda ya zata kuwa hakane, yana shiga ya iske bilal zaune a falo shida budurwar shi, kota kansu bai bi ba a fusace ya haye sama.

Cike da mamaki suka bishi da kallo, "Jira kiga in bishi nasan yau halin ya motsa, mutumin nawa akwai matsala."
Cewar Bilal tare da miƙewa zai haye sama.

Bata fuska tayi tare da cuno baki.
"Ɗan wahala kawai, kai yanzu daga shigowar shi har ka wani mike kaji lafiyar shi, nifa wannan guy ɗin bai wani burgeni hasalima nafishi ranshin darajar da yake ji da ita."
Cewar Amna

"Kee! Wallahi ki shiga hankalin ki wancan guy ɗin ya fiki iya bariki, kwaro ne da kike ganin shi."
Ya ƙarasa maganar tare da hayewa sama.

Saman gadon ya ganshi zaune yana sauke ajiyar zuciya, "ayya mutumi na ran maza ya baci, lafiyar ka kuwa naga ka shigo kana shirin yin ball damu."
Cewar BILAL.

"Kai na ya ɗauki zafi, bani son dogon surutu, ina LEEMCY  take."?
AL'AMEEN ya fada a taƙaice.

"Nikam ina zani san inda LEEMCY take, ka kirata mana kaji."

Turo ƙofar da akayi ne ya dakatar dasu daga maganar da yake, LEEMCY ce ta shigo cikim muguwar shiga irin ta gogaggun yan duniya, domin tun bayan shigowar Al'ameen Amna ta sanar da LEEMCY.

Ganin shigowar tane yasa BILAL ficewa daga dakin.

"Honey! Mike damunka miya bata maka rai."?
Cewar LEEMCY.

"ki bari kawai gida kowa bai sona babu mai kaunata, yanzu haka na baro masu gidan su bazani koma ba har sai sun nemeni."

Wani irin daɗi ne ya lullube zuciyar LEEMCY, domin koba komi ta samu damar da zata cika burin ta.

WACE CE LEEMCY?
Ɗiya ƙwalli ɗaya ga Alhaji Marwan da kuma Hajiya Nusaiba, Alhaji Marwan mutum ne mai matuƙar kuɗi babban ɗan kasuwa wanda duniya tasan da zaman shi domin har kasar waje yana da hannun jari.

Tun tasowar Ɗiya ɗaya a garesu wato Halimatu wadda ake kira leemcy yarinya ce mara ɗa'a gatan da suke nuna mata shine yayi sanadin ta ida lalacewa, zata iya fita tayi kwanaki bata dawo ba kuma babu wanda ya isa ya tanka mata domin ta samu daurin gindi ga mahaifin ta, hatta karatun ta a kasar waje tayi shi haɗuwar su da AL'AMEEN ce tasa a ka maidota ƙasar ta taci gaba da karatu, tun bayan haɗuwar su LEEMCY babu yadda batayi ba ganin taja ra'ayin AL'AMEEN  sun aika zina amma bata samu dama ba, domin kuwa duk iskancin AL'AMEEN gyamar Zina yake yi, wannan yasa yau ta ɗana tarkon ta ganin AL'AMEEN ya baro gidan su.

"Honey!.?"
Leemcy ta faɗa.

"Na'am Baby na."

"Yaushe zamuyi aure."?

Jin tambayar yayi wani banbara kwai, shifa duk lalacewar shi yaba taba fatan ya auri LEEMCY, yafi so inya tashi aure ya samo wata natstsiyar ya aura.

"Kayi shuri."
Leemcy ta jefa mashi tambayar.

"Shi aure yana buƙatar natsuwa kibari mu dai_daita da mahaifana sai mu yi auren mu hankali kwance."

Kallon shi tayi tare da saƙa wani abu a zuciyar ta.
"Karya kake AL'AMEEN, sai ka aure ni koda baka so, duk duniya babu namijn da nike so sama dakai, dole ne in koma gidan boka a sake sabon shirina kan ka."

"Mi kike tunani haka."
Al'ameen ya katse mata zancen zucin da take.

"Babu komi rayuwar auren mu nike haskowa wadda zamu gudanar."

"Sakara! Baki da hankali, ni zani auri yar bariki.a matsayin matar aure na, ai sai dai kiji ana ɗaura mani aure da wata."
Ya ƙarasa maganar cikin zuciyar shi.

"Duk ka gama guje_gujen ka lokaci na baka, domin Boka ya shaida mani sai ka aureni, indai nice zaka zo hannu."
Ta karasa maganar cikin zuciyar ta.

Tun bayan barin AL'AMEE Haj Salima ke kuka sakamakon cin mutumchi da ta sha wurin MARIYA.

"Salima!"
Alhaji ya ambaci sunan shi.

Ɗago kanta tayi da idanunta da sukayi jajur tsabar kukan da tasha.

"Ko wane bawa da kike gani da tashi ƙaddarar, ki daina zubda ma AL'AMEEN hawaye domin hakan babban tashin hankali ne a gareshi, kiyi hakuri mu dage da addu'ar wannan ita ce ƙaddadarar mu, addu'a ita ta kamace mu ba kuka ba."

Fadila kuwa tun bayan ficewar Al'ameen baƙin ciki ne cunkushe a zuciyar ta domin taso ta haɗashi da jami'an tsaro amma sai ga mahaifin su ya shigo, dogom tsoki taja tare da ɗaukar key ɗin motar ta tabar gidan.

Ɗakin Wizee ta nufa domin yau tayi alƙawarin bazata kwana gida ba inta huce zata dawo...

---

...Dakin ne ya fara girgiza ga kuma dariyar HIBBA dake tashi cikin amo mara ɗaɗin sauti tamkar kukan jaki gamida kukan jarirai ya hade wuri daya ya bada wani rikitaccen sauti.

"Ba yanzu ya kamata ki fara fitsari ba, ki bari ki amshi sakamakon ki."

"Wato ku yan ɗaɗi zuwa wurin boka ko, hada kulle ni a ɗaki, cikin ku wace ce ta kulleni a ɗaki."?

Caraf Hajiya Turai ta nuna  Hajiya Murja.
"Kin ganta nan i ta ce wadda tace a kulle ki."

Cike da mamaki haj Murja ke kallon Turai ganin zata jaza mata wani bala'in.

"Turai! Waya kawo shawarar a kulleta inba ke ba."

"Ƙarya kike mani, ke nifa Murja kin cuce ni kin jaza mani bala'i miyasa baki shaida mani gidan ki a kwai aljanu har haka ba, Allah ya isa tsakani na dake wayyo Allah aljana da girman uwarki da Ubanki ki gafarce ni.

Falau! Taji an Gwabre mata baki da wani basamuden hannu.
"Niki ke zagi Uwata da Ubana kike zaga, ni sheɗaniya kike zaga, hhh yau zaki gane kurenki.

"Na tuba sheɗaniya ki gafarce ni a buɗe mani gida in Fita wallahi ko hanyar gidan nan bazani sake kallo ba."

Tuntsirewa HIBBA tayi da dariya tare da fara shawagi a sama domin har yanzu bata sauko ƙasa ba.

"Yau zaki ga ƙarshen sheɗanci sai kin gane kinyi kuskuren shiga faɗan dan da babu ruwanki." Ta gama faɗar haka ta nuna TURAI da hannu sai ga wani iska ya kwasheta sunyi sama, duk ƙiba irin ta Turai haka iskan nan yayi sama da ita ya ɗaure kafar ta jikin fanka.

Ihu kawai take kurmawa tare da tsinema Boka da Kuma Haj Murja, fankace ta kunna kanta tare da kece wa wani irin gudu tare da Turai dake jikin ta maƙale.

Hajiya Murja kuwa ganin abinda ya faru da Turai jikin ta babu inda bai kyarma.

Tamkar giftawar ido haka HIBBA ta dira gaban Haj Murja.
"Mai gayya mai aiki nadawo kanki, kina tunanin boka zai iya raba wannan faɗan dake tsakanin mu, gabar dake tsakanina dake ta fara ne tun kafin zuwabna duniya, kin rabani da farin cikina rayuwata wanda ya kasance shine rayuwa ta domin cikar burin kun, ta karasa maganar hawayen jini nabin fuskarta."

"HIBBA! kin san kuwa abinda bakin ki ke furtawa, minayi maki dawa na rabaki a rayuwar nan." Rufe bakinta keda wuya Hibba ta Nunata da hannu take wasu hannaye suka shiga ɗauke Haj murja da lafiyayyun maruka.

An ɗauki sa'o'i sun kai biyar kafin a daka ta
"Kamar yadda na rabu da farin ciki kema har abada a haka zamu tabbata dake daga ƙarshe kuma in kashe ki."

Murja bata san mike faruwa ba domin marukan da tasha sun rikita mata kwalwa ta koma ganin mutane bibbiyu.

Hannu HIBBA ta ɗora a goshin murja lokaci ɗaya wani farin abu ya shiga jikin murja tamkar wadda aka jona ma shokin ɗin nepa haka Murja ta riƙa kyarma idanun ta suka kafe ta dena motsi.

Turai dake saman fanka ma jeho ta akayi ƙasa tim, komi ya juye mata sakamakon gudun da fanka ta riƙayi da ita, dan haka zafin faɗowar da tayi ne yada ta shiga kurma ihu tana neman temako.

"Zaki rufe mana wannan rubabben bakin naki ko sai mun farke shi."

Ba shiri Turai tasa hannu biyu ta toshe bakin ta gudun kada kukan da take  ya fifo, ganin Murja kwance ƙasa shirim! Ba karamin tayar da hankalin Turai yayi ba da sauri ta kara toshe bakin ta ganin kukan na neman sake kubce mata.

HIBBA kuwa wasu ƙananun yara masu suffar tane suka bayyana, kawunan su kuwa sun linka girman jikin su sau biyu.

A tare suka tuntsire da dariyar da ta sanya ɗakin amsa kuwwa.

"In an yanka nike son kai."

"Ni kuma tumbinta nike so."

"Kafafun za'a bani."

"Ni kuma kan nike so."

Jin abinda halittun gaban Hibba ke fada yasa Turai fashewa da kuka tana kiran sunan mai gadi.

"Na tuba kuyi man rai ku barni da rayuwa ta, nida gidan nan ko kuma shiga sabgar Murja har abada, kada ku cinye ni wayyo ni Turai yau naɗebo ruwan dafa kaina."

"Kina so kibar gidan nan lami lafiya."?
Cewar HIBBA.

"eh."
Ceqar turai tare da yayumar gyale ta miƙe tsaye.

"Indai kina son barin gidan nan sai kinyi mana rawa irin wadda aljanu keyi."

"Nashiga ukku ko kiɗan aljanu ban taba jiba bare kuma rawar su dan girman iyayenki kiyi mani rai bani iya rawa bakiga yadda nike ba a dunƙule kamar giwa."

Mari aka ɗauke ta dashi sai gata ƙasa warwas.

Kafin rai na ya baci ki miƙe ki fara taka mana rawar aljannu.

Lokaci ɗaya ɗakin ya ƙaure da wata rikitacciyar waƙa maradaɗi sautin ta kaɗai  ya isa ya sumar da mutum.

"Ruum_ruum dumdumarun, shuuuw,ƙuuuw duuuw, rumdumdum ruuuw, ƙuuuuwduuuw."
Amon waƙar ya cika dakin

Miƙewa tayi ta fara taka rawa in tayi gabas sai tumbinta yayi yamma haka take rawa tana gantsarewa ga tayi nan da gudu sai ta dawo ta daka tsalle sai uban tumbinta yayi wata girgiza kafin su dawo ƙasa.

Ganin yadda ta dage tana ɗirkar rawa yasa Aljanun kecewa da dariya suna fakar idon ta su tofa mata wani abu data taka zata sulɓe ta faɗi haka zata taƙarƙare ta mike taci gaba da ɗirkar rawa.

Ganin irin galabaitar da tayi ne yasa HIBBA daka mata tsawa, "ki dakata, basai na gaya maki komi ba domin kuwa jikin ya gaya maki, in na ƙara ganin ƙafarki cikin gidan nan gawarki ce za'a fitar, kada ki kuskura ki faɗama wani abinda ya faru in naji maganar nan wurin wani kashinki ya bushe, ta ƙarasa magana tare da daka mata tsawa.

"Wallahi naji natuba hanyar gidan nan ma bazani ce nasani ba."

Ƙofar falon ce ta buɗe kanta "tashi ki bar gidan nan kafin mu mufiddaki Ɗan ƙarami kuyi mata rakiya."

Jin wannan rakiya da za'ayi mata yasa ta zabga da gudu ko gyale ma a hannu yake, tun daga nesa take kwalama mai gadi kira.

A rikice ya fito da adda domin kiran da take mashi yasan bana lafiya bane.
"Hajiya lafiya, ina zaki babu tufafi."

"Uwarka Nike Ɗan iya, tsirara ka ganni ko nan ubanka ne jikina,Talaka mai muguwar tambaya ƙurilla shin kana bude mani gida ko sai nabi ta kanka na wuce, Gantalalle baka ganni ba a gantale a wannan dare har ka tambayi lafiya, bude mani nace, in yaƙi buduwa ka bani tsani yau kota katanga ne sai na dira nabar wannan baƙin gida."
Ta karasa maganar tare da juyawa taga ko masu yi mata rakiya sun ƙaraso.

A rikece jin wannan zagi daya sha ya buɗe get ɗin, ƙafar da zata sa waje sai ji tayi ance "bata fitaba kuyi mata rakiya."
Sakin gyalen tayi tare da barin wurin a million...

---

... Wasu hirɗa_hirɗan ƙadangaru ta hango guda biyu sun shaƙe Gaje ta hanyar yi zagaye wuyan ta kamar tasa sarƙa.

Ganin wannan al'amari yasa Kulu rugawa a guje ta faɗa ɗaki ta rufe tare da barin mahaifiyar ta tana mai kurma ihu.

A guje Lubna tayo kanta zata kamata, saurin riƙeta Mahaifinta yayi tare da girgiza mata kai.

Mutane kam kamar jira suke sai ga gida ya cika da yan kallo suna ta tofa albarkacin bakin su.

Duk yadda kayi ƙoƙarin raba Gaje da jankwatakayen nan abu yaci tura kana matso inda take zaka ga sun buɗe baki tare da sakin wuyan ta kai kuma sunyo kanka ba shiri gida ya fara darewa kowa ya fara ficewa cike da tsoron wannan al'amari.

Wasa_wasa Gaje sai suma take tana farfaɗowa har yamma abu ɗaya ake duk wani mai kama ƙadangaro an nemo amma abu ya gagara.

Ganin Gaje ta fita hayyacin ta yasa Lubna fara kuka tare da rokon mahaifinta ya barta taje ga mahaifiyar ta amma furr ya hana.

Abu har dare ana abu ɗaya ƙadangaru sunƙi barin jikin Gaje, baci ba sha Kwana ɗaya amma duk ta fita hayyacin ta.

Da kyar malam ya bar Lubna ta nufi Mahaifiyar ta, babu tsoro tare da nufi kama ƙadangarun, abun mamaki kafin hannunta ya isa jikin Gaje sai ga kadangaru sun saki wuyanta a guje sun haye bango.

Maida numfashi Gaje tahauyi a galabaice, domin ta azabtu, ganin an raba Gaje da ƙadangarun yasa Kulu ƙoƙarin matsowa inda Gaje take.

Mutanen da abun ya faru gaban idon su sai suka kara tabbatar wa lallai Lubna ba mutum bace.

Shigowar Saratu tayi dai_dai da tashin Lubna aguje suka rungume juna.

Wace ce Saratu
Saratu diya ce ga Malam zailani makwaftan su Lubna, tun tashin su Saratu ke tare da Lubna duk da ƙoƙarin rabasu da akayi amma abun yaci tuna, Saratu mace ce da bata ɗaukar Reni ko alama domin tane ma mutanen garin ke rangwantama Lubna saboda bala'i da masifa in kana son su to ka taba kawar ta tabbas zakaga yadda ake ruwan bala'i domin Saro masifa kamar yadda suke kiranta bata ɗaukar reni ko alama bata shiga sabgar kowa amma inka shiga tata akwai matsala, bayan gama karatun su Saro gidan kakarta taje hutu shine dalilin rabuwar su da Lubna.

Hanun ƙawar tata taja suka shige ɗaki.
"Dawowa ta kenan kaya na kaɗai na aje nace sai nazo na ganki, sai na iske gidan ku cike da mutane lafiya kuwa."?
Cewar Saratu

Nan Lubna ta kwashe kaf abinda ya faru ta faɗama Saratu

"Hmm duk da mahaifiyar kice amma banso kika cire mata kadangarun nan ba naso ki barta  ta koyi darasin rayuwa."

Bata rai Lubna tayi, "kin san fa banison haka mahaifiyata ce fa."

"To naji mubar maganar."

Ko sallama babu haka Kulu ta faɗo ɗakin tana mai jan dogon Tsoki.
"Babu dai zuciya an yar kare ya ɗauka."

Murmushi Saro tayi domin yau bata da lokacin Kulu ta barta ne zuwa gobe

Bata bar gidan ba sai da aka fara kiran magriba.

Gaje kuwa takai sati tana jinyar wuyan ta daya sha shaƙa, tana karasa warkewa suka ɗora daga inda ta tsaya.

Sallama akayi da Malam da haka yana fita Gaje ta lallaba tabi bayan shi domin tabbatar da abinda take zargi.

Babu jimawa tadawo cikin gidan tamkar kubububuwa ranta a jagule jira kawai take ya shigo.

"Lubna! Lubna!!."
Malam ya shiga kwala mata kira.

Ita da Kulu a tare suka fito
"Ki fara shirye_shirye na sanya gonata a kasuwa da zarar na sayar zani biya maki kuɗi kici gaba da karatu."

"A hayye nanaye, yau ake yinta gobe sai labari, yanzu dama abinda kunnena ya jiyo mani ba gizo bane da gaske gona ka sayar zaka biyama wannan Annobar kuɗin makaranta, wallahi ka bani mamaki, indai ina raye wallahi kota fara karatun nan saita barshi, in sha Allahu ka sanyata makarantar nan sai ta dawo maka daɗiya ko ɗa, kai nifa da ace asibiti na haihu babu abinda zai hana ince musayar diya akayi mani, natsani lubna mai kaunar tama bani ƙaunarshi indai karatu ne ta fara kagani zakasha mamaki."

Wani nauyi zuciyar shi tayi da ƙyar ya ɗaga hannu tare da nuna gaje idanunshi sunyi jajur tamkar gauta, amma abinda ya tokare mashi zuciya ne ya sashi dafe ƙirjinshi da sauri, wani tari ne ya turniƙeshi lokaci daya jini ya fara ambaliya ta hanci da bakinshi sai gani suka yi ya sulae ƙasa.

A guje LUBNA ta fasa wata ƙara tare da rufowa da gudu kafin ta iso harya kai ƙasa...

*MASOYAN ASALI INA MATUKAR GODIYA DA NUNA KULAWARKU GARENI😍 NAGA KIRANKI DA SAƘON NINKU NAJINA SHURU DA KUKAYI INA MATUKAR GODIYA ALLAH YABARMU DAKE YABAR ZUMINCHI* 😍😍😍

*MEEN@RT...✍🏻*
08133562798
[7/23, 9:04 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE9️⃣__🔟*
... Kamar yadda yayi niyya hakan ce ta kasan ce domin kuwa sai da ya kwashe mako guda a waje ba tare da ya nemi mahaifanshi ba, su Haj Salma kuwa hankalinta yayi ƙololuwar tashi sakamakon rashin ganin tilon ɗan nasu.

Alhaji ne mai kwantar mata da hankali ta hanyar shaida mata duk inda yake zai dawo, shike sawa hankalinta na ɗan kwanciya, kullum cikin kai kukan ta wurin Allah take.

Tamkar wanda ƙwai ya fashe mawa a cikin lakka haka ya ƙaraso cikin falon inda Mahaifanshi ke zaune, ratsasu yaso yayi ya wuce sai dai kiran sunan shi da suka yi ne ya sashi dawowa da baya.

"Barkan ku da safiya."
AL'AMEEN ya futa kanshi a ƙasa.
```

Cike da zallar mamaki suka amsa domin rabon da ya gaishesu an ɗauki lokaci mai tsayi.

"AL'AMEEN daga ina kake?, yanzu kayi mana adalci kenan katafi kabar gida har tsawon mako daya baka dawo ba, ka kuwa san irin cikin halin da ka sanya mu."?
Hajiya Salima ta kara maganar cikin bacin rai."

"Kuyi haƙuri."
AL'AMEEN  ya furta ba tare daya hada ido dasu ba

Mamakin dake fuskokin su a bayyane yake, yau AL'AMEEN ne ke basu haku, "Alhamdulillah Allah maji roƙon bawa."

"Alhamdulillah mu fatan mu a kowane lokaci bai wuce Ubangiji ya shirya mana kai ba ka dawo tamkar sauran mutane, magana ta gaba da nike so dakai i ta ce kafiddo matar aure cikin ƙanƙanin lokaci nike so ayi bikin ka, shin kanada wata wadda kake so."?
Alhaji Sufyan ya jefama AL'AMEEN tambayar.

"Eh Daddy."
Ya bada amsa

"To wace ce? Waye mahaifinta? Kuma a ina take da zama."?

"Ɗiyar Alhaji Marwan ce ɗan kasuwar nan dayayi fice."
AL'AMEEN yaji bakin shi ya furta ba tare daya bashi izini ba, kwata_kwata ya rasa mi yasa ana fara mashi waɗan nan tambayoyi sai dai yaji kawai bakin shi ya hau bada amsa bayan shi kwata_kwata bai fatar LEEMCY ta zama matar shi.

"Alhamdulillah tunda ka samu mata har kun dai_dai ta tomu bamu da matsala, ni zami samu Marwa zaboda muna da kyakkyawar alaƙa dashi."

Babu yadda hajiya Salima ta iya sai haƙuri domin tasan wace ce Leemcy amma tana fata wannan auren ya zama sanadin shiriyar su, su duka biyun.

Alhaji Sufyan duban shi ya mai da gasu Hajiya Mariya tare da kiran sunan fadila.

"Kema ki fito da mijin aure domin ina sane da duk wasu abubuwa da kike aikatawa kece fita ki kwana waje yawo babu inda baki zuwa to duk ina sane da ƙaryar da mahaifiyar ki keyi in na tambaya a lokutan da baki nan domin ita ke goya maki baya duk abinda kike, cikin samarinki ki fiddo wanda kike so za'a haɗa auren ku dana AL'AMEEN."

"Wallahi wannan sharri ne ake mata, kawai dan mutum yaga ɗan shi lalatacce ne sai ya ɗauka ɗan kowa ma haka yake, to Fadila ba haka take ba Alhaji wannan sharri ne ake mata irin na maƙiya."
Hajiya Murja ta ƙarasa maganar cikin zafi

Murmushin takaici Alhaji Sufyan yayi "domin yasan wannan duk aikin haj Mariya ne, ita ce sana din lalacewar Fadila.

Kamar yadda Alhaji Sufyan ya fada haka kuwa akayi cikin makon aka sanya bikin AL'AMEN da LEEMCY wata ɗaya.

LEEMCY kuwa Ganin yadda aikin bokan ta yaci ƙara tashi tayi tsaye tayi domin tayi alƙawarin raba AL'AMEEN da duk wanda taga suna da kusanci....

---

...Alhaji Lamaru kuwa hankalinshi duk a tashe yake ganin ga zabe ya taho amma babu wannan halitta da aka sashi nemowa duk yadda ya baza mutane a gari amma shuru har yanzu babu labari.

Zulfa'u kuwa sam hankalinta ba kwace yake ba tun bayan mutuwar ɗansu mai kimanin shekaru biyu, da aka wayi gari aka iske gawarshi.

Sam Alhaji Lamaru hankalin shi bai tashi ba da mutuwar ɗan nasu domin shine ya bayar da shi akayi mashi aiki domin samun duniya shiyasa sam hankalin shi bai wani tashi ba.

Alkawari ya dauka indai yana raye sai ya samo wannan halittar a duk inda take koda kuwa zai rasa ranshi...

---

...Sanyin Ruwan da ya sauka jikin tane ya sa ta tashi a matuƙar firgice tare da fara waige_waige

"Lafiyar ki kuwa, ace bacci tun dawowa ta kike yi amma har yanzu baki farka ba."
ABBAN HIBBA ya ƙarasa maganar cike da zallar mamaki.

Waige_waige ta hau yi cike da mamaki domin ganin ta tayi kwance bisa gadon ta, " To mi haka ke nufi, ita da ke falo kwance a sume tun bayan azabar da HIBBA ta gana masu."

"Wai mike damunki kina ji ina maki magana amma kinyi shuru."
ABBAN HIBBA ya katse mata tunanin da take.

"Bakomai zazzabi ne ke damuna amma naji sauki."

"Ok Allah ya karo sauƙi, kada dai ku manta gobe friday tun wuri za'a zo a kwashe ku mUkoma sabon gida.

Bala'inda take ciki harya mantar da ita tashin da zasuyi, dan haka cikin daren ta haɗa duk wani abu da take buƙata, cike da tsoron abinda HIBBA ta aikata mata domin har yanzu jin jikin ta take tamkar ba nata ba.

Unguwar da suka koma yanzu ita ake kira ihunka banza domin kuwa irin unguwannin nan ne na nesa da gari.

Iya ƙeruwa gidan ya ƙeru domin an ƙawata shi da kayan alatu na more rayuwar duniya.

Abinda suka san suna matuƙar bukata na daga abin amfani dasu kaɗai suka taho amma komi ABBA HIBBA ya zuba a Sabon gida.

Sai yanzu Hajiya Murja ta tuna da ƙawar ta wato hajiya Turai, waya ta ɗauka tare da kiranta domin jin lafiyar ta, sai da tayi mata 3 miss call a na hudun ne ta dauka.

"Kai jama'a! Wannan bala'i dami yayi kama, kin kirani ne keda aljanar ɗiyarki ku ƙarasa kashe ni, to nida ke har abada mun rabu ke hanyar da gidan ki ma yabi nida ita har abada babu ni babu ke, number kima yanzu zanyi blocking ɗinta, ina zaman zamana kika jawo mani bala'i sai gani da taka rawar Aljanu sune dayi mani rakiya har gida, babu ni babu ke har abada."

Kafin Haj Murja tayi yunƙurin furta wani abu ji kake ƙit! Haj Turai ta tsinke wayar.

"Yanzu shikenan ni ɗaya ta zaki jazama bala'i ki barni dashi, ni Murja nashiga Ukku na lalace yau nakai kai na ga halaka saboda son abun duniya."

Hibba kuwa tun bayan dawowar su gidan baka taba gani ta fito da rana sai dai in dare yayi kaji fitowar ta.

Ganin tun bayan dawowar su gidan babu wani mugun abu daya faru yasa Hajiya Murja sakin jiki tare da zallar murnar wannan al'amari.

Tun safe ABBAN HIBBA ya bar gidan dumin wata harkar kasuwanci da ta taso masu, dan haka yau gidan daga HIBBA sai Mahaifiyar ta.

Abinci ma mai aiki ce ta dafa shi ta kaima kowa ɗakin shi dan haka duk yau idon HIBBA bai haɗu dana Hajiya Murja ba.

Kasancewar Alhaji bai nan yau tun wuri Hajiya ta shige ɗaki ta kulle kanta.

Dare ya raba bakajin motsin komi sai kukan karunuka da kuma mujiya, A hankali ƙofar ɗakin Haj Murja ta fara buɗe kanta wani baƙin hayaƙi na shigewa ɗakin.

Labulayen ɗakin ne suka fara tashi sama sakamakon wata iska mai tafiya a hankali data fara kaɗawa, wutar dakin dake kashe ce ta fara kunna kanta tana fafarniya ta ɗauke ta dawo, a hankali baƙin hayaƙin nan ya fara haɗewa wuri ɗaya tare da koma wa wani dogon hannu mai farata zaƙo_zaƙo ya tafi luuuw! Ga Haj Murja dake bacci bata san mike faruwa ba...

---

...Da sauri likitan ya fito yana yarfe zufa, duban su yayi tare da furta.

"Ku same ni office."
Tare dayin gaba abinshi cikin sauri

Gaje ya mutsa fuska tayi cike dajin haushin likitan, ita so tayi ya fito yace SULE ya rigamu gidan gaskiya.

Baya shigar su office ɗin likitan zaune suka iske shi yana dakon su.

"Kamar yadda na shaida maku halin damuwa da baƙin ciki shine musabbabin wannan almari da ya tsintsi kanshi, zuciyar shi ta fara kumbura i ta ce sanadin aman jinin daya fara, a tunaninmu za"ayi ma shi aiki amma Alhamdulillah mun fara shawo kan matsalar tunda ciwon baiyi nisa a jikin shi ba kuka kawo shi, zamu riƙe shi a hannun mu amma gaskiya zan jima muna kula da lafiyar shi amma yanzu haka muna bukatar dubu ɗari domin taimakon da zamu rika bashi shine zai hana ayi mashi aiki."

"Shikenan ka gama likita."?
Gaje ta faɗa tana yatsina fuska.

"Eh wannan sune adadin kuɗin da muke buƙata."

Mikewa tayi tare da furta.
"Sai ka jimu."
Tayi gaba abinta.

"Likita dan Allah mahaifina zai rayu kuwa."?
Lubna ta tambaya hawaye nabin rabin fuskarta.

"Allah shine mafi sanin gaibu, ku dage da addu'a sannan kuyi ƙoƙari samo kuɗin nan da wuri muke bukatar su."

"Insha Allah zamu kawo."
Lubna ta ƙarasa maganar tare da bin bayan mahaifiyar ta da sauri.

"Mama dan Allah gonar da baba ke magana kanta ki taimaka a sayar da ita azo ayi mashi magana."
Lubna ta ƙarasa maganar da karyayyar murya.

"Gafara can! Ba za'a sayar ba, da in saida gonar nan dana sama raina kaunar ta ƙara in na samu mai sayen ki in sayar a bani kuɗin."
Gaje ta karasa yin maganar cike da masifa.

Mugun hali irin na Sailuba da Gaje a nan take suka shirya gidan aikin da zasu kai Lubna a basu Adadin kuɗin da suke buƙata sai Lubna tayi aiki na adadin kuɗin.

Cikin ikon Allah ashe gidan su Al'ameen aka kai Lubna tayi aiki, a bangaren Hajiya Salima, sosai Hajiya Salima ke ƙaunar Lubna ganin irin jarabtar da Allah yayi mata, ba wani aiki mai

wahala take sanya ta ba daga wanke wanke sai sharar ɗakin Al'ameen girki ma ba koda yaushe take yi ba.

Ubangiji yakan jarabci bawan shi ta kowa ne fanni to haka ce ta faru ga Lubna tun bayan sanya idon ta kan AL'AMEEN taji kaf duniya babu wanda take so sama dashi.

Sabanin Al'ameen da tunda ya hada ido da ita yaji sam bata yi mashi ba da gangan zai sata aiki da tayi kuskure ya hauta da cin mutumci in bayan idon Hajiya Salima ne ya haɗa mata hada duka.

Saratu ta samu ta sanarma da  damuwar ta, nan fa Saro ta tubure tahau bala'i ita bata yarda ba Lubna tabin kwalwa ne ya sameta ta rasa wanda zata so sai wanda ke gana mata azaba.

Ganin ran Saro ya baci yasa daga ranar bata kuma yi mata magana ba.

Al'amarin asibiti kuwa jikin Malam Sule ya fara samuwa amma jin halin da Lubna ke ciki ya ɗaga mashi hankali ɗiyar shi zasu tura aikatau? Ganin halin da yake ciki yasa bai tayar da maganar ba, Kulu kuwa ganin mahaifinta na kwance ba lafiya yasa ta buɗe sabon babin yawo domin kuwa yanzu babu mai kwabarta bare kyara.

Lubna ce cikin dakin AL'AMEEN tana ta faman gyara cike da damuwar rashin ganin Al'amedn ɗin a yau.

Share ɗakin tayi tas tare da feshe shi da kayan ƙamshi na ɗaki  mai daɗin kamshi, tsaye tayi tare da kallon photon Al'ameen da aka aje a bedside hannu ta kai ta ɗauka tare da zama a gefen gadon tana mai ƙarema photon kallo.

Tsaye yayi sororo ganinta bakin gadonshi zaune, ashariyar daya ɗura ce ta sanyata saurin tashi tare da sakin photon a matuƙar firgice.

"Kee! Da wannan ƙazamar fatar taki da kazamin jikin ki kika zauna mani saman gado, minahika da wata fuskarki ta munagince kullum a rufe bana hanaki shigo mani ɗaki ba."
Cewar AL'AMEEN yana mai tunkaro inda take.

"Dan Allah kayi haƙuri hajiya ce ta sanyani in gyara maka."
Maganar ta ce ta kasa karasawa sakamakon ɗauketa da wani wawan mari da yayi.

Wata mahaukaciyar kara ta saki tare da zubewa saman gadon bata numfashi lokaci daya wani

kakkauran jini ya fara bin kafar ta.

Ihun Lubna shi ya sanya Hajiya salima da Alhaji shigowa dakin a guje.

Abinda idanunsu ya gane masu ne Lubna kwance saman gadon Al'ameen ga jini yayi kaca_kaca ya sa hajiya Salima dafe kanta tare da furta "INNALILLAHI WA'INNA ILAIHIRRAJI'UN, AL'AMEEN mika aikata haka."?

Kafin ya fita daga cikin rudun tambayar da hajiya ta jeho mashi Alhaji ya ɗauke shi da wasu lafiyayyun maruka dama da haggu.

Lokaci daya jijiyoyin kan Alhaji suka yi burɗin_burɗin
"Mu zaka zubar ma da mutumci, diyar mutane ka lalata Al'ameen, innalillahi wa'inna ilaihirrajiun, fyaɗe Al'ameen a cikin gidana, abinda zaka saka mana dashi kenan."?
Ya karasa maganar Cike da bacin rai.

Zafin marin ne ya kara gigita kwalwar Al'ameen da kuma tuhumar da ake mashi wadda sam bai san mi ake nufi ba.

"Wallahi tallahi bazaka zubar mana da mutumci ba, dan haka ka shirya nan da sati mai zuwa za'a hada da ita da Leemcy a ɗaura maka aure dasu...

*MEEN@T...✍🏻*
[7/24, 9:07 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine
```

ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE1️⃣1️⃣_1️⃣2️⃣*
...Zafin marin bai hana shi buɗe baki da ƙyar tare da nuna Lubna dake kwance bata san mi ake ba.
"Daddy waccan halittar zaka ce in aure, wallahi na tsane ta bani ƙaunar ta na tsane ta, zani iya kashe kai na, in kace sai na aure ta, da in rayu da ita ƙara na rayu da baƙar macijiya."
Marin da Alhaji Sufyan ya sake ɗauke shi dashi ne yayi sanadin maƙalewar sauran maganar a bakin shi.

"Ƙarya kake, karyar ka ta sha ƙarya har ka isa in yi magana ka musa ko ka ƙi koka so ya zama wajibi ka aure ta na gama magana."
Alhaji Sufyan ya ƙarasa maganar tare da ficewa a ɗakin rai a matuƙar bace.

Hajiya Salima dake rakube yau kukan ma ta kasa sai wata ajiyar zuciya da take saukewa duban AL'AMEEN tayi.
"Baka kyauta mana kana cin amanar tarbiyar da muka baka, miyasa? AL'AMEEN miyasa zaka aikata haka, yanzu ya zamu ce ma itayen yarinyar nan innalillahi wa'inna ilaihirraji'un."

Kasa furta koda kalma ɗaya ce yayi domin yau komi ganin shi yake tamkar a mafarki, "shine zai auri waccan halittar, ina bazai yiyu ba natsane ta."
Ya karasa maganar zucin tare da nufar inda mahaifiyar shi take.

Kafin ma ya karaso inda take gani yayi ta ɗaga mashi hannu tare da mikewa ta nufi gadon da Lubna ke kwance.

Da kyar Hajiya Salima ta yi nasarar shigar da Lubna cikin ɗakin nata, harta gyara mata jikinta bata farka ba sai ajiyar zuciya da take ta faman saukewa.

Ita mace ce dan haka ta fahimci abubuwa da dama game da Lubna amma fahimtar abinda tayi bazai sa ta faɗa ma Alhaji gaskiya ba a fasa auren, harga Allah tana matuƙar ƙaunar hada jini da lubna ita saman lalurar ta bata dameta ba hankali da natsuwar ta suke ƙara burgeta.

Bayan fitar Alhaji kai tsaye asibitin da ake kula da Malam Sule ya nufa.

Jin maganar da mahaifin Al'ameen yazo da ita ba karamin dadi tayi ma Malam Sule ba, koba komi kafin yabar duniya yana da tabbacin ya bar Lubna a family din da yana da tabbacin ko da mutuwa yayi zasu kula da ita.

Babu bata lokaci ya bada auren Lubna ga Al'ameen tare da fada mashi matsalar da Lubna ke fama da ita, kuma anan take yayi ma Alhaji Sufyan wasiyyar koda kafin ranar daurin auren ya mutu kada a kuskura a daga daurin aure.

Bakaramin dadi yaji ba lokacin da yaji Mahaifin Lubna ya amince dan haka tashi yayi tare aje mashi makudan kudade na nagani ina so da kuma na kayan sa biki da ba'a kawo ba, su biyun su suka sa biki ba tare da kowa ya sani ba.

Bayan tafiyar Alhaji Malam Sule mikewa yayi zaune domin yanzu jikin shi Alhamdulillah, shugowar Gaje ce ta sanya shi dago da kai fuska cike da zallar farin cikin wannan al'amari.

Sam hankali Gaje yana kan turin kudin da ta hango tsube gaban Malam, cikin azama ta mika hanmu tare da daukar bandir daya tana juyawa.

"Malam wane ne wannan bakon domin ni bansan shi ba, amma dai mai arzikine ko, wannan kudin duk naka ne ya mallaka maka."?
Gaje ta karashe maganar tana washe baki.

"Nasan dai sunan shi a cikin gari hasalima ban taba ganin shi ba sai yau din nan, wannan bako ba kowa bane face Alhaji Sufyan garkuwar talaka."

Jin wannan suna yasa ta sake wangale baki domin kuwa babu wanda bai san Wanban sunan ba.
"Cewa zaka yi zakka ce ya fidda ta fado mana."

Ganin yadda ta rude ganin wadannan kudi murmushin takaici tayi.
"Wadan nan kudi da kike gani ba kudin komi bane face nasa ranar babbar diyar ki wato LUBNA."

A gigice ta saki kudin suka watse a kasa tare da dafe kirji.
"Ban fahimci abinda kake son fada mani ba, ka fito fili kayi mani bayani, domin nidai nasan Lubna ko kare bazai furta yana sonta ba, kai in takaice maka magana ni nasan babu wanda zai

iya auren ta bare kuma kace daga gidan Alhaji Sufyan Garkuwan talaka ake neman auren wannan Annobar, ka fito fili ka fada mani inda ka dosa hala Kulu kake son cewa ka furta LUBNA."?

Murmushi yayi irin na Dattawa.
"Kamar yadda kika ɗauki Lubna kika kai aikatau to burinki ya cika yaron masu gidan ya bata mata rayuwa amma halayya irinta Garkuwar Talaka yazo ya nema ma danshi auren Lubna kuma na bashi nan da sati daya za'a daura aure, kudin dake hannunki kuma kuɗin auren Lubna ne."

"A hayye nanaye! Ba tun yau ba na fada maka banida burin daya wuce inga Lubna ta wulakanta, tun suna jarirai in baka manta ba sai da nace mu kashe ta ko kuma mu je mu jefar da ita amma ka ƙeƙashe kasa ka ƙiya dan yanzu ta wulakanta ni ko a jikina koda yau a ce kashe Lubna yayi ko a jikina sai ma godiya da zanyi ma shi, aure kuma ina bakin ciki indai nina haifeta ba'a taba daura auren nan ba sai ya sakota ta dawo gida."
Ta ƙarasa maganar tare da mai da duban ta ga Malam Sule.

"Bakar fatarki sai dai ta kare kanki amma badai Lubna ba, Gaje ki kiyayi ranar da Allah zai kama ki da haƙƙin wannan yarinyar domin Allah ba azzalumin bawa bane, aure kuma In shaa Allahu kamar anyi ne."

"Ayi mugani in tusa zata hura wuta."
Gaje ta karasa maganar tare da barin ɗakin fuuu!.

A hankali ta fara buɗe idon ta daya yi mata nauyi, saurin karasa miƙewa tayi tare da koƙarin saukowa ƙasa dan sai yanzu ta lura bisa gadon uwar dakin ta take kwance, ga kuma Hajiya Salimar gefen gado.

"Aa koma ki kwanta jikin kin na buƙatar hutu, kada ki damu yanzu matsayin sirikar gidan nan kike.

Wani banbarakwai Lubna taji maganar hajiya Salima.

Sannu ta fara yi mata tare da bata haƙuri akan abinda ya faru, bata kawo komi cikin ranta ba domin ta dauka tana bata haƙuri ne bisa ga tagwayen marukan da AL'AMEEN ya sauke mata da suka yi sanadin suman ta.

Kamar yadda ta saba yau ma shiryawa tayi bayan gama aiki ta nufi asibiti, a nan farfajiyar asinitin an fito da marasa lafiya suna shan iskan Ubangiji wasu kuma an kama su suna tattakawa domin samun karfin jikin su.

Wurin mahaifinta ta matsa tare da gaidashi da jiki, wani mugun kallo ne Gaje ta aika mata tare da kutawa.

"Kin dawo daga yawon karuwancin."?
Gaje ta fada a ƙufule.

Gabanta ne yayi mummunar faɗuwa jin abinda mahaifiyar tata ta fada mata, domin yau ne karo na farko da ta fara furta mata wannan kalmar.

Mikewa Gaje tayi tare da rufe Lubna da bugu tana sababi tare da ɗaga murya.
"Abinda kika aikata ya dawo mana, miya mai doki wurin mu lalatacciya mara daraja, batun yau ba nike fatar in kin lalace kiyi nesa damu to yanzu mizai sa ki dawo gabanmu miya maidoki."
Duk wannan hayaniya da Gaje keyi mutanen wurin na saurara dan haka a guje sukayo kanta tare da ƙokarin kwatar Lubna.

Da ƙyar suka yi nasarar kwace Lubna da gefen fuskar ta ke zubda hawaye.

"Mi yasa zaku kwace ta, ita ba mutuniyar kirki bace da kuke ganin ta karuwa ce lalatattace la'ananniyace tsi..."
Maganar ta ce ta dakata sakamakon wata mahaukaciya tsawa da Malam Sule ya daka mata.

Kafin yayi ƙoƙarin furta wani abu gani akayi wani wani tari ya sarke shi lokaci daya ya fara aman jini ta hanci da kuma baki.

Likitocin da isowar su kenan a guje suka shige da Malam Cikin Emergency.

Nan fa mutane kowa ya fara surutun diyar kishiya ce da gani domin babu wanda zai yima ɗanshi haka.

A gigice ta nufi inda taga anyi da mahaifinta, "Koki bar asibitin nan ko kuma in zama ajalinki."
Gaje ta faɗa tare da tunkaro Lubna.

Babu shiri Lubna ta fice daga asibitin cikin zallar tashin hankali tare da nufar gidan su Al'ameen bala'i ma in yayi yawa kuka ma kasa yi kake dan haka gudu kawai take cike da zallar tashin hankali.

Dawowar Daddyn Al'ameen kenan yana sanar dasu yadda suka yi da Mahaifin Lubna domin bai boye mata komi ba yadda sukayi dashi kaf ya kwashe ya fada mata.

Jinjina lamarin ta fara domin abun da daure kai yake a ce uwa ce ke yima diyar da ta haifa haka.

Banko ƙofar da akayi ne yasa su kallon ƙofar a rikice, Lubna ce da Kallo daya zakayi mata ka gane bata cikin natsuwar ta.

"Ku taimaka bani Babana zai mutu, dan Allah ku taimaka mani."
Ta karasa maganar tana shassheka.

A rikice suka miƙe tare da hada baki.
"Miya sami babanki."

"Zai mutu."
Ta karasa maganar tare da yin zaman yan bori.

Salati da sallallami suka hau yi tare da daukar key din mota su nufi asibiti.

Duk yadda Mahaifin Al'ameen ke tsala gudu bisa titin amma Lubna gani take yi kamar ba gudu yake ba.

Suna isa asibitin ta bude motar tare da fita a guje, bayan ta su Hajiya suka bi.

Tsattsaye suka iske su Gaje da Kulu bakin kofar ɗakin.

Likita ne ya fito tare da kallon su.
"Wace ce Lubna da Alhaji sufyan."?
Likitan ya faɗa.

"Gamu nan suka fada da sauri."

"Ku shigo yana buƙatar magana daku."

Bayan likitan suka bi zuciyoyin su cunkushe da damuwa.

Ganin mahaifin nata kwance magashiyan ji tayi wani sabon kuka yaxo mata

"Lubna yanzu ba lokacin kuka bane, domin kuwa kukan ki yazo karshe Ubangiji ya yaye maki damuwar ki ya hada ki da sirikai na gari, Lubna ko yanzu nabar duniya Alhamdulillah na damƙaki a inda bani dana sani ko alama."

Jin maganganun mahaifin nata tayi tamkar a mafarki, "yau she aka sa mata biki da wani ba tare data sani ba."?

Nan mahaifin ta ya kwashe kaf abinda ya faru ya sanar da ita, ita kam tama rasa kukan mi take najin dadi ko kuma na fuskantar ƙalubalen irin rayuwar da zasuyi da AL'AMEEN

"Alhaji dan Allah ina neman wata alfarma , in zaku tafi ku haɗa da LUBNA na roke ku kada ku sake barinta tazo sai tare da ɗayan ku."

"Babu matsala Malam Ubangiji dai ya baka lafiya."

Kamar yadda ya bukata haka aka yi domin suna tashi tafiya gida da ita suka haɗa suka tafi.

Al'ameen kuwa da jinshi yaje tamkar a mafarki miƙewa yayi tare da barin gidan cikin ƙunar zuci.

Kai tsaye LEEMCY ya kira suka yi mahada a gidan su domin yau bata kaiga fita ba.

Jin abinda ya fada ne ya sa ta sakin wata kara tare da yin tsalle ta dira..

"Ni zaka yima haka Al'ameen! Kishiya tun kafin in aure ka har an baka wata, ni Halimatu bani haɗa miji da wata koma wace ce in bata rabu da kai za zatayi ta rayuwar ta."

"Babu yadda na iya Daddy ne yayi mani umarni, amma kada ki damu domin kaf duniya banga wadda nike ji na tsana ba kamar wannan halittar."

Kuka Lubna ta hau yi tare da shigewa gidan su a guje, sanin halinta na sanin ba zata fito ba yasa shi tayar da mota yayi gaba.

Kuka take tamkar ranta zai fita.
"Ita ce za'a ya kishiya, duk matsayin ta da wayewar ta i ta ce zata zauna da kishiya, wallahi ba zata sabu ba, bindiga a ruwa."

Ƙawar ta Feedo ta rika, suna gama maganar ta katse wayar, ba'a dauki lokaci mai tsayi ba sai ga Feedow cike da tashin hankali domin abinda Leemcy ta fada mata yayi matukar bata mamaki, babu bata lokaci suka fice tare da nufar gidan bokan.

Duk da duhun magriba da gari ya fara hakan bai dame su ba sai ma parking da suka yi tare da shigewa gidan bokan.

Tun bayan fara masu aiki da yayi har yanzu abu daya ake ya kasa ganin komi dangane da Lubna.

Tun yana aiki cikin dadin rai har wata zufa ta fara wanke sassan  jiki.

Wata mahaukaciyar kururuwa bokan ya saki, Su Leemcy dake gaban shi ba shiri suka toshe kunnuwa a matuƙar firgice...

*MEEN@T...✍🏻*
[7/27, 5:59 AM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
        _Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
        *M.W.A*

 *Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
```

https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE1️⃣3️⃣ 1️⃣4️⃣*
...Cikin firgici ya kalle su tare da daka masu tsawar da ta haddasa masu miƙewa zasu zabga da gudu.

"Tafi ƙarfin mu, Ki fidda ran cewa zaki iya galaba a kanta, kada ki sake kuskuren zuwa wurina da sunan kina son ganin bayan ta, ku bace mani da gani."
Bokan ya ƙarasa maganar cikin ƙatuwar murya domin shi kaɗai yasan azabar da ake gana mashi a jikin shi.

"Ka taima mani a duba lamarin nan bani iya zama da kishiya ba."
Cewar Leemcy murya na kyarma.

A fusace bokan ya fara magana
"Ku bace mani da gani ko in haɗa ku da baƙaƙen aljanu suyi maku rakiya."
A guje suka fice daga wurin zuciyar su cike da tsoro.

Sai da suka yi nisa da wurin kafin su tsaya suna mai da Numfashi.
"Kai yau mun auna arziki, Leemcy yau Boka yayi mana abinda bai taba yi mana ba, anya yarinyar nan bata fi ƙarfin mu ba, Bokanta yafi namu iya aiki."
Cewar Feedow tana maida numfashi.

"Ƙarya take koma wane ne Bokan ta tilas ne nima in canza Boka, bani ji zani iya rayuwa da Al'ameen tare da wata, dan haka muje gida gobe ki kuma raka ni wurin wani."
Sai da dare yayi sosai kafin su isa gida.

Abinda zai baka mamaki babu wanda ya tambaye ta dalilin fitar ta balle kuma aji ina taje tayo dare haka...

---

...Ɗakin kusa dana Hajiya Salima nan aka gyarama Lubna, kasan cewar babu mai rayuwa cikin ɗakin duk yayi datti.

Da kanta ta kai ta ɗakin tare da jawo mata ƙofa kasan cewar dare yayi sosai.

Zaune tayi bakin gado zuciyar ta cunkushe da abubuwa da dama a zuciyar ta.
"Bake daya bace zai aura akwai wata da yake so ɗiyar Alhaji Marwan wato Leemcy, Lubna nasan auren nan ƙaddara ce ta haɗa shi kiyi ƙoƙari ki haɗa da hakuri ki so Al'ameen ki fiddo shi daga cikin duhun da yake, ni nasan abun akwai wahala amma hakuri zakiyi ki dage da addu'a Halimatu da kuke gane kowa yasan ba yarinya bace mai jin magana nasan zaman ku ba daɗi zai yi da ita ba amma kiyi hakuri komi ya faru ki ɗauka ubangiji ne ya jarabce ki ta wannan hanyar."
Maganar Hajiya Salima ta riƙa yima Lubna yawo a cikin kai.

Zamewa tayi tare da kwanciya bisa gadon.
"Ya Allah ka ƙara mani hakuri da juriya akan duk wani al'amari da zai same ni, na rungumi ƙaddara ta da hannu bibbiyu."

Alwallah ta tashi tayo tare da tada Sallah.

Bayan ta gama kwanciya tayi domin wani bacci da taji yana fizgar ta.

Bakin wani wawakeken rabi ta ganta tsaye ga wani iska mai ƙarfi dake neman jefa ta cikin ramin, wata bishiya ta ƙama ta riƙe gam tana am ambatar sunan Allah.

Wata bakar hallitta mai mummunar suffa naga ta fara tunkaro in da Lubna ke maƙale tana neman taimako.

Ilahirin jikin halittar gashi ne bazagar_bazagar tamkar wani dodo, idonta guda ɗaya ne sai hannuwa rututu, baki ta wangale tare da kecewa da dariya.

Sai da tayi mai isarta kafin ta turbune fuska tare da nuna Lubna da yatsa.

"Kamar yadda suka tarwatsa farin ciki na na zama bawa gare su nike masu duk wani aiki da suka sani, kema alƙawari ne na ɗauka ba zaki taba farin ciki ba a rayuwar ki damuwa da bacin rai sune Abokan zaman ki, bashin da suka ci kece wadda zaki biya shi ba zani bari a so ki ba bare kuma aure ki dole ne koma waye sai nayi yadda nayi kuka rabu, matsayin baiwa kike a wurin na ke mallakina ce tun shuɗaɗɗen lokaci aka mallaka mani keee."
Yana karasa maganar ya fizgeta suka fada cikin ramin.

A firgice Lubna ta farka daga wannan mummunan mafarki da tayi, Rabin fuskar ta ne taji ya fara motsi, gyalenta ta sanya ta rufe wurin tare da shigewa toilet tayi alwalla ta tayar da sallar asuba.

Bata koma bacci ba domin jin abun tayi wani banbarakwai domin ita a gidan su da asuba Tayi

take tashi ta hau aiki kwata_kwata bata baccin safe.

Haka taita yan tunane_tunane na wannan mugayen mafarkai da suka aure ta kwanan nan.

Hajiya Salima ce ta turo ƙofar hannun ta ɗauke da breakfast, saurin sauko wa tayi tare da gai sheda Hajiya Salima cikin girmamawa.

"Lafiya lau Alhamdilillah ya kika tashi."

"Alhamdulillah ta amsa kanta a ƙasa."

"Lubna!."
Hajiya Salima ta kira sunan ta.

Amsa wa tayi kanta a kasa tana wasa da yatsun hannun ta.

"Kada ki dauke ni a matsayin sirika, ni matsayin ɗiya ta na ɗauke ki, duk wata damuwar ki kada ki boye mani dake da Al'ameen duk ɗaya na ɗauke ku a wuri na."

Kanta a kasa ta furta.
"Nagode mommy."

Ba karamin daɗi Hajiya Salima taji ba da kiranta da Lubna tayi da Mommy.

Hajiya Mariya kuwa jin abinda ya faru nan ta shiga yan haibace_habaice tana sakin magana.

Hajiya Salima mace ce mai haƙuri da kawai ci dan haka ba ta bi ta kan ta ba bare kuma suyi rigimar da Mariya ke nema.

Fadila kuwa indai zata ga Lubna yanzu zata fara kiran ta da karuwa anzo an biyo abokin iskanci an nanike masu a gida.

Hajiya Salima ita ke kwantar ma da Lubna hankali tare da karfafa mata guiwa

Saratu kuwa jin kawar tata shuru bata sake dawowa unguwar ba kuma taje asibiti bata ganta ba yasa yau ta yanke shawarar zuwa gidan su Al'ameen koma mi zai faru sai dai ya faru.

Lubna na kwanceba cikin dakin ta taji Saratu ta turo kofa da zallar farin ciki suka  rungume juna tare da zama bakin gadon.

"Lubna kinga kuwa yadda jikin kinya koma kinyi fresh rama ce kadai naga kin ɗan yi, shi wai mima kike yi a cikin gidan nan."

Nan fa Lubna ta kwashe kaf abinda ya faru ta sanar da Saratu.

Guda ta yi tare da furta Alhamdulillah.
"Buri na zai cika zakiyi aure a gidan da koda wancan gantalellen Al'ameen ɗin bai sonki to iyayen shi na sanki, ita kuma waccan da kika ce kina tsoro ni har kin bani kunya ita ɗin banza, ke tsaya kiji wallahi ki cire ma kanki tsoron wata kishiya yadda take matsayin matar shi kema haka keda ma kike da digi Mahaifan shi na matuƙar ƙaunar ki akan wane dalili zaki sama kanki tsoron wata banza, cikin hidimar bikin nan ni sai na kimtsama duk masu yi maki wargi zama ɗaya bayan ɗaya, kai ayyiriririreeee."
Saro ta sake guda.

Fadila da tazo giftawa ta ƙofar dakin Lubna jin guɗar ne ya sanya ta turo ƙofar.

"Uban waye ke yima mutane guɗa cikin gida kamar na iyayenshi."
Cewar Fadila tana ƙoƙarin shugowa dakin.

"Uwar ki ce keyin gudar ko akwai yadda za'ayi dani."
Saro ta fada tare da turo ɗan kwali gaban goshi.

Jin wannan zagi da aka maida mata ne ya sanya ta shigowa ɗakin da sauri.

Turus taja ta tsaya tare da ƙarema Saro kallo.

"Wace marar kunyar ce a cikin ku nayi magana ta zage ni."
Cewar Fadila tana mai riƙe kugu.

Saurin riƙo Saro Lubna tayi tana ƙoƙarin hanata magana magana.

"Ke ar! Uwar yan tsoro ni sakar mani hannu domin dai_dai nike da zamaninta, nice nan na baki amsa ko akwai yadda zakiyi dani."?
Cewar Saro

"Ke ni kike kallon idona kike fadama magana."
Cewar Fadila tana mai nuna saratu da yatsa.

"Naga dai ke mutumce a cikin mutanen ma kuma mara tunani gallaƙeƙiyar banza, ko zamu gwada ƙwanji ne a fidda reni."

Ganin yadda Saro tayo kan fadila, kuma fadila taga lallaifa inta tsaya tana ruwa domin Saro ba irin Lubna bace da suke cin zalinta tana kyalewa.

"Ke ɗin mi, akan wane dalili zani hada jiki da ɗiyar talakawa ai sai ƙimata ta ragu, gayyar tsiya anzo an addabi mutane."
Fadila ta karashe maganar tare da barin ɗakin cikin sauri.

"Ai da kin tsaya yau dana gwanje wannan bakin inga gobe damu zakiyi ma wani rashin daraja, ke kuma ki zauna kowa ya riƙa taka ki kinji."

"Tashin hankali ke bani so."

"Nabi rashin san tashin hankali a guje buje a hannu, ke ki saurara kiji wallahi tun yanzu ki miƙe ki zama mai kwatar ma kanki yanci in kika zauna haka kuwa to kowa ma zai ci gama da taka ki kina nan zaune sasakai."
Saro ta karashe maganar tana jifa ma Lubna harara.

Sai gaf da magriba Hajiya Salima tasa driver yakai saratu har gida.

Al'ameen kuwa abun duniya duk ya isheshi domin yanzu jin soyayyar Leemcy yake tamkar ta kashe shi.

Kai tsaye gidan Bilal ya wuce.

Jin wanna jawabi na Al'ameen yasa Bilal yi ihu tare da ba abokin nashi hannu.

"Shegen sama, kace kai auren gata iyayen ka zasu yi maka, kai wallahi su Hajiya na ƙaunarka ba kaɗan ba, Mata biyu a rana ɗaya."

Ganin yadda Al'ameen ya bata rai yasa Bilal kecewa da dariya.

"Kaga angon mata biyu, miji ga Leemcy da kuma Lubna, wannan haɗi shi ake kira riba biyu."

Bilal ya karasa maganar tare da kecewa da dariya.

Rai bace Al'ameen ya mike tare ds furta.
"Sai kayi da wani kuma, ni na bar maka gida."
Ya karasa maganar tare da ɗaukar key yayi gaba abinshi.

"Kaga aboki yi hakuri dawo mu karasa irin shagalin da zamu sha nan da kwanaki uku."
Ko juyowa Al'ameen bai yi ba ya Tayar da mota yayi gaba.

Ganin shigowar Al'ameen ne yasa Hajiya Salima kiran Lubna tare da bata Coffee ta kaima Al'ameen.

Jiki a sanyaye ta furta, "Mommy!"

"Kin ga Lubna ban san ki da gardama ba amshi kawai ki kai ma shi."

Babu musu ta amshi Coffee ɗin tare da nufar part ɗin Al'ameen gabanta na faɗuwa, kasan cewar magriba ce bata iske kowa falo ba kai tsaye ɗakin ta nufa.

Tura ƙofar tayi bakin ta ɗauke da sallama.

Ba tare daya amsa ba ya ɗago tare da kallon ta.

"Kee! Wane tsautsayi ne yasa kika kwaso wannan mummunar fuskar taki kika shigo mani ɗaki."
Cewar Al'ameen yana mai dirowa daga saman gadon.

"Mommy tace in kawo maka Coffee."
Ta fada murya na kyarma.

"Ok! Jira ki gani."
Amsar zazzafan Coffee ɗin yayi tare da juye mata shi akai

Cikin rashin sa'a Coffee ɗin ya zuba a bangaren fuskar namijin.

Wata ƙara ta saki tare da dafe fuskar ta, lokaci daya ƙofar ɗakin Al'ameen wani iska mai matuƙar ƙarfi ya rufe ta ji kake garam!

Wutar dakin ce ta dauke wata mahaukaciyar dariya aka kece da ita cikin mabanbantan muryoyi...

...Murja dake ta sharar baccin ta ba tare da sanin abinda ke faruwa ba haka wannan hannu ya rika sulalowa tare da wanka mata mari.

A firgice ta farka daga baccin tare da kallon abinda ke gabanta, ihu ta saki ganin gundulmim hannu babu gangar jiki a gabanta.

A gigice ta diro daga saman gadon ta fada Toilet tare da banko ƙofa ta rufe tana maida numfashi.

Rashin dabara da rabon wahala yasa ta nufi gaban mirron dake manne jikin bango da nufin duba inda aka wanka mata mari.

Saurin waigawa tayi bayan ta ganin sak wata Hajiya murjar irinta ta cikin Mirror tana mata dariya.

A gigice ta juya bayan ta dan ganin koda gaske ne abinda ta gani cikin Mirron.

Wayam! Babu kowa bayan ta babu kowa, sake juyowa tayi ta kalli mirror nan fa taga da gaske mai suffar ta ce.

Ja ta fara yi da baya cike da zallar firgici, caraf Murjar cikin mirror ta zuro hannu tare da shaƙe Hajiya Murja ta ainahi.

Idanun ta ne suka fara firfitowa waje, daga cikin Mirror ta riƙa fitowa har sai da ta fito gaba ɗaya.

"A tunanin ki duk inda kika je ba zamu iya binki ba."?

"Muna tare dake ruhinki bazai taba samun salama ba kamar yadda muma kika salwantar da farin cikin kinmu."
Dagata tayi da hannu biyu ƙafar ta na wutsil niya a sama.

Sakin ta tayi ta faɗo kasa tare da bace wa bat, wuyan ta take shafawa cike da tashin hankali domin ba karamar shaƙa akayi mata ba.

Da kyar ta miƙe tare da dafa ƙofa da nufin ta bude, kafin hannunta yakai ka ƙofar ji tayi ƙofar Toilet ɗin ta bude da kanta.

Falon ta saka kafar ta cike da tsoro tana sanda zata koma ɗakin ta,  da gudu taji an gifta ta bayan ta, saurin juyiwa tayi cike da fargabar abinda zata gani.

Wayam! Bata ga kowa ba, ajiyar zuciya ta sauke tare da dafe kirji, ƙit! Taji ƙaruwar plasma dake manne jikin bangon ɗakin ta kunna kanta.

Jariri ne karami ya bayyana cikin Tv ɗin yana mata dariya, tsabar firgita kasa motsawa tayi daga inda take sai jikin ta dake kyarma tamkar mazari.

Wani jaririn ne ya sake bayya suka ci gaba da dariya, "Mama suka furta a tare."
Suna masu nuna ta.

"mu fito zuwa gareta."
Taji jariran sun furta.

Kafin tayi wani ƙoƙari gani tayi jariran sun fara fitowa daga cikin Tv ɗin tamkar ana amayo su kwatsa_kwatsa, ganin yadda dandazon jaririran suka yo kanta yasa ta sulalewa kasa.

Ba ita ta farka ba sai da gari ya waye tangaram, tsamin da jikin ta yayi mata ne ya sa ta dafe bayanta dake mata matuƙar ciwo.

A gogon dake manne jikin falon ta kar ƙarfe 12:30 da rabi dai_dai cike da mamaki take kallon tsayin lokacin da ta kwashe a sume.

Mikewa tayi tare da nufar Toilet turus! taja ta tsaya sakamakon tuno abinda ya faru jiya.

Ganin bata da wata mafita Yasa ta fada Toilet ɗin tare da yo wanka ta yo ta fara rama sallolin da ake binta.

Mai aikin ce ta kawo mata abinci tare da juyawa zata fita.
"Uwani."
Hajiya Murja ta kira sunan mai aiki.

"Na'am ranki shi dade."
Uwani ta amsa tare da dukawa.

"Hibba fa kin kai mata nata."

"Aa Hajiya yau Hibba tun safe ta fita."

"Je kici gaba da aikin ki."
Hakiya ta faɗa tare da sauke ajiyar zuciya jin Hibba ta fita ba karamin daɗi yayi mata ba.

Bayan gama cin abincin shiri ta hauyi domin yau dole taje ta sanar da mahaifinta abinda ke faruwa, wajen karfe uku na yamma ta shirya tare da nufar gidan tsohon shugaban ƙasa wato Alhaji Mamman wada.

Bata yadda driver ya bita ba domin yau tana so ne suyi sirri bata so kowa yaji.

Gudu take tsalawa tamkar zata tashi sama, zuciyar ta cunkushe da abubuwan da dama.

Abinda ya shude shekara da shekaru ne ya fara dawo mata tamkar a lokacin ya faru, firgigit ta dawo daga duniyar tunanin da ta afka sakamakon ganin Hibba da tayi tsaye gabanta tana niyyar taka ta da mota, a firgice Hajiya Murja tayi niyyar kauce mata ta hanyar ɗibar wata hanya daban kafin tayi ƙoƙari taka birki motar ta kwace mata tare da kai ma wani iccen bedi dake gefen Hanyar karo, a cike da tashin hankali mutanen da abun ya faru kan idon su suka yo kanta...

*MEEN@T...✍🏻*
[7/29, 5:55 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*
```

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*TALLAH!*
Ina mata yan kwalisa , mata masu aji ,KASAITATTUN  mata masu mallakan zuciyan me gida kuzo ga ummu Abdullah tazomuku   da mayikan gyara jiki,kala kala,da sabulai na gyaran jiki, da turarreka wuta da na jiki Dana kaya da na tsuguno,da humra kala kala da shi'umar humra, da kayan chemical,irin  su liquid soap, perfume,air freshener,, Hair cream,Shampoo etc tana kuyawa tana hada kaya ,domin Neman  Karin bayani Sai kutuntibi wanna lambar 07046858716.

*PAGE1️⃣5️⃣_1️⃣6️⃣*
...Ƙarar buguwar ƙofar ne ya sanya shi kallon ta raina 6ace, "Ki Bace mani da gani na ce maki." Al'ameen ya faɗa raina matuƙar 6ace.

Ita kam dafe take da fuska ga kuma hasken nepa dake ɗaukewa yana dawowa.

Da yake bala'in cinshi yake ganin hasken ɗakin na ɗaukewa touch light ya zaro tare da haskawa yaga shin ina take.

Wayam babu kowa ɗakin sai shi kaɗai, hannun shi daya ta6a jikinta ya kalla ya wani 6ata rai tare da nufar Toilet ɗin domin wanke hannunshi.

Abun mamaki wutar Toilet ɗin lafiya lau take sabanin ta dakin dake ɗaukewa tana dawowa.

Kai ya tura tare da shigewa ya sakarma jikin shi ruwa tare da rufe idanunshi, ruwan Coffee ɗin daya juyema Lubna akai ne photon yadda abun ya faru ya fara dawo mashi sabo fil.

Saurin buɗe ido yayi tare da nufar Mirror ɗin yana gyara gashin gemonshi, wuƙil! yaga wata baƙar mage ta wulga ta cikin mirror ɗin, a razane ya ɗan juya domin shi kaf duniya babu halittar daya tsana kuma yake tsoro kamar mage.

Dube_dube ya hau yi amma wayam babu mage babu dalilinta, ci gaba da aikinshi yayi tare da watsar da tunanin magen.

Ɗago kan da zai yi ƙatuwar mage ya gani da girmanta ya kai na jaririn maraƙi ta buɗe baki tana babbaka dariya.

Wani gumi ne yaji yana wanke ilahirin jikinshi lokaci daya wata kyarma ta kwace mashi a hankali ya far juya akalar shi domin yaga koda gaske i ta ce,karo yaci da wata mummunar mage da ilahirin jikinta wasu dogayen gashi ne masu matuƙar tsayi, kanta kuwa rabi fuskar Leemcy rabi kuma ta mage.

Kecewa tayi da dariya tare da nuna shi da hannu.
"Kayi kuskuren aikata abinda kayi, ni zaka ƙonama fuska, ka ko san hukuncin wanda ya taba fuskata, ka taba marin fuskar amma na gyaleka amma yau zaka ɗanɗana kuɗarka."
Ta karasa maganar bakinta na fidda wani irin tiriri.

Zubewa yayi bisa guiwar shi, "dan Allah dan girman Allah ki taimaka ki yafe mani, ko kallon inda kike bazani sake ba, anti Lubna na roƙe ki wallahi bansan ke Aljana bace."
Bugun da magen ta kawo mashi a baki ne yayi sanadin hadiye sauran maganganun shi.

"Bani yafiya bani afuwa hukuncin kisa naso yanke maka, amma naga bazani iya kasheka ba duk ƙoƙarin da nayi amma zan Kyale gane ba kowa ake tabawa ba a zauna lafiya."

"Na tuba Lubna ki gafarta mani, ina sonki ina kaunar ki wallahi kece ma Uwar gida ki ceci rayuwata kada ki illata mijinki na roƙe ki."

Kecewa tayi da dariya tare da kallon shi a fusace
"Zaka rayu saboda wani dalilina ba zani kasheka ba amma zaka ɗanɗana kuɗarka.

Tana karasa maganar wasu kananun maguna masu kawuna rututu suka bayya tare da baibaye Al'ameen, kafin yayi wani kwakkwaran motsi tuni sun haje jikinshi masu yakushi nayi masu cizo nayi, ihu yake tsalawa koda za'a jishi a kawo mashi dauki amma a banza suru kake ji domin,Duk ihun da zai yi ba za'a taba jin shi ba.

Babban abinda ke kara ruɗar dashi bai wuce a jikinshi inda jini ke fita ba haka magunan nan ke lasar wurin suna kara girma.

Cak ƙatuwar magen nan ta ɗageshi sama kanshi na reto a ƙasa ta rika hajijiya dashi tammakar yadda fanka ke sharara gudu.

Sakin shi tayi yayo kasa inda shi kuma idanun shi suka hasko mashi wani ƙaton rami da

gefenshi yaya mulmulawa zai faɗa ciki.

Kanshi ne ya bugu lokaci daya idanunshi suka rufe saman girarshi jini ya fara fita, kecewa tayi da dariya tare da lasar jinin shi ta lumshe ido domin tunda take yau ne karo na farko da ta ɗanɗani jinin da bata taba ɗanɗanar irin shi ba.

Rikiɗewa tayi tare da komawa sak Lubna, ta cikin bangon ta rika ratsawa harya karasa ɗakinta, bisa gadon ta zube wani nannauyan bacci yayi awon gaba da ita.

A hankali wani ruhi mai kama da hayaki ya fara fita daga jikin Lubna, har ya fice tas! Shidai wannan abu tamkar hayaki haka yake, suffarshi kuwa namiji ne tsaye.

A hankali ya zo dai dai saitin fuskar Lubna tare da fashewa da kuka mai firgitar da ruhin bil'adam.
"Ban kamaci ratuwa jikin kowa ba amma haka suka mayar dani tamkar bawan su sun rabani da kowa nawa banida sauran gata a wannan dunuyar, taya zani barki kiyi rayuwa cikin farin ciki bayan mahaifanki sune silar komi, zani rayu dake ne har ƙarshen ratuwarki domin a wurina tamkar hadaya kike an mallaka mani ke tun shuɗaɗɗan lokaci."

Ya gama faɗar haka ya ratsa ta cikin bangon tare da shigewa ɗakin Fadila dake faman bacci.

Tun tana jin kukan awakin sama_sama har yayi ƙarfin da yayi sanadin tashin ta daga bacci.

Farkawar ta tayi dai_dai da ganin wasu baƙaƙen akuyoyin masu kai irin na kadangaru idan su ɗata rak a tsakiyar goshi,cike da ɗakin sun buɗe bakuna suna mata ihu.
"Kan uba!."
Fadila ta furta tare da dirowa daga saman gadon.

"Miya kawo awaki cikin ɗakina? Kodai wani ya bude gidan gonar dady ni kuma suka shugo mani daki, ni gidan nan an rena mani wayo awaki har cikin ɗakina dole in iske dady yanzu kuwa."
Ta karasa maganar tare da miƙewa.

"Ni zaki aika ƙafafuna takwas zani fiki saurin kai wa."

"Aa ke baki da gudu nita cikin bango nike bi zani fiki saurin karasa wa."

"Ni uwar garke har ku fada mani sauri yanzu nan zani bace in sanar da Ubanta abinda take faɗa."

A wakin dake gaban Fadila suka hau gardama, a firgice tayi wani wawan tsalle da nufin fadawa bisa gado sai jinta tayi tabar ƙasa.

Kecewa suka yi da dariya tare da yin kuka Meeeeeeyyy!

Ƙara rikicewa tayi domin sai yanzu ta fahimci irin halittar dake jikin su, ihu ta fara tana neman temako.

"Keyi mana shuru ko kema yanzu halittarki ta koma irin tamu."
Zakaƙurar cikin su ta faɗa.

"Na tuba nabi Allah na biku akuyoyi, kuyiwa girman iyayenku ku bar mani ɗaki, wallahi ɗakina ba garken akuyoyi bane."
Ta karasa maganar tana mai sakin kuka.

Garam! Suka gwabje mata baki da kofato.
"Masu daraja kike kira da awaki, maza ɗauko makilin da borosh ki wankema kowa baki in kin ƙiya yanzu jikin ki ya gaya maki."

"Na shiga ukku na lalace tunda nike ban taba gani an yima akuya borosh ba yanzu wannan kawunan naku na ƙadangaru zani wanke wayyo uwata da ubana Hajiya kina ina."?

"Ba zaki fasa kiranmu da akuyoyi ba, Uwar garke ku hora ta."
Tamkar yadda ake buga ball haka awakin suka rika jifa da Fadila in wannan ya bugo tanan sai wannan ya bugo tanan.

Sai da suka yi mata lilis kafin su fara magana.

"Zaki fara wanke mana bakin ko sai jikin ki ya gaya maki."

"Kuyi mani rai zani wanke."
Ta faɗa a gabaice

Haka ta rika bin Awakin nan tana wanke masu baki, da ta fara wanke wa zataji kaf haƙoran sun fara ficewa suna zubowa a hannunta.

Ko kuma tana zura hannu zata fara wanke masu bakin taji sun lafta mata cizo sun datse bakin ga hannunta ciki.

Bata gane bata da wayo ba sai da tazo kan uwar Garwake, tana fara wanke bakin ta hada da hannuwan ta cije, ihu Fadila ta fara tana sakin kuka.

Azaba ranar babu kalar wadda bata sha ba jikinta duk sawun bugu ne fatar ta duk ta farfashe.

Shugabar su ce ta fara magana.
"Wannan hukuncin kadan ne kika gani muddun baki fita sabgar Lubna ba nan gaba yanka ki zamuyi mu tsotse jinin jikin ki kinaji kina gani."

"Ni da ita har abada kai in ma kince ba su kada in sake hada ido da ita to daga yau na dena."

Kecewa suka yi da dariyar da ta haddasama ɗakin girgiza tare da bacewa bat.

Fashewa tayi da kuka tare da fadawa kan gado jikin ta na mata raɗaɗin azabar da tasha.

Lubna kuwa
Kamar yadda ta saba duk safiya sai taje ta gaida su Hajiya Salima yau ma haka taje suka gaisa tayi mata gyaran ɗaki sannan ta nufi kitchen.

Har 12:00 amma sam hajiya bataga gilmawar Al'ameen ba, tunani tayi ta aika Lubna sai kuma wata ziciyar tace taje da kanta ta gani.

Bakinta ɗauke da sallama ta tura ƙofar ɗakin, turus taja ta tsaya tare da rafka salatin daya jawo hankali Lubna da Daddyn Al'ameen suka shugo ɗakin a rikice.

Kuka Hajiya Salima keyi iyakar karfinta tana ambatar sunan Allah, waya Alhaji ya zaro a rikice tare da kinran family doctor nasu, Lubna kuwa wani kuka ne ya kubce mata ganin Al'ameen yashe babu alamun rai a tattare dashi...

---

...A wani ƙasurgumin jeji Hibba ta bayyana fuskar nan a turniƙe

Yanayin jejin kadai ya isa ya firgita Ruhin bil'adam amma Hibba ko ajikinta sai ma kara ƙaimin

kutsawa da take cikin jejin.

Bakin wata bishiyar Kuka ta tsaya tare da Nuni da hannu ƙasan bishiyar take wata guguwa ta taso ta turniƙe wurin lokaci ɗaya wani rami ya bayyana a ƙasan bishiyar.

Cikin ramin ta shige tare da dauko wani katon akwati da aka ƙera da zallar karfe, direshi tayi a kasa tare da rungumeshi tana mai fashewa da kuka lokaci daya jejin ya fara girgiza tsuntsaye na tashi sama.

"Sun azabtar da ruhinka sun salwantar da rayuwar ka sun mai dani mareniya bani da kowa a wannan duniyar sai kai daya,alƙawari ne na ɗauka sai naga bayan duk wanda keda hannu cikin wannan al'amarina ne."
Ta karasa maganar hayaƙi na fita a bakin ta.

Hajiya Murja kuwa ganin yadda goshin ta ya fashe ga jini kaca_kaca yasa mutanen daukar ta tare da nufar asibiti mafi kusa

Emergency aka shiga da ita domin wasu ma suna kyautata zaton ta mutu ganin yadda suka dauke ta.

Jikkar ta aka duba nan aka ga wayar ta cikin,sunyi sa'a wayar a bude take bata sa password ba, Hajiya Turai shine kira na ƙarshe a cikin wayar ta dan haka nan suka kira amma kwata_kwata wayar bata shiga, Abban Hibba shi suka kira, ta can bangaren shi anyi sa'a yana kan hanya dan haka Hibba ya kira ta iso kafin ya ƙaraso.

Kashe wayar Hibba dake makale saman fanka tayi tare da fashewa da dariya, ƙafarta ita ce sakale jikin fanka inda kanta da hannuwanta suke reto a kasa.

"Ko baka kirani ba yanzu zani wuce asibitin, Burina shine in ganta cikin masifar da sai ta kwammace mutuwa da rayuwar da zatayi."
Tana karasa maganar tamkar tsuntsuwa haka ta diro daga saman fankar, komi nata tsayawa yayi domin Jikinta ya bata akwai wani a laɓe a inda take.

Kanta ne ya juyo tare da kallon bayan ta, Uwani dake labe jikin Window ihu ta saki tare da ƙoƙarin guduwa.

Kwatsam! taga Hibba ta bayyana a gaban ta, "Hhh ni zaki ha'inta Uwani ni zaki tonama asiri, wanda duk ya shiga hanyata kauda shi nake, domin ni ruwa ce in na taho babu mai tare mani hanya."

Jiki na ciri ta bude baki da nufin yin magana.
"Ki gafarce, kiyi mani rai babu wanda zai san da wannan maganar nayi maki alƙawari."

Kecewa da dariya Hibba tayi.
"In kin rayu ne har zakiyi ƙoƙarin tona mani asiri."
Tana karasa maganar tayima Uwani wata shaƙa lokaci ɗaya idanunta suka fara firfitowa jinin jikinta ne Hibba ta fara tsotsewa sai da ta gama tsotseshi tas fatar Uwani ta koma fara sol kafin ta saketa ta faɗo ƙasa a ma ce.

"Duk wanda yayi ƙoƙarin tona mani asiri mutuwa ita ce sakamakon shi."
Tana karasa maganar Ta ratsa ta cikin bango ta nufi asibiti...

*MARASA COMMENT DUK WANI HAKURI NAYI AMMA TABBAS YAU A WAJE ZANI TATTARA KU IN WATSA KUMA ALƘUR'AN KADA WADDA TA BIYONI PC DOMIN NASON MASU COMMENT, KUMA NASAN YAN ZAMAN KASHE BUJE*

*MEEN@RT...✍🏻*
[7/30, 11:44 AM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---
```

*PAGE1️⃣8️⃣_1️⃣9️⃣*
...Kamar yadda tayi niyya haka ta bayyana kwatsam cikin asibitin, duk inda ta wulga dole ne a bita da ido wasu ma harsai ta bace ma ganinsu, domin Hibba mace ce mai matukar kyau kana iya ma tunanin bata cikin jinshin mutane kyawunta yayi yawa.

Ba ta tambaya ba bare ace dama can tasan ɗakin da mahaifiyar ta ke zaune, kai tsaye ɗakin ta tura babu ko sallama haka ta afka ɗakin, mahaifinta tagani zaune bisa kujera kusa da mahaifiyar ta.

Ɗago kanshi yayi tare da kallon ta, "Hibba duk mi kike har haka ace nida ke nesa sai da na rigaki zuwa wurin nan, shin wai bisa mima kikazo domin lokacin da na kiraki ina cikin asibitin nan yanzu kuma ko minti goma ba'ayi ba amma gaki kin karaso."?

"Kana buƙatar sanin abinda ya kawo ni ne."?
Hibba ta faɗa murya ƙasa.

"Mikika ce."?
Abban Hibba ya tambaya.

"Ni Abba bani son yawan tambaya dan wata rana in dai kana ƙure ni da tambayoyi tabbas zamu samu matsala dakai dan haka yanzu dai gani ya jikin Umma."?
Hibba ta karasa maganar tare da matsawa gafda gadon mahaifiyar tata.

Cike da zallar mamaki Mahaifin nata ke kallon ta.
"Kwata_kwata kwanan nan ya rasa mike damun Hibba bata jin nauyi tayi mashi abinda taga dama ga rashin nuna kulawar ta ga mahaifiyar ta amma ya dauki laifin faruwar haka ya dora a kan su domin su suka yi mata tarbiyya a haka, ganin irin yadda jikin Hajiya Salima yayi laushi yau ta matuƙar jigatuwa yasa Alhaji kiran mahaifinta ya sanar dashi halin da ake ciki.

Kafin kace mi karar jiniyar motocin jami'an tsaro ta cika asibitin, wanda suka yo ma tsohon Shugaban kasa rakiya, yana fitowa jami'an tsaro suka take mashi baya cike da girmamawa.

Kallon daya zaka yima irin tafiyar da yake ka fahimci irin saurin da yake na ganin tilon ɗiyar tashi data rage mashi a duniya.

Karo yaci da Hibba tana fitowa daga ɗakin da Hajiya Salima take, ko kallon inda yake bata yi ba

ta raba shi zata wuce.

Ganin jami'an tsaro sunyo kanta zasu kwasheta daga hanyar yasa Alhaji mamman dakatar dasu.

"Hibba ya jikin mahaifiyar taki."?

"Ba gaka a kofar dakin ba zaka iya shigewa ka gani."
Hibba ta faɗa tana mai aika mashi da mugun kallo.

Tuni masu tsaron lafiyar shi suka yi kanta a fusace, tsawar daya daka masu ce ta dakatar dasu, domin inda sabo ya saba da kiyayyar da jikar tashi ke nuna mashi tun tana ƙarama dan haka bai bi ta kanta ba ɗakin suka shige.

Hibba kuwa jikin ta wata iriyar tsuma da yake ji tayi inama ace ba a bainar jama'a take ba da babu abinda zai hana ta salwantar da rayuwar mutumin can.

Ciki ya iske Abban Hibba, bayan sun gama gaisawa ne Hajiya Murja ta farka, ba karamin daɗi taji ba da ganin mahaifin nata wani kuka ne ya kubce mata domin harga Allah mahaifinta kaɗai take raba taji sanyi a ranta.

"Murja miya fito dake ba tare da driver ba, shin bana hanaki fita ke ɗaya ba, kina so ki salwantar mani da rayuwar ki ne in rasaki kamar yadda na rasa mahaifiyar ki."
Mahaifinta ya karasa maganar cike da kaunar ɗiyar tashi.

"Kayi hakuri gani nayi in zani je gida har sai na tafi da wani driver, amma nayi alkawari hakan ba zata sake faruwa ba.

"Mi likitoci suka ce game da lafiyar ta, ko akwai matsala mu fiddata kasar waje."?
Mahaifin Hajiya Murja ya tambaya.

"Aa Alhaji likita yace buguwar da tayi ce kanta ya fashe amma jikinta Alhamdulillah tana samun sauƙi zuwa gobema za'a iya sallamar ta."

Duk da basu buƙatar kuɗi amma haka mahaifin murja haka ya aje masu maƙudan kuɗi tare da barin asibitin.

Idanun Hajiya Murja na ga ƙofa ganin ko Hibba zata shigo amma shuru, rashin shigowar ta ba karamin daɗi yayima Hajiya Murja ba.

Hibba kuwa duk asibitin ta isheta domin kwata_kwata basu rayuwa cikin asibiti yanzuma ƙarfin hali ne kawai ya sanya ta zama.

Ganin duhun dare ya fara yasa Hibba fitowa harabar asibitin zata fice, karo suka ci da wata mata mai tsohon ciki da aka kawo lokacin, suna haɗa ido da hibba mai naƙudar nan tayo kanta tamkar yunwataccen zaki.

Shake Hibba tayi tana kururuwar "ku riƙeta kada ku bari tabar asibitin nan, ku samu igiyoyi ku ɗaure ta nace ku rike ta kada ta tsere."
A gigice mutane suka banbare matar mai tsohon ciki suna yima Hibba sannu.

Tamkar mahaukaciya haka matar nan tarika ihu tana su sake ta sai ta kashe Hibba, mutane da dama sun tausayama matar nan mai naƙuda domin sun dauki wanan abu daya faru a matsayin zafin nakuda.

Da kyar likitocin suka shige da wannan mata labour room, Hibba kuwa Murmushin gefen baki tayi tare da kallon gabas da yamma sai da ta lura hankalin mutane bai kanta kafin fara magana.
"Karya kike ba zaki tona mani asiri ba, duk wanda yayi ƙoƙarin shiga gona ta kauda shi nike daga hanya ta."
Tana gama fadar haka ta rufe idonta tare da karanto wasu ɗalasimai kamar ƙiftawar ido wutar Nepar asibitin ta dauke wani matsanancin duhu ya mamaye asibitin...

---

...Bayan likitan ya gama duba lafiyar shi cewa yayi kowa ya bashi wuri domin ana buƙatar ya ƙara hutawa kafin ya tashi, ɗakin suka jawo mashi tare da fatan samun lafiya.

Yau Fadila da Lubna sune da haɗuwa wuri ɗaya amma Fadila babu alamun bakar magana bare habaici sai nan nan take da Lubna.

Wannan abu ba karamin ƙona ma Hajiya mariya rai yayi ba dan haka jan Fadila tayi suka shige ɗaki.

"Mi nike gani haka, yau kece da wani shisshige ma Lubna anya kuwa kanki ɗaya."?
Hajiya Mariya ta fada a fusace

"Ni fa Hajiya ki kyale ni ki daina shiga Gonar Lubna wallahi kuwa, shin Hajiya tunda kike kin taba yima awaki Brush."
Fadila ta tambaye mahaifiyar tata.

"Ke bani son zance banza, ke tunda kike kin taba ganin inda aka yima dabba wankin baki."?

"To Hajiya ki kiyayi ranar da za'a baje maki garken Awaki ace ki wanke masu baki, musamman uwar garke duk ta fisu baƙin hali,ni bala'in da nagani ba kaɗan bane, nifa kada ma ki jaza mani wani bala'in kinga tafiya ta."
Fadila ta karasa maganar tana barin ɗakin mahaifiyar tata da sauri.

"Awaki da Uwar Garke kuma, to ko dai ita ma Fadilan ta fara shaye_shaye ne."
Hajiya Mariya ta tambayi kanta.

Lubna kuwa yinin yau banda kuka babu abinda take, ita dai tasan tun sa'in da Al'ameen ya zuba mata Coffee akai bata sake sanin mike faruwa ba sai dai ganin ta tayi bisa gado kwance" ya Allah kasa bani bace sanadin fadawar shi wannan yana yi."
Kaf abinda Lubna keyi a kan idon Hajiya Salima dan haka wani irin tausayin ta ne taji ya kara shigar ta ba kaɗan ba.

Kiran da ake ta yima wayar Al'ameen ce ya sanya Hajiya Salima dauka tare da Sallama, ashe ma sirikar ta ce wato Leemcy jin Al'ameen ba lafiya nan Leemcy tace gata nan zuwa, Feedow ta kira domin ta raka ta, basu ma tsaya ɗaukar mota ba Napep suka hau domin dama suna da aikin da sabon bokan su ya basu suyi a cikin gidan su Al'ameen sai gashi kuma anyi a sa'a zasu samu damar shiga gidan...

---

...Mahaifin Lubna kuwa jiki yayi sauki domin suna sanya ran sallama anan kusa.

Gaje kuwa baƙin hali sai ma gaba da yayi domin babban baƙin cikin ta bai wuce gidan hutu da Mahaifin Lubna ya bada auren ta ba.

Alƙawari ne ta ɗauka indai tana raye baza'a ɗauran auren nan ba Sai tayi yadda tayi aka fasa auren nan.

Kulu kuwa wannan zaman asibiti ribane a gare ta yawon banza sai abinda yayi gaba, da Malam Sule ya tambayi inda take Gaje zata hau masifa tana fadar "ita ya sa mata ido bayan waccan

ɗayar ita tana can yawon banzar ta.

Haka yake kyaleta domin indai baƙin ciki ne ba yau Gaje ta fara kumsa mashi shi ba ya hadiyi gubarta babu iyaka.

Shiyasa yanzu yabi shawarar likita ya dena biye mata kodan lafiyar shi, yana so ya rayu yaga ɗiyan Lubna yaga yadda Lubna zata samu farin ciki a gidan ta.

Kulu kuwa kullum addu'ar shi ita ce kada Mahaifiyar ta talalata mashi tarbiyyar ta, Bikin Lubna kuwa bai da wasu dangi a ƙasar nan domin a salinsu A sudan suke sakamakom wata Annuba da ta barke a garin mutane da dama suka rasa rayukan su ta sanadin haka suka rasa danginsu suka dawo nageria da zama, dan haka bikin Lubna babu wani danginshi kona Gaje sai dai yayan Gaje guda ɗaya daya rage mata...

---

...Tun cikin Napep ɗin suke shirya yadda zasu gabatar da aikin su ita da Feedow.

A kofar gidan aka safke su, nan suka fara buga ƙofa mai gadi ya bude ganin kalar shigar dake jikin su nan fa mai gadi ya hana su shiya yana fadar "sunyi kuskure ba nan gidan suke nema ba."

Ganin wannan renin wayo da mai gadi ke masu yasa Leemcy fara ɗura mashi ashariya tana niyyar fizgoshi.

Hayaniyar da Hajiya taji anatayi taƙi karewa ce ta sanya ta fitowa dan ganin abinda ke faruwa, kallo ɗaya Hajiya Salima tayi ma Leemcy ta gano ita ce wadda ta taba iskewa a ɗakin Al'ameen.

Dogon numfashi taja tare da Umartar mai gadi daya barsu su shigo, babu kunya haka Leemcy ta shugo gidan tana hura hanci ko Hajiya Salima bata gaida ba.

Falo aka zaunar dasu tare da kawo masu abun tabawa, wurga ido kawai  Leemcy keyi taga inda Al'ameen zai bullo, basu wuri Hajiya Salima tayi dan su sarara.

"Ke nifa banzo gidan nan dan waccan matar ta ajemu faloba, tunda nasan ɗakin Al'amen kinga ni nayi gaba."

Leemcy ta karasa maganar tare da nufar part ɗin Al'ameen.

Ba karamin jin daɗin ganinta yayi ba dan koba komi yanzu aikin da akeyi kanshi ya fara tasiri, tamkar wata muharramar shi haka ta haye gado tare da jero mashi sannu.

Dawowar da Hajiya Salima zatayi nan ta nemi Leemcy ta rasa, Feedow ke ce mata ai ta shiga dakin Al'ameen ta duba shi.

Cike da mamakin rashin ɗa'a irin na Leemcy Hajiya tayi zaman yan bori saman kujerar falon.
"Ba irinta naso ta Zama sirikata ba amma Ubangiji haka ya tsara Allah ka bani ikon cinye wannan jarabawa."

Kaf abubuwan da ke faru akan idanun Hajiya Mariya dake lafe ta kafar labule tana kallon su.
"Dani kike maganar aikeda kwanciyar hankali a cikin gidan nan har abada, a kai na zaki gane auren mijin wata babu riba."
Ta karasa maganar tare da sakin labulen.

Lubna kuwa wani abu taji ya tokare mata zuciya da ƙyar take hade yawu, tun bayan zuwan Leemcy.

Leemcy kuwa ranar ita ce har marece tana ɗakin Al'ameen taki tafiya sai wannan iyayi take hatta abinci ranar ita ta amso wurin Hajiya Salima taba Al'ameen.

Marece liƙis tayi sallama da yan gidan suka fice.

Basu suka samu Napep ba sai da suka yi tafiya mai nisa da gisan su Al'ameen, Feedow tasha zagi wurin Leemcy domin ita ta hana a taho da mota wata napep ce ta tsaya gabansu ba tare da sun tsai da ba.

Shigewa suka yi tare da fadar inda zai aje su.

Leemcy ce ta kalli Feedow.
"Kin dai yi aiki kamar yadda aka buƙata ko."
Leemcy ta jefama Feedow tambayar.

"Aiki kuma ai sai dai wani na gaba Amma Lubna sai dai wata ba ita ba, yanzu haka nasan jakar ta tsallaka."
Kecewa suka yi da dariya tare da tafawa.

"Farida da Halimatu! Nace anya kuwa kun barbaɗama Lubna maganin nan yadda ya kamata, nifa gani nike kafa ta koda na tsallake kofar ban taka ba, amma ku duba mani ku gani kafata kona taka bangani ba."
Suka ji mai tuƙin Napep ɗin ya fada tare da sakin akalar Napep ɗin ya zuro masu kafar shi mai dauke da kofato....

*MEEN@RT...✍🏻*
08133562798
[8/1, 10:12 AM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE 1️⃣9️⃣2️⃣0️⃣*
Mun saba number a page ɗin da ya gabata zamusa page 17_18 sai mukayi kuskure muka sa page 18_19.

*WANNAN PAGE ƊIN NAKU NE YAN GROUP ƊINA NA RUWA BIYU 🥳🥳 KUYI YADDA KUKE SO DA PAGE ƊIN NAN*

...Tsananin duhun daya mamaye asibitin ne ya rikitar da likitocin ba shiri suka furfito tare da
```

nufar inda tushen Nepar Asibitin yake, Mahaifiyar Rukayya kuwa matar da ta shaƙe Hibba kuwa, lokaci ɗaya ta afka ɗakin da ɗiyar ta take tare da ruƙota tana mai fara tofaa mata addu'o'in.

"Mama miya sa kuka kwace ni, miya sa kuka bar matar nan ta tafi."
Cewar Ruƙayya da azabar naƙuda ke ci.

"Rukayya yanzu ba lokacin surutu bane, kiyi addu'a domin nima sam ban yarda da ita ba, ina kalonta jikina ya bani ba ta kirki bace da kyarma in ba ruwa biyu bace, Rukayya kiyi addu'a nima ina nan ina tofa maki insha Allah babu abinda zai Same ki sai alkhairi

Mahaifiyar Ruƙayya mace ce mai matuƙar addini, a ƙa'idar ta sam bata yarda ɗaya daga cikin yaranta in yana naƙuda ba a ce wai wani makwafci ko wani bare ya kai mata su asibiti, ita ke kai duk wani yaro nata domin tasan haɗurran da ake fuskanta lokutan naƙuda, a binciken da nayi kashi goma cikin matan dake mutuwa lokacin naƙuda wasu ba mutuwar Allah da Annabi bace, lokacin na ƙuda lokacine da al'ajanu yan kungiyar shan jini da kuma wani tsohon suhiri da aka taba yi maka duk zasu iya samun ka amma komi sai Allah ya amince.

Shiyasa Mahaifiyar Ruƙayya bata yarda a haɗa yaranta da wani ba a lokacin nakuda domin wani ɗan rakiyar ko addu'a bazai umurceka kayi ba bare kuma kasa ran shi zai yi maka.

Addu'ar da mahaifiyar ta ke tofa mata ce ta sanya ta jin sanyi cikin ranta a hankali sauki ya fara samuwa.

A ƙalla matan dake cikin ɗakin haihuwar sun tasar ma Mutum hudu daga cikin su biyu ne kaɗai ake yima addu'a sauran kuwa duk yan rakiyar su sannu kawai suke jero masu.

Wani irin kukan maguna ne mara daɗin sauti ya kacame a cikin labour Room ɗin, ji ɗaya zaka yima kukan indai kana da hankali ka tabbatar ba kukan lafiya bane domin wani irin kuka ne da in sunayi har cikin zuciyar ka tsikar jikin ka kuwa duk sai ta tashi.

Jin wannan kuka yasa Mahaifiyar Ruƙayya riƙe ɗiyar ta gam tare da ci gaba da kwararo mata addu'o'in.

Tun Kukan magunan nayi a hankali harta kai kuka ya kece sosai in wannan tayi sai wannan ta amsa gashi da alama magunan suna cikin labour Room ɗin amma an rasa ina suke domin babu

wanda ya gansu.

Babu zato babu tsammani Jibgegiyar Mage baƙa wuluk ta bayyana a gefen Ruƙayya.

Da yake Mahaifiyar Ruƙayya tun bayan ɗaukewar Nepa ta kunna torchlight ɗin wayarta Shine yasa ma ta ganta, kallo ɗaya maman Rukayya tayi mata taji gabanta ya faɗi, saurin kai hannu tayi bakin ta ɗauke da sunan Allah da nufin bige magen sai dai kafin hannunta ya kai ga magen tuni magen ta ɓace ɓat.

Lokaci ɗaya Marar Ruƙayya tayi wata irin murɗawa ba shiri ta ƙara ruƙo mahaifiyar ta tare da yin addu'a kamar yadda Mamanta ta Umurceta, dube_duben gefen su Mahaifiyar Ruƙayya ta hauyi ko zata ga inda magen ta makale amma wayam sai ma kukan magunan dake ƙara cika ɗakin.

Ganin magen da tayi gaf da kan ɗiyar ta bata san lokacin da ta kai mata wani buguba, sai ga magen ta faɗo daga saman gadon tana mai aikama Mahaifiyar Rukayya da mugun kallo , domin kuwa tun zuwan farko tayi ƙoƙarin aikawatar da aikin ta sai dai kash! Tana nufar su taji wani tiriri na dukan jikinta tamkar zai ƙonata, sai gashi kuma yanzu an wullota daga saman hadon har an ji mata ciwo a hannu, yanzu kam ta shaida Ba zata iya kashe wannan mata ba abu ɗaya ya rage mata shine ta sanya matar manta abunda ya faru ɗazu.

Kafin mahaifiyar Ruƙayya ta ankara sai gani tayi magen ta daka wani wawan tsalle ta haye bisa kan Ruƙayya, mahaifiyar ruƙayya kuwa ganin wannan al'amari bata san lokacin da ta wawuro nagen ta bugata da bango ba, zafin buguwar da magen tayi ne yasa ta sakin wani kuka da murya irinta mace, kowa cikin ɗakin ganin al'amarin dake faruwa shuru yayi jikina kyarma ido ya rena fata, zafin bugun da aka yima magen ta jima a yashe tana kuka kafin ta mike rai a matuƙar bace duk da cewa tasan tayi nasarar mantar da Ruƙayya abinda ya faru, kallon masu naƙudar ta farayi ɗaya bayan ɗaya, wata yarinya mai haihuwar fari da kakarta ta kawo idon magen ya sauka kanta, baki magen ta buɗe tare da zabgawa da mugun gudu ta dira saman wannan yarinya da kakarta ta kawota haihuwa, kasancewar mutanen karkara ne ga kuma rashin ilimin addini da tsohuwar ke fama dashi domin tun zuwan su asibitin babu wata kalma daya ta addu'a data yima jikar ta ko kuma ta umurci jikar Tayi

Haka magen nan ta shafi cikin matar tare da dirowa daga saman gadon ta bace bat!

Yarinyar da magen ta hau kuwa wata mahaukaciyar ƙara ta saki tare da fara fizge_fizge, lokaci ɗaya ta fara aman jini ta baka da hanci, kafin kace mi ta kakkafe idanunta sunyi sama, ganin jikarta ta dena motsi da alamu na rai yayi halin shi yasa Kakar sakin wata kururuwa tana mai ambatar sunan jikar ta.

Duk matan dake cikin ɗakin sun shiga tashin hankali mara misali ganin wannan masifa data afku lokaci ɗaya...

Hajiya Murja Kuwa wutar asibitin Na daujewa jikinta ya hau bari, domin tasan kadan daga cikin aikin Hibba ne.

Fitilar wayar ta mahaifin Hibba ya kunna tare da aje ta kusa dasu cike da mamakin ɗaukewar Nepar

Meow!
Suka ji kukan mage cikin ɗakin, kallon kallo aka fara tsakanin su biyun.

"Kin ji abinda kunne na ya jiyo mani kuwa."?
Cewar Mahaifin Hibba

"Cike da tsoro nike, yanzu haka ko kwakkwaran motsi bani iya yi."
Hajiya Murja ta ƙarasa maganar tare da fara kalle_kalken in da zata ga magen ta ɓullo.

"Kufa mata tsoron ku yayi yawa, daga jin kukan mage sai ki wani tsorata, bari ni inje in duba."
Ya karasa maganar tare da kunna fitilar wayar shi zai fice.

Saurin ruƙoshi tayi
"Aa ka daka ta kada ka tafi ka barni."
Ta karasa maganar cikin tsoro.

Bai saurare ta ba haka ya kunna kai yayi gaba abinshi, kaf kukan da yake ji yanzu ya fara ragewa a hankali, da gudu yaji an gitta ta bayan shi, da sauri ya waigo dan gane ma idonshi miye, amma wayam baiga kowa ba.

Juyowa yayi da nufin komawa ɗakin abinda idanunshi suka gane mashi ne yayi sanadin hadiye wani yawun wahala ji kake Ƙutt!

Ba komi bane Mahaifin Hibba ya gani ba face wani mutum sak mai irin suffarshi daya bayyana a gabanshi.

Jiki na kyarma Mahaifin Hibba ya ɗaga hannu tare da nunashi.
"Kai waye."?
Mahaifin Hibba ya faɗa murya na kyarma.

"Ni ne mahaifin Hibba kai kuma waye."?
Jabun mahaifin Hibba ya faɗa.

A guje Mahaifin Hibba ya tattare babbar riga tare da kwaɗawa da gudu.

Jabun Mahaifin Hibba kuwa kecewa yayi da dariya tare da zura kafarshi tayi taku daya sai gashi ya iske mahaifin Hibba n ainahi.

"Ba zaka guje mani ba duk inda kaje sai na bika."
Jabun Mahaifin Hibba ya faɗa.

Mahaifin Hibba na ainahi kuwa idone ya rena fata.
"No condition is permanent, or no condition is permanent."
Mahaifin Hibba na ainahi ya shiga maimaita wannan kalma tamkar ya samu wata addu'a ga jiki ya jiƙe da gumin wahala.

😂💔
Baka bugu bane Alaji

Barkewa da dariya Jabun shi yayi tare da bacewa bat! Wata nannauyar ajiyar zuciya Mahaifin Hibba ya Sauke, ji yayi tamkar ana janye mashi babbar riga dan haka a firgice ya waigo, kan kwarangon ne ya gani ya cije mashi babbar riga, a firgice ya sake mikewa tare da furta, "Or my God!."
Ya karasa  maganar tare da zabgawa da gudu yana waigen kan kwarangwal ɗin dake biye dashi.

Gudu yake amma kwarangwal ɗin bai dena binshi a guje ba, ganin yana gaf da shigewa ɗakin da Mahaifiyar Hibba ke ciki ya sashi kara ƙaimin gudu, juyawar da zai yi jarirai ya hango suma sun Take mashi bayaa guje, yana gaf da shigewa ɗakin ƙofar ta rufe kanta ji kake Garam!...

---

...''Mun bani mun shiga tara, Leemcy kina ganin abinda idanuna ke gane mani kuwa."
Feedow ta karasa magana jiki na ɓari.

Kecewa da dariya mai Tuƙin Napep ɗin yayi kamannin shi sun sauya kanshi ya koma sak kan doki ga ƙafafun shi sun koma kofato.

Sai da yayi dariyar shi mai isar shi kafin ya turbene mummunar fuskarshi.
"Kaf duniya ina tunanin babu wanda ya fini ƙeta da kuma mugun ta, ko kuna gardama ne."?
Ya karasa maganar tare da zare masu ido.

"Wane mu ƙananun shegu wallahi Baba doki ka fimu komi kai ne Oga, karya muke dan Ubanmu."
Leemcy ta karasa maganar a matuƙar tsora ce.

Kecewa yayi da dariyar da ta haddasa ma napep ɗin girgiza tamkar zata kife.
"Cikin ku wace ce ta bada maganin."?
Ya tambaya yana haɗe rai.

"Wannan ce."
Leemcy ta nuna Feedow.

"Ni zaki zalumta ashe dama muguwar tare muke, Allah ya debe maki albarka gantallaiyar banza, bani bake."
Feedow ta karashe maganar tana share hawaye.

Marin da aka shiga ɗauke su dashi ne ya gaddasa masu fara kururuwa suna neman ɗauki, an ɗauki lokaci mai tsayi kafin a dakata, fuskar nan tasu kuwa tsabar azaba ta fara kumburi.

"Bani yafiya bani ragi bani ragowa in ka shiga gonata dole ne in ɗauki mataki a kanku, kunyi kuskure kuma yau zaku gane shayi ruwa ne."
Nuna su yayi da hannu take aka watsasu waje jikin su ya bugu da ƙururruban dake wurin.

Wasu halittu ne masu kama da Birai suka bayyana sunfi su goma jikin su wani gashi ne tamkar an yafara masu bargo.

Halittun mubayi'a suka yi ga Shugaban su dake tsaye gaban su Leemcy.

Wata hatsabibiya ce da duk ta fisu gashi ga munin ta ya ninka nasu sau goma ta fara magana.
"Shugaba Soyawa za'ai go gasawa ko kuma tsire."?
Ta karasa maganar tana lasar baki.

"Wannan bana ci bane, zamu koya masu hankali ne domin su gane tsakanin jinnu da bil'adam a kwai banbanci, ke makirar da kika zuba maganin da hannun da kika yi aikin dashi zaki ƙirga gashin dake jikin Uwar garke koda wasa kika bata ƙirga jikin ki ne zai gaya maki."
Kafin ya rufe baki tuni Uwar garke ta bayyana tana washe baki

A gigice Feedow ta fara kuka tana ƙirga adadin gashin dake jikin uwar garke, da zarar ta aza hannunta fa fara ƙirga sai Uwar garke tayi girgiza gashin jikinta ya kara yawa ƙirga ta bace,
"Tayi kuskure a bugeta."

Shine abinsa Uwar Garke ke faɗa.

Nan zasu rufe Feedow da duka ta ko ina haka zata mike taci gaba da ƙirga.

Ganin irin azabar da ake gana ma Feedow Leemcy Kuka ta fara domin tasan ita azabarta ta musammance.

"Mai gayya mai aiki, shugabar minahikai ta duniya yau kashinki ya bushe, hukuncin ki yafi na kowa yawa."
Yana gama maganar ya Umurci sauran Aljanun da su shige Napep sai da ya rage babu kowa sun tsaunu saman napep wasu bisan wasu sai Uwar garke da Feedow dake ta faman ƙirga.

"Zaki rika tura mu har mu ƙarasa gidan ku idan kika sake tsautsayi yasa kikayi mana ba dai_dai ba tabbas jikin ki zai gaya maki fatan kin gane.

Babu musu Leemcy ta miƙe tare da ɗaura gyale a ƙugu domin tasan yau kashin ta ya bushe, ita da hatta driven yi mata ake yau ita ce da turin napep sauƙin ta daya dare ya fara mutane ba zasu ganta ba.

"Shugana nima zabi biku, amma kuma ga wannan aikin  da aka ba Wannan wahalalliyar."

Dariya shugaban yayi tare da furta.
"Ke hatsabibiya ce zaki iya rabuwa biyu a barma Feedow daya ɗaya kuma ta shigo Napep mu wuce.

Rufe bakinshi keda wuya Uwar garke ta rikiɗa ta rabu biyu tare da shigewa Napep.

Turi Leemcy keyi iyakar ƙarfinta amma Napep ɗin ko mutsi ta kasa yi, ƙarfinta ta haɗa wuri ɗaya tare da tura napep ɗin, ji kake ɓur! Leemcy ta saki wata tusar wahala, turi take tana kuka domin kaf karfin ta yau ta tattara shi ta haɗe wuri ɗaya, kasancewar dare yayi haka ta rika ratsa unguwanni cike da azabar da take ji ajikinta, ana cikin tafiya Uwar Garke zata fasa ihu ace miye tace kanta ya faɗi sai yanzu ta lura, haka zasu Umurci  Leemcy taje daukowa kai yaƙi ɗaukuwa data mika hannu zata ɗauka zai bude baki ya gartsa mata cizo haka take ihu kuma dole taje ta dauko shi.

Azabar duniya ranar Leemcy ta shata ba kadan ba, kafin su isa gida kan Uwar Garke ya fadi yafi a kirga, tun hawayen azaba na fita a idon Leemcy har suka kare.

Isarsu ƙofar gida nan Leemcy ta zube tana maida Numfashin wahala.

Hada baki suka yi a tare suka furta.
"Sai kuma haduwa ta biyu."
Suna gama maganar wata Guguwa ta kwashe su tayi sama dasu.

Bugun get ɗin take tamkar zata karya shi security ɗin ne ya buɗe a fusace da nufin balbale mai bugun ƙofar da masifa, ganin Leemcy ce dole yaja da baya cike da mamakin ganin yadda ta koma Hajaran_majaran.

Dura mashi ashariya ta hau yi cike da masifa ta bangaje shi tana kuka, tana shiga ɗakin ta fadawa tayi kan gado tare da sakin wani kukan na wahala.

Al'ameen kuwa haushin kanshi ya rika ji wai yana handsome guy amma ya kira waccan jakar da Aunty.
"Mtsww!."
Ya ja dogon tsoki.

"Ko zani mutu sai ta gane kurenta radda duk na riƙeta."
Ya karasa maganar tare da gyara kwanciya.

Hajiya Salima kuwa tun bayan tafiyar Leemcy a gidan hankalinta ya kasa kwaciya tunani mabanbanta ne suka addabi zuciyar ta ganin irin matar da tilon ɗan ta ke shirin aure, ganin dare ya fara ne yasa ta nufar dakin ta.

Gidan yayi tsit baka jin motsin komi sai karar A.C da kuma fankoki dake aiki

Hajiya Mariya kuwa bacci yayi daɗi sai juyi ake saman gado, cikin bacci taji kamar wani abu na lasar mata ƙafa, a gigice ta buɗe ido cike da tashin hankali.

Kai babu gangar jiki ya dage sai lasar kafarta yake, ɗago kan da zata yi nan tayi arba da abinda ya sanya numfashin ta tsayawa na wucin gaɗi...

*MEEN@RT...✍🏻*

[8/2, 5:33 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE 2️⃣1️⃣ 2️⃣2️⃣*
...Wagegen bakinta ta wangale tare da kallon Hajiya Mariya da tayi mutuwar zaune lokaci ɗaya.

"Ba zaki zube ki kwashi gaisuwa ba sai na wargaje maki wannan tulelen tumbin naki."?
Uwar garke ta fada.

Hajiya Murja kuwa tsabar rudewa jiki ko ina ciri yake tama rasa shin kan dake saman gadon ta zata gaida ko kuma gangar jikin dake tsaye gabanta cikin mummunar suffa.

"Tuba nike ki gafar ceni, uwar Aljanu nace kan zani gaida ko kuna gangar jikin."?
Hajiya Mariya ta fada jiki na kyarma.

Kecewa da dariya Uwar Garke tayi tare da ɗauko kanta dake bisa hadon Hajiya Murja ta mannashi da wuyanta sai ga kai ya zauna  daram.

"Nafi karfin uwar Aljanu ni hatsabibiya ce Uwar hatsabibai ni ce Uwar garke mai taƙama da mugunta da kuma baƙin hali."

"Ɗauko maganin da kika boye."
Uwar Garke ta fada kanta na juyewa gefe.
```

A firgice Hajiya Mariya ta zaro ido cike da zallar fargaba.

"Zaki dauko maganin ko sai jikin ki ya gaya maki."?
Uwar garke ta fada tare da nuna Mariya da rubabben hannunta.

A gigice Mariya ta buɗe bed side sai ga wani magani ƙulle cikin leda ta fiddo, dariyar data haddasa ma dakin girgiza Uwar garke ta fara.

"Kin ɗauka ke kaɗai kika iya mugunta, kin je gidan bokan ki kin amso maganin zaki zuba ma Al'ameen cikin abinci kamar yadda bokanki ya umurce ki."
Dakatawa da maganar Uwar garke tayi tare da kallom Mariya.

Mariya kuwa tsilli_tsilli da ido tayi jiki na rawar mazari.
"Wannan magani zaki zuba shine a cikin abincin Al'ameen da zarar yaci zai balle da zawo babu ji babu gani zawo bazai tsaya ba har sai ruwan jikin Al'ameen ya ƙare da haka za'aita nema mashi magani har har ruwan jikin shi ya ƙare ya mutu ba tare da an samu maganin cutar shi ba, kinga koda ya mutu ba za'a zarge ki ba, ko ba haka akayi ba."
Uwar garke ta ƙarasa maganar tare da daka ma Hajiya Murja tsawa.

Kuka Hajiya Murja ta fashe dashi.
"Na tuba Uwar Garke kike ko Uwar akoyoyi ki ceci rayuwata ki yafe mani."

Wani wawan bugu da ya haddasa masa bakin Hajiya Mariya fashewa uwar garke ta sauke mata.
"Uwar Garke nike, ba Uwar Akuyoyi ba dan haka ki iya bakin ki ,maza amshi maganin nan ki shanye yanzu."
Uwar Garke ta karasa maganar tare da miƙama Hajiya Murja maganin.

"Ni jikanyar Dumbe da Tsayyaba na jangwalo ma kaina bala'i, Uwar Garke ki gafarce ni kada ki jaza mani zawon da ban shirya ba..."
Marin da aka ɗauke ta dashi ne yayi sanadin ɗaukewar ganinta na wucin gadi.

"Zaki sha ko sai na kira yan korena sun banƙare ki mun ɗura maki shi "

Ba shiri ta amshi maganin tare da shanyeshi tas! Dariyar mugunta Uwar Garke ta Babbake da ita.
"Keda zawo mutu ka raba shine zai zama ajalin ki."

Shikenan tata tariga da ta ƙare.
"Kin taba yima Aljani tausa."?
Uwar Garke ta tambaya.

"Na rantse da Allah billahil azeem ban taba yima koda bil'adam bane bare kuma Aljani, ki taimake ni ki bar mani ɗakina wallahi warin ki ya shika mani ɗaki."
Wasu mahaukatan naruka aka shiga dauke Mariya da su sai da ta fita hayyacin ta.

"Ina daga tsaye nike so kiyi mani tausa , in kika bari jikina ya bantake ko wata gaba ta balle jikinki ne zai gaya maki, zani sa guntu yayi maki kisan mummkuƙe."

"Wallahi zaniyi ranki shi daɗe mai daraja uwar Garke."

Kecewa da dariya Uwar Garke tayi tare da nuni da hannunta sai ga wani mulmulellen baƙin Aljani ya bayyana riƙe da wani ƙaton kulki da yayi biyun kanshi.

"Gafarta Uwar Mu Uwar Garke mi kike da bukata yanzu in aiwatar."
Baƙin Aljanin ya tambaya.

"Tausa zata yi mani muddun kaga ta ciro wani sashe daga jikina kayi mata Luguden Kulki."

"An gama Uwar mu."
Aljanin ya faɗa

A guje Hajiya Mariya ta zabgo da gudu tare da fara yima Uwar Garke tausa, daga taba hannu sai ga hannu ya balle ya biyo Hajiya Mariya.

Guntu kuwa cigaba da ɗauke Mariya yayi da kulkin hannunshi yana luguden bugu ta ko ina ihu kawai Mariya ke yi jin yadda ake mata Luguden Kulki.

Wato Ranar taga tashin hankalin da bata taba shigar irin shi ba jikin ta sai da ya kasance ayi mata ligif ta daku ba kaɗan ba.

Ana gama bugun ta zata ci gaba da tausai sai dai taga naman jikin Uwar garke ya biyu hannunta

Tun tana kurma ihu koda za'ayi sa'a wani ya jiyota amma a banza domin shuru babu wanda ke jin abinda ke faruwa da ita

Ɗan Guntu ya mata luguden kulki tamkar zata sheƙa, cikin ta ne yayi wata murɗawa lokaci ɗaya wani zawo ya balle tamkar an buɗe fanfo.

Kecewa da dariya Su Uwar Garke suka yi tare da bacewa tamkar basu taba wanzuwa a cikin ɗakin ba.

A guje Hajiya Mariya tayi Toilet amma kafin ya karasa harya fara zuba ra6a6a.

Kafin gari ya waye Hajiya Mariya ta hada wani gulbil zawayi cikin ɗakin ta yayi kaca_kaca duk inda ka duba zawo ne ra6a6a.

Wari ne ya bugar ma Abban Al'ameen hanci tun kafin ya karasa cikin ɗakin, daurewa dai yayi cike da jarumta ya karasa shigewa ɗakin.

Toshe hancinshi yayi ganin ɗakin ya hade da zawo ra6a6a tamkar wani Kwatamin ga kuma Hajiya mariya can gefe tana nishi a galabai ce.

"Subhanallahi Mariya miya sameki haka ko wani abu kika ci wanda ya bata maki ciki."?

"Alhaji ka kira mani fadila tazo ta gyara ni."

Da sauri ya tado Fadila de kwance tana bacci, ɗakin ya bar masu tare da dokama Family Doctor kira.

Hanci a toshe Fadila ke aikama da mahaifiyar ta kallo mai nuna tuhuma.

"Uwaki kika saki le6e kina kallo! Kizo ki kai ni Toilet ki gyara mani jikina."
Hajiya Mariya ta ƙarasa maganar a fusace.

"Wa! Ni zani tabaki Mama kin gama bare wannan uban zawo sannan kice in tabaki baki so gaskiya ba, wai dan Allah mi kikaci ma kike bara zawo kamar sabuwar kura."

"Ubanki daya fita yanzu shina baɗama yaji na cinye, Fadila ni zaki fallasa ki bari cikin zawo har sai waccan baƙar dagar tazo taga halin da nike ciki taji daɗin fallasani."?

"Dole ce tasa ni tsayawa cikin ɗakin nan, kin ga Ni na tafi in kira su Inna mai aiki suzo su gyaraki ammani haram in taba zawo."
Tana karasa maganar ta fice da gudu_gudu.

Babu yadda ta iya haka su Inna mai aiki suka kwasheta suka nufi toilet suma kansu gudun masifar Hajiya Mariya yasa suka daure basu toshe hanci ba.

Ɗakin suka gyara tare da feshe shi da kayan Qamshi itama suka gyarata.
"Duk minahikar da ta sake naji ta tsegumta ma Salima halinda nike ciki a bakin aikin ta."
Ta karasa maganar tare da kafe su da ido.

"Wane mu hajiya ba za'aji wannan a bakin mu ba."
Suka faɗa kai a kasa cike da tsoro.

"Ku bace mani da gani."
Ta faɗa a tsawa ce.

Sumi_sumi kai a kasa suka fice, wata doguwar ajiyar zuciya ta sauke cike da fargabar abinda zai faru, ga jikin ta dai daya sha luguden Kulki har yanzu azaba yake bata ga kuma zawo daya balle ba ji babu gani.

A guje ta nufi Toilet jin wani zawon zai zubo, a kalla kafin likitan ya karaso tayi zawo yafi shida, duk wasu bincike da zaiyi yayi amma shuru baiga komi ba, balle ayi tunanin wani abu ya haddasa mata zawon.

Cike da mamakin wannan al'amari ya rubuta mata magani tare da kama gabanshi, Hajiya Salima kuwa ta tausayama Murja ganin halin da take ciki...

---

...Ganin ƙofar ta rufe kanta yasa Alhaji jan wani wawan birki tare da juyawa bayan shi.

Jariran ya hango biye dashi bakunan su na zubda jini, faratan su zaƙo_zaƙo.

"Ki buɗe Nace, Murja wai kina ina ko sai sun halaka ni zaki farka daga baccin asara da kike."
Abban Hibba ya karasa maganar tare da bugun ƙofar tamkar zai karya ta.

Murja da tsoro ya gama cikama ciki da sanda ta taho tare da buɗe ƙofar, sai ga Abban Hibba taɓar yayi kundin bala kafin yayi ƙoƙarin tashi babbar rigar dake jikin shi ta nannaɗe shi sai gashi a kasa yana tanbulan, a gigice hajiya Murja ta rUfe kofa dan taji Abbab Hibba yana gasu

nan.

Bata bi ta kanshi ba a guje ta shige karƙashin gadon  jiki na ciri, da dai ya gama mulmula a kasa ya samu ya cire babbar rigar shima karƙashin gadon ya nufa.

"Hajiya bani ƙurya, nace ki bani ƙuryar nan."
Ya fada yana ƙoƙarin shigewa ƙuryar gadon.

Wutar Ɗakin ce ta dawo dama ta asibitin baki ɗaya haske ya gauraye ko ina.

Ganin haske ya dawo nan hankalinsu ya fara kwanciya amma an rasa wanda zai fara fitowa daga kasan gadon.

"Hajiya ɗan leƙa ki gani shin sune suka kunna wutar ko kuma ta zahiri ce ta dawo."?
Abban Hibba ya fada yana kara lemewa.

"Kana namiji amma ni zaka tura kamar wata gantalalliya kace inje in gani, kai da kake namiji baka fita ba sai ni Murjanatu."

"Bani son wargi, nida ke waye babba ba ni ne mijin ba, aljannar ki fa na ƙarƙashin ƙafata."
Ya fada tare da turbune fuska.

"Ko ba Aljanna ba, in kaso ka take kafar ka amma babu inda zani fita haka kawai su kashe ni."

Bugun ƙofar da aka fara ne ya  ƙara firgitar dasu.

An rasa mai lekawa ya buɗe, "ku buɗe mune."
Suka ji malaman asibitin sun faɗa.

Jin lallai sune nan fa Alhaji yayi karfin halin fitowa daga karƙashin gadon yana zazzare idanu.

Sai da ya fara leƙawa ta kafar ƙofar ya tabbatar sune kafin ya buɗe, shigowa suka yi domin duba lafiyar Murja ganin kuma tana cikin ƙoshin lafiya yasa suka yi gaba, sai kuma tashin hankalin da suka taras a Labour Room.

Gawar matar da Hibba ta kashe, sun shiga ruɗu sosai ganin irin mutuwar da matar tayi da gani ba mutuwar haka nan bace, babban baƙin cikin su shine hada ɗan dake cikinta ta mutu.

Tafiya suka yi da gawar kafin gari ya waye suba dagin ta

Asubar fari Alhaji ya nemi da a sallame su domin ya lura bazai iya zaman asibitin nan ba abubuwan Almara su halaka shi.

Wajen ƙarfe takwas na safiya aka rubuta masu sallama suna fitowa suka ci karo da  Hibba dake zaune gefe, ganin su yasa ta mike tare da tarbarsu tana mai sakar ma Mahaifiyar ta murmushi.

"Abba harkun fito, nima nan asibitin na kwana can ɗakin yan jinya, Umma ya jikin."
Hibba ta fada tare da kallon Mahaifiyar tata.

Cikin in'ina ta Amsa da "da sauki."

Su duka suka rankaya suka nufi Gida, sam hankalin Hajiya Murja ya gaza kwanciya ganin hada Hibba cikin motar.

Dandazon mutanen dake gaban gidan nashi ne ya sashi yin parking tare da fitowa dan gane ma idanun su mike wakana a gidan nasu.

Buda masu hanya aka riƙa yi dan su ganema idanun su mike faruwa, cincirindon mutanen har cikin gida sannu kawai suke ma hajiya murja cike da jimami.

Gawar Uwani da suka gani kwance ce tasa Hajiya Murja jin wani jiri na ɗibar ta ba shiri tayi saurin yin zaman yan bori...

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/2, 9:01 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine
```

ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE 2️⃣1️⃣ 2️⃣2️⃣*
...Wagegen bakinta ta wangale tare da kallon Hajiya Mariya da tayi mutuwar zaune lokaci ɗaya.

"Ba zaki zube ki kwashi gaisuwa ba sai na wargaje maki wannan tulelen tumbin naki."?
Uwar garke ta fada.

Hajiya Murja kuwa tsabar rudewa jiki ko ina ciri yake tama rasa shin kan dake saman gadon ta zata gaida ko kuma gangar jikin dake tsaye gabanta cikin mummunar suffa.

"Tuba nike ki gafar ceni, uwar Aljanu nace kan zani gaida ko kuna gangar jikin."?
Hajiya Mariya ta fada jiki na kyarma.

Kecewa da dariya Uwar Garke tayi tare da ɗauko kanta dake bisa hadon Hajiya Murja ta mannashi da wuyanta sai ga kai ya zauna  daram.

"Nafi karfin uwar Aljanu ni hatsabibiya ce Uwar hatsabibai ni ce Uwar garke mai taƙama da mugunta da kuma baƙin hali."

"Ɗauko maganin da kika boye."
Uwar Garke ta fada kanta na juyewa gefe.

A firgice Hajiya Mariya ta zaro ido cike da zallar fargaba.

"Zaki dauko maganin ko sai jikin ki ya gaya maki."?
Uwar garke ta fada tare da nuna Mariya da rubabben hannunta.

A gigice Mariya ta buɗe bed side sai ga wani magani ƙulle cikin leda ta fiddo, dariyar data haddasa ma dakin girgiza Uwar garke ta fara.

"Kin ɗauka ke kaɗai kika iya mugunta, kin je gidan bokan ki kin amso maganin zaki zuba ma Al'ameen cikin abinci kamar yadda bokanki ya umurce ki."
Dakatawa da maganar Uwar garke tayi tare da kallom Mariya.

Mariya kuwa tsilli_tsilli da ido tayi jiki na rawar mazari.
"Wannan magani zaki zuba shine a cikin abincin Al'ameen da zarar yaci zai balle da zawo babu ji babu gani zawo bazai tsaya ba har sai ruwan jikin Al'ameen ya ƙare da haka za'aita nema mashi magani har har ruwan jikin shi ya ƙare ya mutu ba tare da an samu maganin cutar shi ba, kinga koda ya mutu ba za'a zarge ki ba, ko ba haka akayi ba."
Uwar garke ta ƙarasa maganar tare da daka ma Hajiya Murja tsawa.

Kuka Hajiya Murja ta fashe dashi.
"Na tuba Uwar Garke kike ko Uwar akoyoyi ki ceci rayuwata ki yafe mani."

Wani wawan bugu da ya haddasa masa bakin Hajiya Mariya fashewa uwar garke ta sauke mata.
"Uwar Garke nike, ba Uwar Akuyoyi ba dan haka ki iya bakin ki ,maza amshi maganin nan ki shanye yanzu."
Uwar Garke ta karasa maganar tare da miƙama Hajiya Murja maganin.

"Ni jikanyar Dumbe da Tsayyaba na jangwalo ma kaina bala'i, Uwar Garke ki gafarce ni kada ki jaza mani zawon da ban shirya ba..."
Marin da aka ɗauke ta dashi ne yayi sanadin ɗaukewar ganinta na wucin gadi.

"Zaki sha ko sai na kira yan korena sun banƙare ki mun ɗura maki shi "

Ba shiri ta amshi maganin tare da shanyeshi tas! Dariyar mugunta Uwar Garke ta Babbake da ita.
"Keda zawo mutu ka raba shine zai zama ajalin ki."

Shikenan tata tariga da ta ƙare.
"Kin taba yima Aljani tausa."?
Uwar Garke ta tambaya.

"Na rantse da Allah billahil azeem ban taba yima koda bil'adam bane bare kuma Aljani, ki taimake ni ki bar mani ɗakina wallahi warin ki ya shika mani ɗaki."
Wasu mahaukatan naruka aka shiga dauke Mariya da su sai da ta fita hayyacin ta.

"Ina daga tsaye nike so kiyi mani tausa , in kika bari jikina ya bantake ko wata gaba ta balle jikinki ne zai gaya maki, zani sa guntu yayi maki kisan mummkuƙe."

"Wallahi zaniyi ranki shi daɗe mai daraja uwar Garke."

Kecewa da dariya Uwar Garke tayi tare da nuni da hannunta sai ga wani mulmulellen baƙin Aljani ya bayyana riƙe da wani ƙaton kulki da yayi biyun kanshi.

"Gafarta Uwar Mu Uwar Garke mi kike da bukata yanzu in aiwatar."
Baƙin Aljanin ya tambaya.

"Tausa zata yi mani muddun kaga ta ciro wani sashe daga jikina kayi mata Luguden Kulki."

"An gama Uwar mu."
Aljanin ya faɗa

A guje Hajiya Mariya ta zabgo da gudu tare da fara yima Uwar Garke tausa, daga taba hannu sai ga hannu ya balle ya biyo Hajiya Mariya.

Guntu kuwa cigaba da ɗauke Mariya yayi da kulkin hannunshi yana luguden bugu ta ko ina ihu kawai Mariya ke yi jin yadda ake mata Luguden Kulki.

Wato Ranar taga tashin hankalin da bata taba shigar irin shi ba jikin ta sai da ya kasance ayi mata ligif ta daku ba kaɗan ba.

Ana gama bugun ta zata ci gaba da tausai sai dai taga naman jikin Uwar garke ya biyu hannunta

Tun tana kurma ihu koda za'ayi sa'a wani ya jiyota amma a banza domin shuru babu wanda ke jin abinda ke faruwa da ita

Ɗan Guntu ya mata luguden kulki tamkar zata sheƙa, cikin ta ne yayi wata murɗawa lokaci ɗaya wani zawo ya balle tamkar an buɗe fanfo.

Kecewa da dariya Su Uwar Garke suka yi tare da bacewa tamkar basu taba wanzuwa a cikin ɗakin ba.

A guje Hajiya Mariya tayi Toilet amma kafin ya karasa harya fara zuba ra6a6a.

Kafin gari ya waye Hajiya Mariya ta hada wani gulbil zawayi cikin ɗakin ta yayi kaca_kaca duk inda ka duba zawo ne ra6a6a.

Wari ne ya bugar ma Abban Al'ameen hanci tun kafin ya karasa cikin ɗakin, daurewa dai yayi cike da jarumta ya karasa shigewa ɗakin.

Toshe hancinshi yayi ganin ɗakin ya hade da zawo ra6a6a tamkar wani Kwatamin ga kuma Hajiya mariya can gefe tana nishi a galabai ce.

"Subhanallahi Mariya miya sameki haka ko wani abu kika ci wanda ya bata maki ciki."?

"Alhaji ka kira mani fadila tazo ta gyara ni."

Da sauri ya tado Fadila de kwance tana bacci, ɗakin ya bar masu tare da dokama Family Doctor kira.

Hanci a toshe Fadila ke aikama da mahaifiyar ta kallo mai nuna tuhuma.

"Uwaki kika saki le6e kina kallo! Kizo ki kai ni Toilet ki gyara mani jikina."
Hajiya Mariya ta ƙarasa maganar a fusace.

"Wa! Ni zani tabaki Mama kin gama bare wannan uban zawo sannan kice in tabaki baki so gaskiya ba, wai dan Allah mi kikaci ma kike bara zawo kamar sabuwar kura."

"Ubanki daya fita yanzu shina baɗama yaji na cinye, Fadila ni zaki fallasa ki bari cikin zawo har sai waccan baƙar dagar tazo taga halin da nike ciki taji daɗin fallasani."?

"Dole ce tasa ni tsayawa cikin ɗakin nan, kin ga Ni na tafi in kira su Inna mai aiki suzo su gyaraki ammani haram in taba zawo."
Tana karasa maganar ta fice da gudu_gudu.

Babu yadda ta iya haka su Inna mai aiki suka kwasheta suka nufi toilet suma kansu gudun masifar Hajiya Mariya yasa suka daure basu toshe hanci ba.

Ɗakin suka gyara tare da feshe shi da kayan Qamshi itama suka gyarata.
"Duk minahikar da ta sake naji ta tsegumta ma Salima halinda nike ciki a bakin aikin ta."
Ta karasa maganar tare da kafe su da ido.

"Wane mu hajiya ba za'aji wannan a bakin mu ba."
Suka fada kai a kasa cike da tsoro.

"Ku bace mani da gani."
Ta faɗa a tsawa ce.

Sumi_sumi kai a kasa suka fice, wata doguwar ajiyar zuciya ta sauke cike da fargabar abinda zai faru, ga jikin ta dai daya sha luguden Kulki har yanzu azaba yake bata ga kuma zawo daya balle ba ji babu gani.

A guje ta nufi Toilet jin wani zawon zai zubo, a kalla kafin likitan ya karaso tayi zawo yafi shida, duk wasu bincike da zaiyi yayi amma shuru baiga komi ba, balle ayi tunanin wani abu ya haddasa mata zawon.

Cike da mamakin wannan al'amari ya rubuta mata magani tare da kama gabanshi, Hajiya Salima kuwa ta tausayama Murja ganin halin da take ciki...

---

...Ganin ƙofar ta rufe kanta yasa Alhaji jan wani wawan birki tare da juyawa bayan shi.

Jariran ya hango biye dashi bakunan su na zubda jini, faratan su zaƙo_zaƙo.

"Ki buɗe Nace, Murja wai kina ina ko sai sun halaka ni zaki farka daga baccin asara da kike."
Abban Hibba ya karasa maganar tare da bugun ƙofar tamkar zai karya ta.

Murja da tsoro ya gama cikama ciki da sanda ta taho tare da buɗe ƙofar, sai ga Abban Hibba taɓar yayi kundin bala kafin yayi ƙoƙarin tashi babbar rigar dake jikin shi ta nannaɗe shi sai gashi a kasa yana tanbulan, a gigice hajiya Murja ta rUfe kofa dan taji Abbab Hibba yana gasu nan.

Bata bi ta kanshi ba a guje ta shige karƙashin gadon  jiki na ciri, da dai ya gama mulmula a kasa ya samu ya cire babbar rigar shima karƙashin gadon ya nufa.

"Hajiya bani ƙurya, nace ki bani ƙuryar nan."
Ya fada yana ƙoƙarin shigewa ƙuryar gadon.

Wutar Ɗakin ce ta dawo dama ta asibitin baki ɗaya haske ya gauraye ko ina.

Ganin haske ya dawo nan hankalinsu ya fara kwanciya amma an rasa wanda zai fara fitowa daga kasan gadon.

"Hajiya ɗan leƙa ki gani shin sune suka kunna wutar ko kuma ta zahiri ce ta dawo."?
Abban Hibba ya faɗa yana kara lemewa.

"Kana namiji amma ni zaka tura kamar wata gantalalliya kace inje in gani, kai da kake namiji baka fita ba sai ni Murjanatu."

"Bani son wargi, nida ke waye babba ba ni ne mijin ba, aljannar ki fa na ƙarƙashin ƙafata."
Ya faɗa tare da turbune fuska.

"Ko ba Aljanna ba, in kaso ka take kafar ka amma babu inda zani fita haka kawai su kashe ni."

Bugun ƙofar da aka fara ne ya  ƙara firgitar dasu.

An rasa mai lekawa ya buɗe, "ku buɗe mune."
Suka ji malaman asibitin sun faɗa.

Jin lallai sune nan fa Alhaji yayi karfin halin fitowa daga karƙashin gadon yana zazzare idanu.

Sai da ya fara leƙawa ta kafar ƙofar ya tabbatar sune kafin ya buɗe, shigowa suka yi domin duba lafiyar Murja ganin kuma tana cikin ƙoshin lafiya yasa suka yi gaba, sai kuma tashin hankalin da suka taras a Labour Room.

Gawar matar da Hibba ta kashe, sun shiga ruɗu sosai ganin irin mutuwar da matar tayi da gani ba mutuwar haka nan bace, babban baƙin cikin su shine hada ɗan dake cikinta ta mutu.

Tafiya suka yi da gawar kafin gari ya waye suba dagin ta

Asubar fari Alhaji ya nemi da a sallame su domin ya lura bazai iya zaman asibitin nan ba abubuwan Almara su halaka shi.

Wajen ƙarfe takwas na safiya aka rubuta masu sallama suna fitowa suka ci karo da  Hibba dake zaune gefe, ganin su yasa ta mike tare da tarbarsu tana mai sakar ma Mahaifiyar ta murmushi.

"Abba harkun fito, nima nan asibitin na kwana can ɗakin yan jinya, Umma ya jikin."
Hibba ta faɗa tare da kallon Mahaifiyar tata.

Cikin in'ina ta Amsa da "da sauki."

Su duka suka rankaya suka nufi Gida, sam hankalin Hajiya Murja ya gaza kwanciya ganin hada Hibba cikin motar.

Dandazon mutanen dake gaban gidan nashi ne ya sashi yin parking tare da fitowa dan gane ma idanun su mike wakana a gidan nasu.

Buda masu hanya aka ŕika yi dan su ganema idanun su mike faruwa, cincirindon mutanen har cikin gida sannu kawai suke ma hajiya murja cike da jimami.

Gawar Uwani da suka gani kwance ce tasa Hajiya Murja jin wani jiri na ɗibar ta ba shiri tayi saurin yin zaman yan bori...

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/3, 6:51 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE2️⃣2️⃣_2️⃣3️⃣*
Ina ga fa Hibba ta fara ziyartar mu jiya ma mun saba number zamu sa 20_21 sai muka saba Number muka sa 21_22

...Abban Hibba tsabar ruɗewa yama rasa shin a sama yake ko kuma a ƙasa, hular dake kan shi ya cire tare da firfita da ita cike da tashin hankali.
```

"Alhaji sai dai hakuri, muma haka muka wayi gari da wannan Al'amari, sai dai ihun mai gadin ka muka jiyo yana kururuwa mun ma ɗauka wasu yan fashi ne suka dira a gidan muna shigowa muka iske Gawar mai aikin ku a yashe a ƙasa har kawo yanzu mun rasa miye yayi dalilin mutuwar ta, amma alamu sun nuna ciwo ne ya sameta dare zuwa safe Allah ya amshi abun shi, Alhaji sai dai hakuri haka Allah ya rubuta."

"Yanzu kamata yayi a yima wannan baiwar Allah sutura a kira dangin ta suzo mu sadata da gidanta na gaskiya."

Amsa kuwaa maganar makwafcin nashi ce keta yi mashi yawo cikin kai, waya ya zaro tare da kiran dangin Uwani, babu jimawa sai gasu sun iso cike da tashin hankali domin Uwani baza'a kirata da ƙarama irin matan nan ne da basu haihuwa shine ma sanadin rabuwar ta da mijin ta haka nan ta taho birni aikatau dan ta samu abinda zata rufama kanta asiri.

Wannan mutuwa ta Uwani ta girgiza duk wani mai hankali da tunani musamman Hajiya Mariya da har yanzu idonta ya kasa dena Zubda hawaye, dangin Uwani sun nema da abarsu su tafi da gawar yar uwar su ƙauye ayi mata sutura, amma Alhaji ya hana sai dai nan gidan shi akai mata zaman makoki.

An kai Uwani gidan ta na gaskiya gidan da koka shirya ko baka shirya ba indai mutuwa ta taho sai kaje, Ubangiji yasa mu cika da imani.

Kamar yadda aka saba haka akayi tsawon kwana uku ana amsar gaisuwa nan dangin Uwani suka sanar da Alhaji zasu koma gida, Abban Hibba ya ji dadin abinda dangin Uwani suka yi mashi ba kaɗan ba domin duk da suna zaune a ƙauye amma akwai wayewa a tare dasu sun dauki mutuwar Uwani a matsayin lokacinta ne yayi, dan haka da zasu tafi sha tara ta arzuƙi Abban Hibba ya haɗa masu sannan ya sanya driver ya maida su har gida.

Tafiyar dangin Uwani bata yima Mahaifiyar Hibba daɗi ba sam domin yau jin gidan take shuru babu daɗi, ga wata kewa dake matukar damun ta.

Zaune suke ita da Abban Hibba sunyi zugum kowa da abinda yake saƙawa a ranshi.

"Alhaji!."
Mahaifiyar Hibba ta kira sunan shi.

Ɗago kai yayi tare da fuskantar ta ba tare daya amsa ba.
"Alhaji ina ganin yanzu lokaci ne daya kamata mu tashi tsaye domin nemar ma Hibba magani, ka duba abubuwan dake faruwa na asibiti da kuma mutuwar Uwani, ina da tabbacin duk da sanyawar hannun Hibba."

Wani mugun kallon ya watsa mata, ji yake kamar ya tashi ya rufe ta da bugu.
"Amma ban san tsanar da kike nuna ma yarinyar nan ta kai haka ba sai yau, yanzu Murja Ɗiyar ki kike dangan tawa da kisan kai wai kam wace irin tsana kika yima yarinyar nan, to tsaya kiji in faɗa maki abinda ya faru asibiti ba komi bane face yanayi na firgici da muka shiga sakamakon ɗaukewar nepa, dan haka ki kiyayi dorama diyata wannan banzan ciwon."
Ya ƙarasa maganar a fusace tare da ficewa fuu ya bar mata ɗakin.

Binshi tayi da kallo hawayen takaici na wanke mata fuska.
"Shikenan ita haka zata ƙarasa rayuwar ta bata da wanda zata faɗama damuwar ta yayi mata magani, Sai yanzu ta tabbatar ta tafka babban kurkure a rayuwar ta wanda ba zata taba iya gyara shi ba, son zuciya duk shi ya kaita ya baro ta gashi yanzu Ubangiji ya bata ɗiyar amma kaf duniya babu wanda take tsoro sama da ita.

Ƙofar da taji an turo ce ta sanyata saurin kallon wanda zai shugo, Hibba ce sanye da wata jar riga kanta ko ɗan kwali babu, bata tanka ma mahaifiyar tata ba face zama da tayi bisa ɗaya daga cikin kujerun dake falon.

Remote ta ɗauka tare da  canza tasha.

"Innalillahi wa'inna ilaihirrajiun!."
Shine abunda mahaifiyar Hibba ta furta lokacin da tayi arba da irin firm ɗin da ake a tashar da Hibba takai.

Wani irin firm ne ake gabatarwa mai suna All of Us are dead, horuna ne suka balle cikin makarantar kwana ta daliba dan haka duk wanda suka kama shima ya zama nama.

Wani ɗalibine horuna suka biyo a guje zasu ciza, gudun ceton ratuwar shi yake inda tsautsayi yasa ɗalinbin yin tuntube da wani icce sai gashi ƙasa kafin yayi ƙoƙarin tashi tuni horunan sun yayyaɓe shi suna watan da da jinin shi.

A furgice Hajiya Murja ta sanya hannun ta tare da rufe idanunta jiki na kyarma, bata buɗe idonta ba sai da ta taji shuru alamun an canza canal, a hankali ta fara bude fuskar ta tare da kallon Screen ɗin Tv, mi zata gani? Horunan dake tsattsaye gani tayi sunyi mubayi'a ga Hibba dake zaune saman kujera ƙafa ɗaya kan ɗaya.

Ƙoƙarin barin falon Hajiya Murja ta fara sai dai mi, kafin ta kai ga aikata haka sai ji taji ƙofar falon ta rufe kanta, kafin ta ankare horunan dake cikin TV ɗin sun fara ratso glass ɗin Tv suna fitowa...

---

...Alhaji Lamaru kuwa duk inda hankalin shi ya kai ga tashi ya kasa zaune ya kasa tsaye, gadai zabe ya taho ga kuma aikin da aka sashi bai kammala ba.

Duk wani bincike da yasa ayi dan ganin ko za'a samu abinda yake nema a cikin garin amma abu yaci tura, shuru kake ji.

Maƙudan kuɗaɗe yasa ma yaran shi ga duk wanda ya samo mashi abinda yake nema, nan fa yaran shi suka fantsama cikin gari sune duk inda suka ga ana wata hidima gidajen biki dana suna, domin alƙawari ne suka dauka indai akwai yarinyar nan a dunuya sai sun samota duk inda take...

---

...Mahaifan Al'ameen iyayen Lubna suka samu tare da kai masu akwatunan lefen da akayi mata.

Tabbas ranar Gaje tayi hauka wanda bata taba irin shi ba domin cewa tayi ko a fitar da kayan kota banka masu wuta.

Mahaifan Al'ameen kuwa mamaki ne ya kashe su lokaci ɗaya suka fara kokon ton anya Gaje ce ta Haifi LUBNA.

"Dan Allah ku tafi da waɗan nan kayan, ina rokon ku da kada ku maido Lubna cikin gidan nan, na aminta daku mahaifiyar Al'ameen ina kallon tane tamkar itace mahaifiyar Lubna saboda kulawar da take bata, koda an ɗaura aure bani fatan a kawo Lubna gidan nan gudun abinda zai faru, bayan an ɗaura AureN Lubna ni zani zo har gidan muyi bankwana da ita."
Mahaifin Lubna ya karasa maganar cikin dattaku.

"Babu matsala Lubna matsayij ɗiyar mu muke kallon ta dan haka kada ka samu damuwa zamuti mata komi tamkar tana gaban ka."

Ba karamin dadɗi Mahaifin Lubna yaji ba ganin mutumci irin na waɗan nan mutane tsakanin shi dasu sai godiya.

Ko bayan tafiyar  baƙin Gaje ta bulbula tijara son ranta, amma Malam Sule bai ɗaga kai ya kalleta ba.

Ya riga yasan Gaje tayi nisa bata jin kira..

Al'amarin Leemcy kuwa ganin ta fara samun sauƙi ga kuma biki ya matso nan ta haukace kiran Feedow domin su bazama neman magunguna domin su Leemcy an dade da 6arar da mutumci a kwalta.

Wayar Feedow a kashe dan haka Zuly ta kira suka samu wata shahararriyar mai magani ta basu magunguna.

Leemcy har gobe bata haƙura ba da sai ta Raba Al'ameen da Lubna yanzu ma hidimar biki ce ta sanya ta ɗan bata lokaci kafin ta dawo kanta.

Yau kam Zuly da Leemcy Gidan su Feedow suka yima tsinke domin jin abinda ke hanata zuwa ana hidima da ita.

Suna shiga gidan ko gaisawa basu yiba suka rufe Feedow da zagi ta inda suke shiga ba tanan suke fita ba.

"Kun gama ko kuwa akwai saura."?
Feedow ta faɗa.

"Bamu gama ba hutawa muke yake shahararriyar marar daraja."
Zuly ta faɗa cike da masifa.

"Kai nifa komi zakuce sai dai kuce amma da hankali na haka kawai Leemcy in sake biye maki a kuma hadani da Uwar Garke, ran nan kunsan azabar data bani kuwa."
Feedow ta karasa maganar tare da fashewa da kuka.

Kecewa suka yi dariya a tare.
"Kin manta mu in abu ya faru mantawa muke mu tari abinda zai faru a gaba, kawai share manta jone damu a dasa daga inda aka tsaya."

"Wallahi na daku wurin Uwar Garke sai da fa ta gama bani wahala a ƙafa na dawo gida a wahalce na fara bacci sai dai naji anyi ball dani buɗe idon da zanyi naji tana in tattaro gashin ta daya maƙale a jikina in bata, kai na fa daku ranar ba kaɗan ba."

Wata dariyar suka sake 6a66akewa da ita.

"Ina gaya maku kusha kurumin ku ranar da aka kai wannan almajirar gidan Al'ameen sai dare yayi mu rufe gida mu naɗa mata bugun bugu."
Cewar Zuly da ta miƙe tana wata girgiza.
Kecewa suka yi da dariya jin shawarar Zuly

Da kyar suka samu feedow ta amince ta shirya tare da binsu.

Ta ko wane bangare shirye_shiryen biki kawai ake, duk da Al'ameen  ya hana ayi duk wani abu daya danganci party amma Leemcy sai da ta tattara ƙawayen ta gogaggun yan duniya suka kama holl suka  gwangwaje.

Tunda Bilal ya kyalla ido yaga Saro duk wata natsuwar shi ya rasa ta, ji yake bazai iya barin gidan su Al'ameen ba tare daya gabatar da kokon barar soyayyar shi ga saro ba.

Da yake cikin falon suke ita da Lubna da aka gama gyarama jiki, su na hira abinsu.

"Dan Allah Amaryar mu ina da magana da abokiyar ki."
Cewar Bilal yana sosa ƙeya.

Murmushi Lubna tayi tare da tashi ta basu wuri.
"Ƙawar mu barka da safiya."

Kamar ba zata amsa ba domin bata son renin hankali tun ba yau ta lura da take_taken Bilal.

"Ƙawar mu magana fa nike."
Bilal ya katse mata tunani.

"Wai Bawan Allah lafiya nifa na tsani ɗabi'ar naci, bashi ko tara zaka zo ka tasa ni gaba da kiran ƙawar ku ta ina na zama ƙawar ka?, kaga bani son kalar dangin da wata gantalewa."
Tana ƙarasa maganar tayi gaba tare da barinshi sake da baki.

Wani murmushi ya saki dan ya san koba komi ya samu irin matar da yake so, waɗan nan shegun yan matan nashi yasan duk zata gyara masu zama, domin shi kaf duniya yana ƙaunar Mace masifaffciya mara hakuri in an tabo ta sai kuma ga Saro  Allah ya haɗa shi da ita.

Ta bangaren Hajiya Mariya kuwa zawo an rasa maganin shi komi tasha yaki tsayawa ta koma wurin boka amma a banza dan haka yanzu sai dai pampers take sawa, ga kuma hidimar biki da aka kacame da ita a cikin gidan.

Hajiya Salima tamkar ita ta haifi Lubna haka ta hidima da ita, mussaman ta ɗauko mai gyaran jiki daga maiduguri ana gyare mata Lubnar ta, kayan ɗaki kuwa dana kitchen ita tayi mata komi ba tare da gajiyawa ba, domin hajiya Salima ta cika mutum.

Rana bata ƙarya sai dai Uwar ɗiya taji kunya, a yau ne ɗaruruwan jama'a suka shaida auren AL'AMEEN SUFYAN GARKUWAN TALAKA da amaryar shi LUBNA SULAIMAN sai kuma HALIMATU MARWAN HARKA akan sadaki kowace dubu Hamsin , ɗaurin aure ne daya samu halartar manyan mutane ta ko wane bangare yan media da sauran kafafen sada zumunta suma ba'a barsu a baya ba.

Malam Sule dake cikin manyan kaya na kece raini da mahaifin Al'ameen ya ɗinka mashi ba tare da sanin kowa ba wasu hawayen farin ciki yaji sun wanke mashi fuska, hannuwa ya ɗaga sama tare da yima Allah godiya.
"Ubangiji nagode maka bisa ga wannan ni'ima da kayi mani, Allah na sauke nauyi na farko Ubangiji ka bani ikon sauke nauyin da yafi ko wane nauyi a wurina, ya Allah ka Albarkaci Lubna ka Albarkaci iyalan Alhaji Sufyan Allah ka saka mashi da sakayya mafi Alkhairi, ya Allah nagode na ƙara gode maka."
Ya karasa maganar tare da share hawayen fuskar shi.

Al'ameen kuwa jin wasu hawaye yayi daya rasa dalilin zubar su, wani nauyi yaji zuciyar shi tayi mashi, wai yau shine da Aure rayuwa kenan.

Bayan kowa ya gama tafiya mahaifin Lubna dana Al'ameen mota suka shiga domin zuwa gida yayi Sallama da Lubna.

Duk wani sukuninta yau babu gabanta keta faɗuwa, wani kuka ne ya kufce mata.
"Yau an ɗaura auren ta abinda ko wace Uwa ke gurin taga irin ranar ga ɗiyar ta amma ita mahaifiyar ta na raye babu damar ta rabeta bare ma ayi maganar samun farin ciki a wannan rana, ta ɗauki wannan a matsayin ƙaddarar ta."
Ganin tana kuka yasa Saro matsowa tana kwantar mata da hankali.

Sallamar Hajiya Salima ce ta sanyata kara fashewa da kuka domin tasan Mahaifinta ya karaso.

Kama ta tayi tate da nufar part ɗin Alhaji da ita, kaɗan ta hana Malam Sule zubda hawaye lokacin da yaga an shigo da Lubna.

Nasiha ya fara mata mai ratsa jiki.

"Alhamdulillah godiya ta tabbata ga Allah daya nuna mana wannan rana mai tarin Albarka, Lubna yau rana ce mai matuƙar amfani a wurin ki ranar da ina fatan kada ta sake maimatuwa a rayuwar ki, Lubna a yau kin bar hanmuna kin koma hannun mijinki, kinbar gida na kin koma gidan mijin ki, kiji tsoron Allah a cikin lamuran ki nasan ke mai sauƙin halice, Lubna komi zaki tarar a gidan mijin ki kiyi haƙuri wata rana zai zama tarihi, a yau a dai_dai wannan lokacin naso sanar dake wani abu a gaban mahaifiyar ki amma kash! Gaje tayi nisa bata jin kira, Ubangiji ya albarkace ki ya baki ikon cinye duk wata jarabawa dake fuskantar ki Allah yayi maki Albarka." Malam Sule ya ƙarasa maganar tare da goge wani guntun hawaye dake neman kuftowa.

Lubna kuwa kuka take tamkar Ranta zai fita mahaifinta ta riƙe gam ta kasa furta koda kalma daya ce.

Da kyar Hajiya Salima ta 6an6are Lubna a jikin mahaifinta.

Ita ma Hajiya Salima nasihar ce tayi mata sosai.
"Lubna yadda na ɗauki Al'ameen haka na dauke ki ki taimaka duk wata matsala ki sanar dani kada ki zama mai boye mani abubuwan da suka shafi rayuwar ki Ubangiji yayi maki albarka ya baki sa'ar shiga gidan miji lafiya.
Da ƙyar aka raba Lubna da Hajiya Salima su duka suna kuka suka rabu.
Nan aka wuce da ita gidan miji.

Leemcy kuwa ita da ƙawayen ta tuni suma suka shige mota sai gidan Al'ameen, gaf da magriba aka sada su da ɗakunan su.

Masha Allah haɗaɗɗen gida Alhaji Sufyan Ya sai ma Al'ameen daka shiga babban falone tsakiya sai ɗakunan su Lubna.

Tun bayan kawo Amaren Ƙawayen Leemcy suka jona manyan Sifikun falon suka kunna wata waƙa ta wasigidi😂 Suna cashewa abinsu, sudai su Lubna daga ita sai Saro cikin ɗaki suna labari babu wanda ya fito falon.

Bayan sun gama chashewa nan suka hau labari wai Leemcy ce da aure harda kishiya lallai ta yi sanyi, ita kam jin abinda ƙawayen ta ke faɗa ji tayi kamar ana zuga ta.

"Nikam ina maganar koyama waccan jakar ta ɗaka hankali."
Zuly ta faɗa tare da miƙewa.

"Yana nan babu inda yaje yanzun nan zamu kaddamar mata."
Wata da ake kira Ruwai ta faɗa.

Feedow kuwa ji tayi cikin ta yayi wata katsawa dan tasan aka bigi Lubna yau kashin su ya bushe.

A ƙalla ƙawayen Leemcy sun kai su goma masu kwana a gidan dan haka dakin Lubna suka nufa.

Kamar suyi hauka ganin ɗakin kulle, babu yadda suka iya haka suka juyo ɗakin Leemcy cike da takaici.

Nan suka dawo suna mitar zasu hade da ita gobe ai bata tsira ba, Feedow ce ta nufi Toilet ɗin da ke cikin ɗakin zata yi fitsari, a guje ta Fito ta tare da bi ta saman waɗan da ke zaune saman gadon ta haye can ƙurya tana faɗar.
"Uwar Garke wallahi ku shirya Uwar Garke ce a Toilet ɗin.

Zuly da Abun ya ƙuleta masifa ta fara.
"Uwar Garke nan tirken Awakai kika gani da zaki ce kinga Uwar Garke."?
Maganar ta ce ta maƙale sakamakon ƙofar ɗakin data rufe kanta ita kuma ta Toilet ta bude da karfi.

Uwar Garke ce cikin Mummunar suffa ta fara yo gaba sai wasu jinga_jibgan kadan garu da girman su yakai girman ɗan akuya, su dai waɗan nan ƙadan garu tsaye suke tamkar mutum suna tafiya da kafar su ta baya hannuwan su na gaba kuwa riƙe suke da mulmulallen Kulki.

Wata mahaukaciyar dariya suka kece da ita data haddasa ma ɗakin girgiza...

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/5, 9:44 AM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

______________________________

*PAGE 2️⃣4️⃣_2️⃣5️⃣*
...iface_iface suka fara ganin wannan bala'i dake tunkaro su, domin tunda Uwar data haife su basu taba ganin kaɗan gare na tafiya da ƙafafun shi ba ga kuma Uwar Garke da kamanninta kaɗai sun isa su sanya ka sakin guntun zawo

Sai da suka gama dariyar su mai isarsu kafin su turbune fuska tare da kallo su Ruwai da suka dunƙule wuri ɗaya jiki na kyarma.

"Madalla da haduwa ta biyu haduwar da jikin ku zai gaya maku zaku gane baku da wayo yau, wace mara ɗa'a ce tabi ta saman ɗana dana aje ta wuce sauran ma suka take mata baya."? Uwar Garke ta ƙarasa maganar tare da nuna yan matan da hannu.

"Kwarankwatsi dubu bani bace sai dai ko Ruwai."
Zuly ta faɗa tare da nuna Ruwai.

"Amma Alkah ya isa tsakanina dake ni zaki jona ma masifa."?
Cewar Ruwai tana Ruwai

Kecewa da dariya Uwar Garke tayi.
"Duk ina zuwa kanku, musamma ke mara kunya mai shegen surutu da baƙar aniya, mu kika kira awaki ko yau zaki gane baki da wayo."
Kafin kace mi wata iska ta fizgo Zuly da Ruwai ta dire su gaban Uwar Garke.

Dauke su aka rika yi da mari ta ko ina, banda ihun su babu abinda kunnuwan ka zasu iya jiyo maka, dakatawa aka yi da marin su kafin Uwar Garke ta fara magana.

"Kasancewar kune Oganni masu shirya mugunta ga kuma dan Auta da kuka taka hukuncin ku sai yafi na kowa tsanani."
Wani yagalgalallen jinjiri mai suffar tunku Uwar Garke ta miƙo masu.
"Wannan da kuke gani ɗana ne shine kuka taka, yau kimanin shekaru ɗari cif! Amma baiyi
```

dariya ba dan haka ku sanya shi dariya ko jikin ku ya gaya maku, duk wasan da kuke muddun yaki dariya to jikin ku ne zai gaya maku maza ku fara."

"Mun Shiga Ukku mun lalace, yau ni Ruwai na ɗebo ruwan dafa kai na, yanzu wannan Tunkun zamu yima wasa, amma dai Allah ya isa tsakanina dake Leemcy, kin san gidan ki haka yake kika sa muka zo."

"Bake kika shiga ukku ba ni zulai nina shiga tara, yanzu wannan halittar zamu saka dariya kiji fa wani rantalelen kai kamar na Uwar turwa."
Rufe bakin Zuly yayi dai_dai da ƙarasuwar kadangarun inda suke tare da rufesu bugu ta ko ina.

Ihu suke suna kiran ƙawayen su dake saman gado ido ya rena fata, sai da suka yi masu lilis kafin su miƙe su fara yima na ƙurungu wasa suna hawaye, kallon su yake da ƙwalelen idon shi gida ɗaya dake tsakiyar goshi tamkar na besfa.

Fashewa yayi da kuka, sai ga Uwar Garke a guje.
"Miya faru ɗan Lele."?

"Tsunkulina suke sam basu iya wasa ba."
Ya fada tare da buɗe bakin shi mai kama da ƙofar gari.

"Tsunkuli, haba shiyasa naga kanata ƙara haɗe rai."

Nuni tayi da hannu sai ga su Zuly anyi sama dasu an ɗaure ƙafadaun su da fanka kan su kuma yana reto ƙasa, ihu suke tamkar zasu fasa maka dodon kunne ganin azabar da zatayi masu yasa suka kasa dena ihu, gudun da fankar ta fara ne yasa Feedow sakin wani Guntun fitsari tare da fashewa da kuka.

"Hhh Faddausi! Kice munyi haɗuwa ta biyu, maraba lale_lale."
Uwar Garke ta faɗa tare da kallon sauran yan matan dake maƙale da juna wasu har sun fara hawaye.

"Yau kowa sai ta goya ɗan lele kai komi yace sai anyi mashi ko jiki yayi tsami."

"Dan girman Uwarki da Ubanki kada kiyi mani haka, ki kwashi tawagar ki ki bar mani ɗaki."
Cewar Leemcy jiki na ciri.

"Hhh! Mai gayya mai aiki, ai mantawa nayi dake domin ranar nan kinci bashi na baki biya ba,

dan mugunta in kaina ya faɗi sai kin tsukuleni kike ɗauko shi, yau hukuncin ki shine goya dan lele har gari ya waye.

"Laaah mun shiga Uku mun lalace."
Leemcy da abokan ta suka faɗa a tare.

"Ai yau muna tare daku har gari ya waye, duk sai naga kunyi laushi domun naga har yanzu da sauran ku."

Leemcy da aka sha kwalliyar Amarci sai ga ta ta bige da goya na ƙurungu, inda zaka san na Kurungu yafi Uwar Garke mugunta sai an goyashi sai ya ballen zanin goyaon  ya faɗo ƙasa da gangan, nan Uwar Aljanu zata riga gama kan Leemcy da bango tana sa waɗan nan jibga_jibgan ƙadangaru suna ma Leemcy ruwan kulki.

"Na dawo kanku."
Uwar Garke ta faɗa tare da nufar su Feedow.

Ganin ta nuho su gadan_gadan yasa su tarwatsewa suna ihu kowa yayi wata hanyar suka bar Feedow kadai data kasa tabuka komi.

"Hhh! Ke ba zani cuce ki da yawa ba, ai nan gaba ƙawance zamu ƙulla dake dan haka taso ki ƙarasa ƙirgar da baki ƙarasar ba."

Duk da a ƙirgar gashin Uwar Garke Feedow tasha azaba amma tafi ƙaunar ƙirgar fiye da komi domin ita kaɗai tasan azabar data sha, amma haka ta dage tana kirga gashin uwar garke.

Sauran Kawayen Leemcy dake neman hanyar guduwa tattaro su aka yi wuri ɗaya ƙadangarun nan suka ci gaba da yi masu ruwan kulakai ta ko ina.

Tabbas ranar ƙawayen Leemcy sunga tashin hankalin da basu taba ganin irin shi ba, wasu har suma suka yi tsabar azaba ga kuma na saman fanka dake shan tasu azabar su ma.

Leemcy kuwa dake faman goyan naƙurungu jikin ta ya gaya mata domin ji take tamjar ta goya ƙayoyi haka yake soke mata baya ga wani cizo daya sauke mata a jiki yau kam kowa ya gane baida wayo.

Haka suka kwana ana abu ɗaya asuba nayi Uwar garke da iyalan ta suka bace bat.

Ruwai da Zuly da aka dora bisa fanka a galabaice suma suka miƙe jiri na ɗibar su

Duk da akwai sauran duhun asuba haka kawayen Leemcy suka riƙa ficewa gidan a guje, ganin saura su hudu yasa Leemcy tarbe kanyar fita.

"Haba Zuly yanzu kuma tafiya za kuyi ku barni, haka ƙawaye na kada kuyi mani haka."
Leemcy ta faɗa cikin marairaicewar murya.

"Nabi ƙawayen ki da gudu buje a hannu, ai Leemcy nida gidan ki har abada daga yau mun raba jiha wai mune da hawan fanka kai yau munga tashin hankali."
Ruwai ta faɗa tare da goge guntun hawayen ta.

"Kema kika tsaya bata amsa aini gaf nike da ɗauke Leemcy daga saman hanyar nan in wuce tun kafin waccan Uwar Garken ta dawo."
Zuly ta ƙarasa maganar cike da jin haushin Leemcy.

"Ni duk kune ku ka jaza mani bala'i, sai da nace bani zuwa harkar bikin nan amma kuka je har gida kuka tattago ni gashi nan kun yi sanadin da kowa sai da yaji jiki a cikin mu."
Feedow ta karasa maganar tana share hawaye.

Ganin Leemcy ba zata basu hanya ba yasa suka direta wuri ɗaya tare da barin gidan a guje.

Leemcy kuwa ganin saura ita ɗaya cikin ɗaki kamar mayya ya sata fashewa da kuka tate da kifa kanta bisa gado tana kukan wannan abu da ƙawayen ta sukai mata...

---

...
Hajiya Murja Kuwa ganin wannan sabon salo da akazo dashi ya sata yadda tabbas yau kwanan ta sun kare domin duk wata azaba da take sha Hannun Hibba ta yau tafi ta kullum.

Tamkar ana amayo su haka suka riƙa fitowa daga cikin glass ɗin TV suna cika falon.

Wani karfi ne ya zoma Hajiya Murja ji tayi ta mike da gudu ta nihi ɗakin ta a guje ta maido ƙofa ta rufe.

Wani gumi ne ya shiga wanke mata jiki abinda bata batayi ba shine yau ta samu bakinta ya ambato wato addu'a, wata irin kara ta riƙa jiyowa tamjar ana tafiya bisa rihin dake ɗakinta, rikicewa ta karayi amma duk da haka bakinta bai dena furta addu'a ba.

Wata mahaukaciyar dariya taji an kece da ita.
"Yau kinyi galaba a kanmu amma zamu hade nan gaba."

Taji wata murya ta faɗa.

Ajiyar zuciya Hajiya Murja ta sauke tare da sulalewa kasa tana maida numfashi, tabbas tasan komi ya faru i ta ce sila son zuciya baiyi ba a rayuwa ta salwantar da rayuwar wata wadda ta kasance mafi kusanci da ita mafi soyuwa a gare ta domin cikar wani burin su yanzu gashi nan Allah ya bata diyar amma tana ƙoƙarin ganin bayan ta.

"Allah na tuba Ubangiji ka gafarta mamu abinda muka aikata a baya, Allah badan halin mu ba ya Allah."
Ta karasa maganar tare da fashewa da kuka.

Yinin ranar sam ta kasa koda buɗe kofar ne bare kuma asa ran zata fito, sai gaf da magriba Abban Hibba dawowar shi ita ce ta yi sanadin buɗe kofar.

Tambayar duniya yayi mata amma amsa daya taje bashi babu komk.

Da haka har ya gaji ya kyaleta, daren ranar sam mahaifiyar Hibba bata rintsaba domin da zaran ta rufe ido Hibba take gani da wuka tsirara tana neman kashe ta.

Babu yadda ta iya haka ta nufi Toilet domin yin Alwallah, dukawar da zata yi ji tayi wani abu na gurnani ta bayan ta, saurin juyawa tayi, nan tayi arba da wata jibgegiyar mage baƙa wuluk kanta ya gutsure ga wuyan ta na zubda jini.

A guje ta baro Toilet ɗin tare da faɗawa bisa gado tana kiran sunan Abban Hibba
"Ka tashi mage ce babu kai a tattare da ita."
Duk da baccin daya ɗauke shi amma jin wannan magana firgigit ya buɗe ido tare da kallonta.

"Mage kuma, yanzu dai magen tana ina."
Ya karasa maganar tare da murtsuke idon shi.

"Tana cikin Toilet yanzu haka nasan ta kusa fitowa."
Hajiya Murja ta ƙarasa maganar tare da nuna mashi ƙofar Toilet ɗin.

"Yanzu abinda za'ayi bani ƙuryar gadon nan."
Cewar Abban Hibba yana ƙoƙarin barin farkon gadon.

"Kamar ya in baka ƙurya, dan Allah kaje ka fiddo mana magen can."
Cewar Mahaifiyar Hibba.

"Wa! Lallai yau na tabbatar baki ƙaunata, nifa na gaji da waɗan nan abubuwan gobe gida zamu canza ina ga hada matsalar gidan nan.

Ranar a haka suka kwana zaune babu batun bacci, gari na waye wa Abban hibba ko kalaci bai yi ba ya bar gidan, mahaifiyar Hibba kuwa tsoron ta ɗaya kada Hibba ta maimaita abinda tayi jiya.

Tun tana sa ran ganin Hibba ta fito har ɗaya da rabi na rana ya wuce amma shuru, miƙewa tayi tare da shigewa kitchen ta dafa abinda zata ci, abinda Hajiya Murja ta lura dashi shine Hibba bata cikin gidan, domin har kawo yanzu bata ga gilmawar ta ba.

Hibba kuwa Kamar yadda ta saba duk rana sai ta ziyar ci dajin nan yau ma haka ce ta kasan ce, bata baro jejin ba sai da marece yayi liƙis.

Tafiya take a hankali tamkar bata son taka ƙasa, kai kace ba son tafiyar take ba.

Titi ne zata tsallaka amma kota duba taga shin akwai motar da tazo wucewa ko aa kanta ta kutsa a nitse zata tsallaka titin, wani mahaukacin hon ne ya danna mata tare da take birki babu shiri, duk da kadan ta hana ya tashi da ita amma ko a jikin ta saima wata tsayuwar ƙasai ta da tayi a tsakiyar titin, kasan cewar duhun magriba ya fara titin babu cukowa sosai.

A fusace ya fito domin dama shi kwallon ɗan iskane bai da mutumci ko alama, ya banke mutum ya ƙi tsayawa wannan aikin shi ne.

A gusace ya fito daga motar tare da ɗauke Hibba da mahaukacin mari.
"Ke wace irin dabbace marar hankali da tunani, titin na Ubanki ne da zaki taho ba tare da kin duba ba, kodan dama ku ɗiyan talakawa haka kuke baku da nutsuwa ko alama, zaki matsa mani a hanya ko sai nabi ta samanki na wuce."?
Saurayi da kallo daya zakai mashi ka tabbatar ba yakai maƙura wurin rashin tarbiyya.

Mutane ne suka fara taruwa ganin an kashe titin ga Hibba tsaye mamaki ya kashe ta kallon shi kawai take.

Nan mutane suka hau bata haƙuri suna ƙoƙarin janyeta, fashewa da dariya da suka ji tayi ne yasa suka sake ta tare da ja da baya, domin sun tabbatar bata da hankali.

A hankali kowa ya dare ya basu wuri, kallon shi kawai tayi tare da yi mashi wani murmushi da ita kaɗai tasan ma'anar shi.

A fusace ya ja  motar shi ya bace a wurin.

Gudu yake tamkar zai tashi sama domin bai da wani buri daya wuce ya ganshi a hotel ɗin da

suka kama zasu gabatar da shagalin su.

Wayar shi da ya ji ta fara ruri ce  yasa ya ɗan rage gudun da yake tare da juyawa baya ya mika hannu zai ɗauko ta.

Caraf idanun shi suka sauka cikin na Hibba dake zaune a kujerar baya tana sakar mashi murmushi, tsabar firgici bai san lokacin daya taka wani wawan birki ba...

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/8, 8:47 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE2️⃣6️⃣_2️⃣7️⃣*

```Barkan mu da shan ruwa Ubangiji ya amshi ta wannan  azumi na Ashura da muka yi Allah ya gafarta mana zunuban mu 😇```

....Motar ya fara ƙoƙarin budewa cike da tsoron abunda ya gani.

"Kar ma kayi ƙoƙari guduwa domin duk inda kaje sai na bika na aiwatar da abinda nayi niyya dan haka kada ma ka wahalar da rayuwar ka wajen guduwa."

Cewar Hibba dake hakimce a kujerar baya zaune.

"Dan girman Allah kiyi mani rai kada ki kasheni in kudi kike so zani baki."
Cewar shi jiki na kyarma.

Kecewa tayi da dariyar da ta kusa sanya shi sakin fitsari
"Kai har kana tunanin ina da buƙatar kuɗi?, gidan mu gaba da baya kudin ne dan haka rike abunka Rayuwarka ita ce muke buƙata."

Kafin saurayin yayi wani yunkuri tuni ta cafki wuyanshi tare da kafa mashi hakora a wuya tana zuƙe jinin jikin shi, a haka har ta gama tare da sakin shi ya kwanta bisa sitiyarin motar.

Fashewa tayi da dare tare da furta.
"Mugunta yanzu na fara ɗaya bayan ɗaya sai na ƙarar da duk wanda ya saba mani kafin in dawo kan Murja da mamman wato mahaifin murja.

Hajiya Murja kuwa ganin har marece yayi liƙis babu Hibba a gidan gyalenta ta zara ta kira drive ya kai ta gidan mahaifinta.

Tun bayan gaisawa da suka yi da mahaifinta ta kasa furta koda kalma daya ce.

Hawayen da yaga suna bin fuskar Murja ne ya ƙara tayar ma shi da hankali, a rikice ya fara tambayar ta.
"Murjanatu lafiya?, wa ya rasu, mike faruwa."?

"Baba da mutuwa akayi zan iya cewa da sauƙi, mutuwa tafi abinda ke faruwa damu sauki, Baba sirrin da muka boye a bayan ƙasa ya tone ya fito."

Wata razana mahaifin nata yayi, "kada kice mani asirin abinda muka boye acan baya yau ya karye."?
Ya faɗa jikin shi na ciri.

"asIrin ya tono tun ranar da Hibba tazo duniya, mutum yana haihuwar ɗaya ya son shi ya ƙaunace shi kodan yaron ya shaƙu dashi amma ni sabanin haka nike sabo da Hibba, kullum bata ƙaunar in rabe ta data fara girma sai ta fara fito mani a suffar aljanu tana ƙoƙarin kashe ni in taƙaice maka zance yanzu haka da ƙyar na gudu na baro gidan, wallahi Baba ina cikin bala'in da ban taba tsammani b."
Ta ƙarasa maganar tare da Fashewa da kuka.

Tsabar tashin hankalin daya shiga kasa zama yayi haka ya shiga yin safa da marwa cikin falon.

"Ina fata dai baki gayama Mahaifin Hibba gaskiya ba."?
Alhaji mamman ya faɗa.

"Eh har yau bai san miye asalin abun ba."
Hajiya Murja ta faɗa.

Komawa yayi ya zauna bisa ɗaya daga cikin kujerun da suka yima falon ƙawanya.
"Tabbas Ubangiji yayi gaskiya duk abinda ka aikata a boye wata rana sai ya bayyana, ko haƙƙi Mahaifin Hibba kaɗai ya ishemu, mun aikata babban kuskure munyi shirka mafi muni a rayuwar mu yanzu ga Mulki nan nayi nagama har ya zama tarihi amma abinda na aikata na bibiyata, babu ko tantama ruhi ne ke rayuwa jikin Hibba kuma bazai taba gyalemu ba har sai yaga bayan mu."

Jin wannan magana da mahaifinta yayi sai da taji cikin ta yayi wata kara ƙuuuuw!

"Ya zamu yi, wallahi in ba'a ɗauki wani mataki ba Hibba kasheni zata yi ni nasan ta kai na zata fara."
Hajiya Murja ta karasa maganar a firgice.

"Ki kwantar da hankalin ki babu abinda zai same ki domin gobe zani je gidan wani amintaccen Boka na komi ya kusa zuwa ƙarshe yanzu kinga dare ya kusa ki tashi kije gida zani nemeki ko mi kenan."

Jiki babu kwari ta baro gidan mahaifin nata, tun kafin ta ƙarasa cikin gidan gabanta keyin wata mummunar faɗuwa.

Jiki ba kwari ta fito daga Motar tare da nufar cikin falon, ƙafar da zata saka cikin falon tayi saurin ja da baya sakamakon abinda idanunta suka gane mata, babu shiri ta saki duk wani abu dake hannunta suka tarwatse a ƙasa...

---

Al'amarin Mariya kuwa kullum ƙara ta'azzara yake gashi abun biyu ya haɗe mata ga zawo ga Kuma Fadila data gudu tabar gida tun lokacin bikin Al'ameen har yau bata dawo ba.

Wannan baƙin cikin yafi damun  Mariya fiye da zawon da take 6arkawa, ji take tamkar zuciyar ta zata tarwatse, wanda take gurin taga ya lalace amma shuru sai ɗiyar ta ce zata bi duniya aikam sai dai kowa ya sara domin alƙawari tayi ko zatayi yawo tsirara sai taga bayan Al'ameen.

Mariya dake fama da ciwo Shiryawa tayi ba tare da sanin kowa ba ta kama hanyar gidan boka.

Shi knshi bokan yayi matuƙar mamakin ƙarfin hali irin na Hajiya Mariya, duk abinda ya faru da ita amma bata daddara ba.

Bayani ta Gama kora mashi, kecewa yayi da dariya
"An gama halakakkiya komi kika nema kin samu, zamu baki magani kije gidan Al'ameen ki baɗa ma shi a bakin kofa, muddun ya tsallaka to fa shida garin nan har abada zai shiga duniya ne ba za'a sake koda jin lanarin shi bane har abada."

Jin wannan bayani na boka Hajiya Mariya ji tayi tamkar ta zuba ruwa ƙasa tasha.

Cike da zallar farin ciki ta baro gidan bokan, koda ta dawo gida bata yadda wani ya fahimci ta fita ba domin ansan yadda take 6arka zawo babu inda zata iya zuwa.

Tun bayan anso maganin ta boye duk wasu mugayen halayen ta domin So take ta samu hanyar da zataje gidan Al'ameb da sunan taje ganin yadda amaren suke.

---

...Leemcy kuwa ta rasa mike mata dadi, "a ce wai ita ce za'ayi auren ta amma kawayen ta duk sun gudu sun barta, bazai yiyuba dole taje a duba mata miye keson zauta ta haka, wannan al'janar ta fara wuce gona da iri."
Da wannan tunanin ta kwanta gefen gado tana tunanin irin tsiyar da zata tsulama Lubna, wani murmushin mugunta ta saki.

Cikin ta da taji yana ƙugi ne yasa ta ficewa tare da nufar inda Kitchen yake, turus! Leemcy tayi ganin Saro ta zage sai aikin abinda zasu ci take.

"Wace kazama ce nan da shigo mana kitchen?, Uban waye ma ya shigo dake cikin kitchen ɗin nan."?
Leemcy ta karasa maganar tana wani ya mutsa fuska tare da toshe Hanci.

Duk da zagin da aka yi mata ya daki zuciyar ta amma basarwa tayi tare da murmushi.
"Barka da safiya amaryar mu an tashi lafiya."
Saro ta fada cikin girmamawa.

"Wace ce amaryar? Allah ya sawaƙe ni nafi ƙarfin amarya sai dai uwar gida, kitattara tsumman rayuwar ki kibar cikin kitchen ɗin nan tun kafin in kifa maki mari, koda yake shi dama talaka duk inda yake bai iya samun wuri ba yanzu zai nuna halin talauci daya gada wurin iya..."
Zazzafan marin da Saro ta ɗauke ta dashi ne yayi sanadin hadiye sauran maganar ta.
Kafin Leemcy ta dawo daga hayyacin ta Saro ta zaro wata zundumemiyar wuƙa tare da shake Leemcy.

"Kice tak! Dan girman Allah, kisake fadar wata magana idan ban luma maki wannan wukar a tsakiyar ciki ba kowa ya huta, yau zaki tantance tsakanin saro bala'i da Lubna akwai banbanci harni zaki buɗe baki ki zaga, in takamar ki hauka ni na zarta ki  hauka, zan farke maki ciki inga in akwai abinda zai faru zaki gane akwai waɗan da sun zarta ki rashin kunya sun shanyeki."
Saro ta ƙarasa maganar tare da ɗago sharbebiyar wuƙar ta

"Anti saratu wayyo wallahi bansan ke mahaukaciya bace da bazani taba ki ba, ki gafar ta mani inda kike ma ba zani kuma kallo ba In ma kince in shige ɗaki in kulle kai na sai kin tafi na rantse maki zanyi."
Leemcy ta ƙarasa maganar tare da sakin wani guntun fitsari,domin tunda take yau ta fara ganin wuƙa tsirara a gaban ta.

Jefar da ita Saro tayi tare da furta.
"Bace mani da gani."
A guje Leemcy ta arta a na kare.

Saro kuwa wani tausayin Lubna ne ya kama ta tasan tabbas Lubna zata wahala wurin Leemcy.

Break fast ɗin su ta ɗauka tare da nufar ɗakin Lubna.

Kasancewar rabon su da abinci tun jiya yasa basu bata lojaci ba suka cinye shi a ƙaramin lokaci.

"Lubna!"
Saro ta kira sunan ta.

Jin yana yin da ta kira sunan ta yasa ta ɗago kanta domin tasan lallai magana mai matuƙar muhimmanci zasu yi.

"Lubna yanzu ba lokacin tsoro bane kada ki zauna Leemcy ta rika gana maki azaba domin ba zamanta ba kike Zaman mijin ki kike, wannan abokiyar zaman taki ba mutuniyar kirki bace karki so kiga yadda muka yi da ita, in ta masam maki wallahi Lubna ina gaya maki kiyi mata Hauka mai sugar in kuna kika tsaya suka rika gana maki azaba ke kika sani."
Nan Saro ta kwashe kaf abinda ya faru tsakanin su da Leemcy ta gayama Lubna.

"Innalillahi wa'inna ilahirraji'un Saro kin ballo mani aiki nasan Al'ameen kaina zai huce."
Lubna ta fada kamar zata yi kuka.

"Dake da Al'amern ɗin da haɗe ku a turmi na ƙulƙule, kedai bazaki dena wannan mugun tsoron ba a rayuwar ki ko, to ki tsaya hawan jini ya kama ki a banza."
Banko ƙofar akayi da ƙarfi ta bugu da bango.

Al'ameen ne rike da hannun Leemcy tsaye yana aika masu mugun kallon.

Saro ko a jikin ta domin babu alamun razana bare wani tsoro a tattare da ita, sa6anin Lubna da wata zufa ta hau wanke ma rabin Fuskar ta.

"Wace lalatacciyar ce a cikin ku take da zarrar yima mata ta barazana da wuƙa.

"Ba'ayi lalatattu ɗaya sai dai biyu, nice nan nayi mata ba kuma barazana nike ba domin ni nan da kake gani na karshen rashin hankali har certificate aka buga mani na hauka, dai_dai nike da zamanin ku in akwai magana kuma ka matso inda nike."
Saro ta karasa maganar tana jefa mashi kallon jikin ka zai gaya maka.

Mamaki ne ya kashe Al'ameen na rashin tsoro irin na saro, wai yau shine mace ke gayama magana kuma ya lura indai ya hayema waccan saron tabbas kashin banza zai sha domin da gani ta fishi iya hege.

"Wuce mutafi ɗaki Sweety, ke kuma saro kike ko sarai kinyi sa'a ina cikin Angon ci bata faɗa nike ba da yau sai jikin ki ya gaya maki."
Ya karasa maganar tare da kama hannun Leemcy suka yi gaba.

"Duk yadda ka kirani haka nike, ai yau daka matso da ka gane shayi ruwa ne sauƙin ka ɗaya kai mijin ƙawata  Ina ganin ɗan mutumcin ka."
Saro ta ƙarasa maganar tana Ta6a hannuwa

"Saro yau na shiga ukku a gidan nan, sai ya kusa kashe ni."
Lubna ta karasa maganar kamar zata yi kuka.

"Ke kina bada mata wlh, in ni ce ke ka nuho ni zaka buga buɗe rabin fuska ta zanyi nasan kai ma ranar jikin ka zai gaya maka."

"Aa bani iya cutar da Al'ameen."
Cewar Lubna.

"To ai sai ki tsaya su mai daki kamar jaka, kinga nasan inna nacan a ƙule domin bataso nazo bikin ki ba bare har in kwana, baba ne ya barni dan haka yanzu tashi mu gyara ɗakin nan ni in wuce."

Saro bata bar gidan ba sai da ta tabbatar sun gyara ko ina kafin itama ta fice, Lubna kuwa wata irin kewar gida taji tazo mata lokaci ɗaya wasu hawaye suka balle a fuskarta.
"Ubangiji ka kara mani dangana da juriya."

Leemcy Kuwa Uwar kissa da makirci bata bar Al'ameen ya baro ɗakin ta ba har yamma.
Lubna baiwar Allah ko abinci rana bata ci ba ga wata azababbiyar yunwa dake cinta.

Sai da ta tabbatar basu cikin falon kafin ta lallaba ta nihi kitchen,  abu mai sauki ta dafa jaluf ɗin taliya da bushasshen kifi , tana fitowa suka ci karo da Al'ameen abincin ya bare mashi a jiki.

Wata kyarma ce ta kwace mata domin yau tasan kashin ta ya bushe.

Wani mugun kallo ya watsa mata tare da fara zare belt ɗin dake jikin shi yayi tare da nufar Lubna.

Ta ko ina ya cigaba da zuba mata shi tun tana ihu har ƙarfin ta ya ƙare tayi shuru.
"Dama ina cike dake saboda nasan wannan ƙawar taki ke kika zugata ta ke koƙarin cutar mani da mata dan haka wannan somin tabi ne, sai kin kwammace baki yarda da akayi auren nan ba, baƙa mummuna dake kullum fuska a rufe saboda tsabar munafirci."
Ya karasa maganar tare da tsallake ta ya wuce.

Da kyar ta samu ta shiga ɗakin tare da zubewa kan gado ji tayi kanta ya fara juyawa alamun ciwon ta zai tashi, miƙewa taso yi domin ta rufe ƙofa gudun kada ta cutar da wani, kafin tayi yunƙurin miƙewa ji tayi an fizgota an jefa saman gadon, wata mahaukaciyar ƙara ta saki lokaci ɗaya ta fara harbr_harbe har ta fado daga saman gado.

Leemcy na ɗakin ta tarika jiyo ihun Lubna, a guje Leemcy ta baro ɗakin ta dan ganema idon ta mike faruwa a ɗakin Lubna, babu neman izini haka Leemcy ta afka cikin ɗakin, abunda taga Lubna nayi ya sa ta tsorata  tayo baya zata fice a ɗakin, sai dai kafin ta kai ga fita ƙofar ce ta rufe kanta ji kake garam!....

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/9, 3:53 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE 2️⃣8️⃣_2️⃣9️⃣*
...Hajiya Murja da tayi mutuwar tsaye kasa motsi tayi domin tasan yau tana cikin wani mugun yanayi, sake kafe murjar dake cikin ɗakin tayi tare da nuna ta da yatsa.

Tuntsurewa da dariya jabun Murja tayi tare da mika hannunta Luuuw yaje ya fizgo ainahin Murja ta gaskitaya cikin ɗakin tare da dire ta a gaban jabun murja.

"Kina mamaki yadda na koma sak irin ki ko? To wannan kaɗan daga cikin aikina ne, batun yau ba nasha gaya maki keda nutsuwar ruhi har abada sai kin za6i ki mutu a maimakon halin da kike ciki."
Jabun Murja ta ƙarasa maganar tare da kife Murja ta ainahi da wani wawan mari.

Zafin marin sai da ya haddasa mata katantanwa ta kife ƙasa, Jabun Hajiya Murja ce ta sanya hannu ta shaƙe Murja ta ainahi ta ɗage ta sama ƙafafu na harbe_harbe.

Tsabar azaba Hajiya Murja ta ainahi Sumewa tayi, jabun Murja kuwa rikiɗewa tayi tare da komawa sak Hibba.

Tintsirewa da dariya tayi tare da kallon mahaifiyar tata dake kwance a sume, "wannan duk somin tabi ne kika fara gani muje zuwa in dai nice."
Hibba ta ƙarasa maganar tare da bacewa 6at.

Sanyin ruwan da aka zuba mata ne yasa ta miƙewa a rikice tana dube_dube ganin Abban
```

Hibba kusa da ita yasa jero mata sannu domin a yanayin daya isketa ya tabbatar ba lafiya.

"Umman Hibba."
Mahaifin Hibba ya kira sunanta.

A hankali ta ɗago da fuskarta dake zubar da hawaye.

"Yau ina so muyi magana ta gaskiya, ki faɗa mani miye ainahin damuwar ki nayi maki alkawarin nema maki magani aduk inda yake  a fadin duniyar nan domin na lura kamar matsalar ki naso ta fara tabo kwalwar ki."
Abban Hibba ya ƙarasa maganar tare da kafe ta da ido.

"Mi kake so in ce maka? Ya kake so inyi da rayuwata, kana ɗauka ta a matsayin maƙaryaciya mai yima ɗiyar ka ƙage, ka kasa fahimtar irin azabar da nike sha a cikin gidan nan, irin azabar da Hibba ke gallaza mani a gidan nan na fara tunanin anya Hibba mutum ce domim tunda tazo duniya har yau cikin cin azabar ta nike."

"Ya isheki!."
Mahaifin Hibba ya kwatsa mata tsawa.

"Shin Murja sau nawa nike maki gargadi akan canfa mani ɗiya da kike yi, to wannan ya zama na ƙarshe in ba haka ma Murja zani ɗauki mummunan mataki a kanki."
Abban Hibba ya ƙarasa maganar a matuƙar fusace.

"Kayi duk abinda zakayi wallahi na gaji da abinda kake mani a cikin gidan nan, kasani cewa nima uwace kuma ni na haifi Hibba bani taba yi mata ƙage ko kuma sharri, amma tunda haka kace Ubangiji yasan ya ta juyo kanka ta riƙa azabtar da ruhinka kamar yadda take azabtar da nawa."
Hajiya murja ta karasa maganar cikin zallar bacin rai tayi daki da gudu tana mai fashewa da kuka.

Galala! Ya saki baki yana kallon Murja da tunda take ko cacar bako bata iya yi dashi amma yau ita ce ke gaya ma shi maganganu haka, anya bazai yarda da maganar Murja ba kuwa."
Wata zuciyar ce tayi saurin kwabar shi.
"Ɗiyar ka mutum ce kada ka sake wasu camfe_canfen Hausawa susa ka fara zargin yar lelen ka.
Watsar da zancen yayi tare da nufar ɗakin Hibba domin tunda ya dawo bai haɗa ido da ita ba.

Kofar ya tura tare da kutsakai cikin ɗakin amma wayam babu Hibba, Toilet ya tura nan ma wayam, mamaki yahau yi ina Hibba zata je har haka basu sani ba? Maganar shi ce ta maƙale

sakamakon hango hibba da yayi kwance bisa gadon ta tamai ƙure da ido, wata firgita da kuma rikicewa yayi ganin ai yanzu ya bincike ɗakin amma ba Hibba, to ta ina ta shigo? tsabar mamakin da yake ne ya hanashi magana.

"Ni fa Abba kana shiga gona ta da yawa, yanzu daka iske ni a yana yin rikiɗa da kwanan ka sun ƙare."
Cewar hibba cikin tsawa_tsawa.

"Kinci gidanku Hibba bani son sakarci daga ina kike."
Cewar Abbanta.

"Daga sama nike ko akwai abinda Zanyi maka ne."?

"Daga sama kuma Hibba."?
Abban ta ya tambaya.

"Bani son tambayoyi , kaga dai bani shiga gonarka a gidan nan to wallahi kada kayi kuskuren shiga gonata bani son tambayoyi, ina ɗaga maka ne a gidan nan saboda babu hannunta ga abinda aka aikata mani tun kafin in zo duniya."
Ta karasa maganar tare da juyama Abban nata baya.

Ganin waɗan nan maganganu da take ma shi sam ya kasa gane inda suka dosa fitowa yayi daga ɗakin jiki a sanyaye.
"Mi Hibba ke Nufi da batun babu hannuna acikinn abinda akayi mata, to mi aka yima Hibba da ta kasa yafewa."
Nan fa zuciyar shi ta shiga yi mashi saƙe_saƙen abubuwa da dama.

Watsar da maganar yayi tare da kama aikin dake gabanshi wato na rarrashin Hajiya Murja domin yasan yau yakai maƙura wurin bata mata rai.

Da kyar ya shawo kanta tare da alƙawarin ya dena mata magana makamanciyar wannan.

Yau Abban Hibba ne maganar Hibba ta tsaya mawa a zuciya harta hana shi bacci sai juyi yake , shawara ya yanke kawai yaje ɗakin Hibba yaga mi take 6oyewa.

Cikin sanɗa yake takawa har ya kusa shiga ɗakin sai wata zuciya tace kada ya shiga, amma irin zakuwar da yayi na ganin mi yar lelen tashi ke boyewa, cikin sa'a yana tura ƙofar yaji ta buɗe kanta.

Ida shigewa kawai yayi, caraf idanun shi suka sauka akan abinda ya sanya shi sakin wani

guntun fitsari a firgice yayi baya zai gudu,amma kafin ya kai ga aikata haka ji yayi an fizgoshi an watsa cikin ɗakin, ƙofar ta rufe kanta da ƙarfi...

---

...Rikewa Leemcy tayi tare da nufar ƙofar tana bugu tare da ƙoƙarin buɗe ta amma sam ta kasa bude ta.

Lubna kuwa wani Kurnani kawai take ta Na harbe_harbe tana ƙoƙarin miƙewa tsaye, tamkar yunwataccen zaki haka Lubna tayo kan Leemcy tare da kwaso ƙafafunta ta shiga buga ta da ƙasa, ihu Leemcy take domin ko azabar da Uwar Aljanu ta bata bata taba basu irin wannan ba, jefata tayi jikin bango ji kake ƙum!

Wani wahalallen ihu ta saki tana ƙoƙarin miƙewa ta gudu amma kafin ta kai ga aikata haka Lubna ta shaƙeta tare da kaimata yakushi da ɗayan hannun, tsabar azaba Leemcy idanunta kakkafewa suka yi ta sume, sakin ta Lubna tayi tare da nufar ƙofa tana wami gurnani tare da ficewa a guje.

Turus! Lubna ta tsaya bata kaiga ficewa ba sakamakon Uwar Garke data gani zaune cikin falon.

Tamkar guguwa haka Uwar Garke ta bayya gaban Lubna.
"Hatsabibi mai matuƙar haɗari, a tunaninka zani taba bari ka gudu da Lubna ne."
Cewar Uwar Garke tana mai watsa ma shi mugun kallo.

Wata mahaukaciyar dariya mai kama da saukar aradu Lubna ta ɓarke da ita, lokaci ɗaya kuma ta turbune fuska.
"Haƙiƙa Kina shiga sabgar da ba taki ba, shin kin manta waye ni ko kin manta zalincin da akayi mani har na dawwama jikin Lubna to ki sani yau zani gudu da Lubna a gaban idonki kuma kikayi kuskuren hanani nayi maki alƙawarin shayar dake mamaki."
Hibba ta faɗa a cikin Muryar maza.

Kyalkyacewa da dariya Uwar Garke tayi har tana faduwa kasa tana mulmula tamkar kwallo kafin ta miƙe tare da Nuna Hibba da yatsa.

"Ruwa ba sa'ar kwando bane haka ko kura ta lalace ta fi ƙarfin karunuka su kawo mata raini, batun yau ba ka sanni nasan ka, a baya ma Ni ce nayi sake ka shiga jikin yarinyar nan dan haka yanzu ƙaryar ka tasha ƙarya bazaka sake taku ɗaya ba da gangar jikin Lubna."
Cewar Uwar Garke.

"Ni ruwa ne in na taho babu mai tare mani hanka koda ace ka tare mani hanya tabbas zani bi ta kanka in wuce, saboda haka yanzu a gaban idonki zan tafi da Lubna tafiya ta har abada babu bil'adam ɗin da zai sake ganinta idan kina gani ke hatsabibiya ce ki hanani barin gidan nan da Lubna."

Uwar Garke kuwa ganin da Gaske Zai iya guduwa da Lubna ya sa ta saurin shammatar shi ta danƙi kanshi tare da sanya mashi wani farin hayaƙi, kururuwa Lubna ta hauyi sannan ta sulale ƙasa.

Daf da kanta Uwar Garke ta matso tare da kallon Lubna dake kwance cikin halin suma.
"Rayuwar ki ta fara ne da ƙalubale tun daga ranar da kika shigo duniya a yanzu ke ba mallakar mutum bace ke mallakin hatsabibin Aljani ce, amma nayi maki alƙawari zani taimakeki duk da addininmu bai kasance ɗaya ba ni mai bada rayuwata ce domin taki, nayi maki alƙawari komi ya kusa zuwa ƙarshe."
Tana ƙarasa maganar ta sungumi Lubna ta kwantar da ita bisa gadon ta, Uwar Garke ɗakin ta kalla ganin yadda Lubma ta farfasa glass nuni Uwar Garke tayi da hannun ta sai ga komi yana komawa yadda yake hatta waɗan da suka farfashe sai gasu suna haɗewa su koma yadda suke.

Sai yanzu Uwar Garke ta lura da Leemcy dake gefen gado a yashe, kecewa da dariya tayi domin tasan koba komi yau Leemcy ta daku a hannun Lubna.

Wani wawan Mari Uwar Garke ta sauke ma Leemcy dake kwance, a gigice Leemcy ta miƙe tana dube_dube domin a zaton ta Lubna ce ke sake jibgar ta.

Jariri ta gani gefen ta ya wangale baki yana mata dariya, wata iriyar zabura Leemcy tayi tare da miƙewa zata gudu, caraf taji Jinjirin ya riƙe mata kafa.
"Uwata ina zaki baki ɗauki ɗanki ba."
Jaririn ya faɗa yana 6angara dariya.

"Na shiga tara ni Halimatu ina na samo jariri da ganinshi ɗan Aljanune."
Ƙoƙarin yakice jinjirin take amma ta kasa.

Fashewa tayi da kuka ganin wannan azaba biyu da aka haɗe mata lokaci ɗaya ga zafin dukan da ta sha hannun Lubna ga kuma wannan nataccen jinjiri dake kiranta Uwata.

"Dan uwar ka dan Ubanka ka sake ni ni duk lalacewa ta bantaba yadda na haihu ba , yau ni ina ganin lalataccen Aljani."
Falau_falau aka shiga ɗauke Leemcy da mari dama da haggu.

Wata mahaukaciyar tsawa aka daka mata, a zarane ta juyo amma wayam bata ga kowa ba.

"Zaki ɗauke ni ko sai an saba maki kamanni."
Jinjirin ya faɗa.

A gigice Leemcy ta rarumi yaron ta buga da bango, memakon jinjirin ya tarwatse koya karairaye sai ma gani Leemcy tayi ya miƙe da ƙafafunshi tare da zabgowa da gudu zuwa inda take, a

firgice ta bar dakin aguje jinjirin na take mata baya.

Ƙofar ɗakinta ta mai do ta rufe da ƙarfi tare da nufar gado ta faɗa, halbar da ita taji anji tayo ƙasa babu shiri.

Uwar Garke ce ta miƙe daga saman gadon tana mai yin miƙa, mutuwar tsaye Leemcy tayi domin tasan yau jikinta sai ya dare saboda dukan da zata sha.

"Eyye! Uwar Gantali daga ina kike kika tafi kika bar ɗaki tun ɗazu."
Uwar Garke ta faɗa tana mai bayyana a gaban Leemcy.

"Uwa mai daraja tuba nike daga ɗakin yar uwata Lubna nike."
Leemcy ta faɗa jiki na kyarma.

Kecewa da dariya Uwar Garke tayi.
"Ƙarya kike ce mani zakiyi kinje  ganij kwaf, daga yau ko ƙofar ɗakinta kika sake shiga sai kinji a jikin ki, yanzu ma ba kyaleki zanyi ba, kin taɓa yima ƙadangare tawai."?
Uwar Garke ta jefama Leemcy tambayar.

"Yau ni na lalace, wallahi ko a tatsuniya bantaba ganin wanda yayima ƙadangare tawaii ba."
Leemcy ta fada hawaye nabin fuskar ta.

"Yau kuwa zaki ga yadda ake ma shi, maza ɗauki wancan Ƙadangare kiyi mashi tawaii in ba haka ba zaki yima zaki brush yanzu."
Leemcy jin wannan jawabi na Uwar Garke yasa ta kai hannu tare da ɗaukar danƙareren Jankwataki ta fara mashi tawaii.

Ihu take tana rufe idon ta domin Ƙadangaren lafta mata cizo yake a hannu gashi kuma Uwar Garke tayi mata kashedin indai ta bari Ƙadangaren ya faɗi jikinta ne zai gaya mata.

Leemcy taga rayuwa, domin tasha cizo ba kaɗan ba ga azabar Uwar Garke dake gefe.

Sai gaf da magriba Uwar Garke tabar ɗakin Leemcy.
Fashewa da kuka Leemcy tayi.
"Allah ya tsine maki Lubna ashe ke dangin Aljanu ce , yau anyi mani bugun da tunda nike babu wanda ya taba yiman irin shi, wayyo baya na zai karye.

Shigowar Al'ameen gidan ce ta sanya Leemcy haɗiye kukan ta domin Uwar Garke tayi mata worning in ta sake wani ya gane halin da take ciki sai jikin ta ya gaya mata.
"Lafiya Leemcy nike jiyo kukan ki tun daga falo."
Cewar Al'ameen dake gefe kaɗan da ita.

"Ba kuka bane dariya ce ni haka nike."
Cewar Leemcy dake danne kwallan dake ƙoƙarin kufce mata.

Galala Ya saki baki yana kallonta.
"Ni kike gayama baƙar magana, in jiyo kukan ki kice kuma wai dariya kike."

"Dan Allah ka rabu dani bani son jaraba."
Leemcy ta karasa maganar tare da ɗan gyasa ƙafar ta kamar gurguwa zata shiga Toilet, ta6arr! Leemcy ta gurɗe ƙafa ta faɗi.

Mi Al'ameen zai yi ba dariya ba,Leemcy kuwa a fusace ta rarrafa ta shige Toilet ɗin.

Al'ameen samun kanshi yayi dason ganin halin da Lubna ke ciki domin in basu tare yafi jin wani abu a kanta amma muddun ya ganta ji yake kamar ya kashe ta, miƙewa yayi tare da nufar ɗakin Lubna.

Buɗe yaga ƙofar dan haka afkawa yayi ɗakin.

Wani ƙamshi wanda bai ta6a shaƙar irin shi bane ya daki hancin shi ba shiri ya karasa shigewa cikin ɗakin.

(🙌🏻😂 Niko nace gyaran ɗakin Aljanu daban dana bil'adama, duk mai buƙatar irin wagga gyaran ɗaki tazo muyi ciniki Uwar Garke kullum a online take tana jira)

Ƙare mata kallo yake tsaf sai yanzu ya fahimci wani abu, Lubna tafi Leemcy jiki mai kyau ga kuma diri mai ɗaukar hankali, wani tsoki yaja daya tuna Lubna baƙar fata ce.

Zama yayi gefen Gadon tare da kafe Lubna da kallo, ji yati babu abinda yake da buƙatar gani kamar Rabin fuskar Lubna dake Lullube kullu yau'mun, a hankali ya fara janye gyalen da ta rufe fuskar ta dashi, cikin bacci Lubna taga wannan namijin daya saba zuwar mata yana gyalgyata dariya tare da faɗar.
"Muddun kika bari Al'ameen yaga fuskar nan bazai ƙara ko minti daya a raye ba."
A firgice ta farka tare da fizge gyalenta tana me ƙara boye fuskar ta.

Wani kallo ya watsa mata.
"Kee! Ni tsaran wasan ki ne, wannan munafukar fuskar da kike 6oyewa ita nike son gani yau."

A firgice ta kalle shi.
"ba zani bari ka mutu ba, in kaga fuskata mutuwa zaka yi."
Ta ƙarasa maganar tare da ƙoƙarin barin ɗakin.

A matuƙar fusace Al'ameen ya miƙe tare da  fizgo....

Shin mi Al'ameen ya fizgo?

Zai mutu ko kuma Lubna ce zata mutu?🥱🥱🥱🥱

Muje zuwa🚶‍♀️🚶‍♀️🚶‍♀️

*MEEN@T...✍🏻*
[8/13, 6:34 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE3️⃣0️⃣_3️⃣1️⃣*
....Buguwar da Mahaifin Hibba yayi ce ta haddasa mashi dafe kanshi dake ƙoƙarin tarwatsewa.

Dishi_dishi idanunshi suka fara gani, da kyar ya miƙe yana laluben hanyar fita domin tseratar da rayuwar shi.

"Kada ma kayi ƙoƙarin guduwa Abba, yau abinda ka jima kana ƙaryatawa gashi a zahiri zaka gane ma idonka, abinda kake kira camfi yau zaka gane zahiri ne ba camfi ba ne."
Cewar Hibba tana ƙoƙari shaƙar wuyan mahaifin nata.

Jikn shi ne ya fara kyarma lokaci ɗaya wani gumi ya shiga wanke mashi jiki.
```

"Hibba! Nasan bake bace canza mani Hibbata akayi dan Allah ki fiddo mani ɗiyata kada ki cutar mani da Hibba."
Mahaifin Hibba ya ƙarasa maganar jiki na mazari.

Tuntsirewa tayi da mahaukaciyar dariya
"Kayi kuskuren shigowa ɗakina a dai_dai wannan lokacin zani raga maka ne saboda kai babu hannunka a cikin cutar dani da akayi, amma duk da haka yau sai ka yaba ma aya zaƙin ta daga yau ba zaka sake ƙaryatawa akwai aljani ba."
Hibba ta ƙarasa maganar tare da dage mahaifinta sama yana wutsilniya.

Ihu ya shiga zabgawa yana kururuwa ko Hajiya zata jishi ta kawo mashi ɗauki amma shuru kake ji.

Sakin shi tayi ya faɗo ƙasa tim tumbinshi ya bugu da tyles ɗis dake cikin ɗakin.
"Na rantse da Allah daga yau bani sake ƙaryatawa akwai Aljani Hibba kiyi mani rai nifa mahaifinki ne, wayyo tumbina."
Ya ƙarasa maganar tare da dafe cikin shi.

"Yi mani shuru! Daga yau in ka ƙara shiga harka ta sai jikinka ya gaya maka ba zaka ji da sauƙi ba ka daina gani ka na matsayin mahaifina ba wuya in murɗe maka kai sai dai a tarar kayi mussai."
Hibba ta faɗa da wata mummunar murya.

Kecewa da dariya Hibba tayi tare da nuna Mahaifinta da hannu sai gashi iska tayi sama dashi ana juya shi tamkar waina a tanda.

Ganin yadda ake hajijiya dashi ya sa shi fashewa da kuka yana kururuwar Hajiya ta kawo mashi dauki, iyakar galabaituwa Yayi ta sai da idanunshi suka fara gano dishi_dishi kafin suyo ƙasa dashi.

Nan ya baje yana nishin wahala domin yau ya fidda rai da sake rayuwa, har ya hango ta yadda Hibba zata gama dashi, ashe dama haka Hajiya keji amma yake ƙaryata ta yake katseta aduk lokacin da ta fara mashi bayanin halin da take samun kanta, Allah sarki ashe Aljanu shegune sai yau ya tabbatar da haka, inda ya samu ya kubuta daga hannun Hibba motar gida Zoo zai dauko a kwashi Hibba domin ta zama halitta abin tsoro ga bil'adama.

Tsawar da Hibba ta daka matace ta haddasa mashi dakatar da tunanin da yake.
"Wannan ya zama na ƙarshe da zaka shiga harkata ina kaunar ka shiyasa ma kaga na yi maka hukunci mai sauki amma karka bari muyi haɗuwa ta biyu dakai tashi fice mani a ɗaki kafin insa ayi maka rakiya."
Da gudu ya 6a66aka ya fice a ɗakin tare da bi ta sakan Mahaifitar Hibba yana ƙoƙarin shigewa

bayan gadon amma tumbin shi ya maƙale, a firgice ita ma hajiyar ta miƙe tare da barin gadon ta buɗe toilet ta shige tare da maido kofa ta rufe.

Ta ɗauki lokaci mai tsayi a cikin Toilet ɗin kafin ta buɗe ta fito tana rarraba ido.
"Abban Hibba lafiya ka kusa latse mani yan hanji ka kai ni lahira ban shirya ba, wai dan Allah mima ya faru ina kaje cikin daren nan."?
Cewar Mahaifiyar Hibba tana kafe shi da ido.

"Ke ar! Kina nan kina baccin asara ana can za'a kashe maki miji, anya Murja kina neman Aljanna kuwa? Ace ina can ana neman halaka ni kina nan kin saki leɓe kina bacci."
Abban Hibba ya fada a ƙule.

"Alhaji nifa ka sanya ni a duhu miya faru haka na ganka a birkice bangane inda maganganunka suka dosa ba."
Hajiya Murja ta ƙarasa maganar cikin ruɗu.

"To yau dai kaɗan ta hana Hibba ta kasheni wahalar duniya yau nashata ba kaɗan ba ashe abinda kike faɗa mani gaskiya ne ban yarda ba sai yau."
Abban Hibba ya karasa maganar yana mai saurin kallon ƙofa.

Murmushine ya Kubcema  Hajiya Murja ganin yau shima da gani ya faɗa hannun Hibba.

"Ayyo! Murja ni kike ma dariya, Murja Mijin Sunna kikema dariya lallai Murja."

"Yi hakuri Alhaji ba dariya nike ba jimami ne nike tayaka."
Ta karasa maganar tare da gumtse dariyar dake neman kubce mata.

"Na yanke shawarar Gobe gidan Zoo zamu kai Hibba domin wannan yarinyar ba mutum bace, barin ta cikin mu ba karamin haɗari bane ga rayuwar mu."

A firgice Hajiya Murja ta kalli mahaifin Hibba.
"Alhaji gidan Zoo fa kace?, yanzu ɗiyar mu zamu kai gidan zoo kamar wata dabba, Alhaji kamata yayi fa mu nemi malamai ayima Hibba magani."
Cewar Mahaifiyar Hibba.

"Eh to sai mu nemo malamai ayi mata magani amma ni yanzu tsoro take bani, na tsorata da Hibba."
Cewar Alhaji.

"Yanzu ka kwanta ka koma bacci kafin gari ya waye mu bazama neman malamin addini ko

zamu dace."

"Ni zani koma bacci murja! Kice so kike Hibba ta la6a6o ta karni, to bazani kwanta ba kedai in kina kwanciya ki kwanta."

Ganin Abban Hibba a tsorace yake bazai kwanta ba ita kwanciyar ta tayi, mahaifin Hibba kuwa yadda yaga rana haka yaga dare, safiya nayi yafice neman malami.

Haj murja na kitchen wurin haɗa breakfast mahaifinta yayi mata 5 miss call, tana ganin wannan kira tasan ba lafiya dan haka kiranshi tayi domin jin mike faruwa, abinda ya sanar da ita ya sata sakin cup ɗin Tea dake hannunta ya fadi ƙasa ya tarwatse a guje ta dauki gyalenta da key ɗin mota ta bar gidatamkar zata tashi sama...

---

...Fizgota yayi yana ƙoƙarin janye gyalen da ya rufe mata fuska.

Tsoron Lubna bai wuce ganin fuskar ta da Al'ameen ke ƙoƙarin yi ba, bata an kara ba taji ta wanke Al'ameen da wani mahaukacin mari, wasu taurari Al'ameen ya gani suna yi mashi shawagi cikin idon kafin duhun daya rufe mashi ido ya fara yayewa.

Dafe kumci yayi cike da zallar mamakin shine yau mace ta ɗaga hannu tare da ɗauke shi da mari lallai yau in bai ɗauki mataki akan wannan yarinyar ba tabbas bai cika Al'ameen ba, Lubna kuwa kuka ta fashe dashi tare da zubewa akan guiwowinta domin harga Allah tasan bata marin Al'ameen ba kaf duniya bata iya ɗaga hannu ta mari wani ba re kuma mijinta na sunna da take matuƙar ƙauna.

A matuƙar fusace Al'ameen ya fice daga ɗakin yana dube_dube, Lubna kuwa kuka ta fashe dashi tana tunanin irin abinda Al'ameen zai aikata a gareta yau.

Al'ameen kuwa yana fita ɗakin Leemcy ya shige tare da neman inda ya aje bindigar shi domin yau babu abinda zai hana shi harbe waccan halittar Al'ameen ya fada cike da zallar 6acin rai.

Jin maganar Al'ameen Leemcy tayi tamkar rugugin aradu, babu shiri ta duro da gurmuɗaɗɗiyar ƙafar ta da bata gama warkewa ba.

"Wallah ba zaka harbe taba ka haɗa mana bala'i da masifa da Uwar Garke, Al'ameen kana hauka zaka kashe Lubna kuwa."?
Cewar Leemcy tamkar zararriya tana tarbe hanyar da Al'ameen zai bi ya fice.

"Zaki bani hanya ko sai na fara harbe ki."
Al'ameen ya faɗa a matuƙar fusace.

"Wallahi sai dai ka Harbe ni, daka haddasa mani bala'in Uwar Garke ƙara in mutu ta hanyar Harbin bindiga da dai in mutu hannun Uwar Garke."
Ta ƙarasa maganar tare da riƙe ƙafar Al'ameen.

A matuƙar fusace Al'ameen ya harbar da Leemcy ta bugu da bango, duk da azabar zafin buguwar da tayi amma haka ta mike ta take mashi baya a guje.

Yana fitowa ya iske Lubna zaune tana kuka, kafin ya aunata da bindiga tuni Leemcy ta shiga tsakani tana ihu.

"Wallahi ƙarya kake, ba zaka ja mani baƙin bala'i wurin Uwar Garke ba, Al'ameen ka fara ta kaina kafin kaje wurin ɗayar minahikar, Lubna kin cuce ni kin kulla mani mummunar alaƙa tsakanina da Uwar Garke."
Ta karasa maganar hawaye nabin fuskarta ga majina da hawaye sun haɗe mata a fuska.

Lubna kuwa ganin bindiga tsirara a hannun Al'ameen kuka me sauti ta fara tana ƙoƙarin guduwa.

Al'ameen kuwa tsabar baƙin ciki auna Leemcy da bindiga yayi.
"Zaki kauce ko sai na tarwatsa maki kwalwa."?
Al'ameen ya fada cikin tsawa.

"Ba zani kauce ba, wayyo ni aure ya zame mani bala'i, Uwar garke Billahil azeem babu ruwa na wayyo Uwar Garke."
Leemcy ta shiga kurma ihu.

Fizgo Leemcy Yayi a fusace yashi wanka mata mari, duk da faduwar da tayi sai da ya bita har ƙasa ya shiga Bugu, ihun Leemcy kadai kake jiyowa cikin gidan.

Ganin irim bugun wulaƙancin da yake ma Leemcy a guje Lubna ta shige ɗaki ta kulle ita tana nata ihun tare da neman temakon jama'a.

Tun Leemcy na surfama Al'ameen zagi har bakin ya mutu murus, Bayan Lubna yabi a matuƙar fusace ga bindiga a hannu.

Bilal ne yayi sallama tare da shigowa falon, a firgice yayi kan Al'ameen dake ƙoƙarin karya ƙofar ɗakin Lubna.

Ga kuma Leemcy dake kwance kallo ɗaya zakai mata ka gane ta bugu.
"Mi kake koƙarin yi haka Al'ameen ko yan fashi ne suka ziyarci gidan naku, duba kaga Leemcy yadda ta bugu fuskarta duk ta fara kumburi."

Cewar Bilal

"Ka rabu dani yau duk sai sun gane kurensu, harni Lubna zata daga hannu ta wankama mari."
Al'ameen ya ƙarasa maganar jijiyoyin kanshi sunyi burɗin_burɗin.

"Mari fa kace."?
Bilil ya faɗa cike da zallar mamaki.

"Yau sai na harbe halittar can in yaso nima a kashe ni."

A razane Bilal ya rike bindigar yana roƙonshi yayi haƙuri kada ya biyema zuciya amma ina Al'ameen ya fusata da yawa.

Da kyar Bilal yayi nasarar amshe bindigar dake hannun Al'ameen.

Hakurin duniya ya bashi amma kamar ƙara tunzura shi ake, ganin Bilal zai kira su Hajiyar nan Al'ameen ya ce ya hakura amma sai ya sauke haushin shi kan Lubna dole ne ita ma jikinta ya gaya mata.

Leemcy kuwa ganin ita ma Allah ya kawo masu wani cikin gidan miƙewa tayi a guje ta faɗa daki ta kulle.

Juyin duniya sunyi amma sam Lubna taƙi ta buɗe ɗakin kukan ta kawai take tamkar ranta zai fita.

Lubna kuwa bata buɗe ɗaki ba sai bayan da Al'ameen ya tahi yima Bilal rakiya.

Falon ta zube tana maida numfashi domin yau ta azabtu da kukan da ta sha.

Ko kallon inda take baiyi ba haka ya tsallae ta ya shige ɗakin ta, Lubna kuwa alƙawari tayi koda zai yanka naman jikin ta sai ta sa me shi ta bashi haƙuri.

"Dan girman Allah kayi hakuri wallahi bani bace na mareka wannan ba halina bane, ka gafarta mani ba zani iya marin wani ba bare kuma kai."
Ganin irin kukan da take cizga tamkar ranta zai fita ya sashi kallon ta a fusace.

"Bani son renin wayo in baya ga Kin rena mani wayo ki daga hannu ki mareni yanzu kina fadar bake bace, mi kika mai da ni."?

"Bani bace."
Ta faɗa tana kuka tamkar zata shiɗe.
Ficewa yayi yabar mata ɗakin rai bace.

Sake fashewa tayi da kuka domin tasan wannan aikin na rabin fuskar ta ce, kecewa aka yi da dariya "Da sannu sai nayi sanadin rabuwarki da kowa domin ni bani yafiya bani afuwa."

Ɗif maganar ta tsaya lokaci ɗaya tamkar anyi ruwa an ɗauke.

A yanzu hawayen fuskar tama sun dena zuba sai dai ajiyar zuciya da take saukewa kawai.

A cikin yan kwanakin Lubna tasha azaba wurin Al'ameen tamkar ba gobe, bugu dai ba wani abu ba tasha shi tamkar zai kasheta, Leemcy kuwa ta tsorata domin yanzu ta gane wata aura dan haka yanzu takardar saki take nema ido rufe, ga babban abinda ke damun ta kawayen ta da har yanzu sun ƙi daukar wayarta ko ta kira su, wannan abu ba karamin tayar da hankalin Leemcy yayi ba, domin ita yanzu ta tsorata da lamarin Uwar Garke, bata da burin daya wuce Al'ameen ya sawwaƙe mata ta rabu da masifar da take ciki.

Hajiya Mariya kuwa zawo sai abinda yayi gaba, amma bata da burin daya wuce taje gidan Al'ameen ta aiwatar da aikin dake gabanta.

Ba karamin mamaki Hajiya Salima tayi ba jin mariya zata gidan Al'ameen,amma sanin zargi baida kyau kauda zargin da take tayi tare da yima Mariya fatan fatan dawowa lafiya.

Shigar Hajiya Mariya gidan Al'ameen ba ƙaramin mamaki tayi ba domin taga yadda Alhaji yayima ɗan lelen shi 6arin kuɗi ita kuma ɗiyar ta na can ta shiga duniya.

Ƙutawa tayi tare da fiddo maganin, ganin , Lubna ta shiga ta kawo mata ruwa maganinta ta fiddo tare da nufar ƙofar shigowa falon tasan dai dole in Al'ameen ya dawo zai tsallaka maganin.

Cike da farin ciki ganin ta aiwatar da aikinta ta miƙe zata koma mazaunin ta.

"Baki baɗa maganin da kyau ba domin can ga wuri can maganin bai je ba."
Hajiya murja taji wata murya ta faɗa.

A firgice ta juyo dan gane ma idonta me wannan murya, Uwar Garke ta gani rike da wani jibgegen Kulki tsaye gabanta.

Wani miyau Mariya ta haɗiya ji kake ƙuttt!  zawo ne ya kubcema Mariya ra6a6a yana bin kafafunta, ba shuri tayi zaman yan bori ta6ar!....

*MEEN@RT...✍🏻*[8/13, 6:37 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE3️⃣2️⃣ 3️⃣3️⃣*
...Gudu Hajiya Murja ke sheƙawa tamkar zata tashi sama, Ubangiji ne kawai ya kaita gidan mahaifin nata lafiya.

Ko parking bata gama yiba ta fito a guje ta afka gidan mahaifin nata, tamkar zautacciya haka ta hau neman shi tsakanin falo da kuma ɗaki, ganin ya fito a wani ɗaki ne ya sanya ta zubewa bisa guiwowinta tana mai da numfashi.

"Baba ashe babu abinda ya sameka, na tsorata matuƙa da abinda ka faɗa mani."
Ta ƙarasa maganar a firgice.

Matsowa yayi tare da zama gefenta.
"Murja gani na tsaye da kikayi da ƙafafuna ba shi bane tabbacin lafiyata lau, ki kwantar da hankalinki kiji abinda zani faɗa mani
"Murjanatu muna cikin gagarumin tashin hankali wanda a binciken da akayi mana asirinmu na gaf da tonuwa, bala'in dake tunkaro mu ba ƙarami bane, yanzu haka rayuwar mu na cikin garari, dama hausawa sunce abinda ka shuka shi zaka girba."
Alhaji Mamman ya ƙarasa maganar cikin karyayyar murja.

"Dama na sani Hibba ita ce ajalina, baba mutuwa zanyi Hibba sai ta kasheni."
Murja ka ƙarasa maganar tare da fashewa da kuka.

"Kiyi haƙuri yanzu haka Boka nacan ya dage aiki babu dare ba rana, kedai ki kiyayi haɗuwa da
```

Hibba cikin yan kwanakin nan."
Cewar Mahaifin nata.

Kasa magana tayi domin tasan kwanakin barin duniyar ta sune suka ƙaraso, mahaifinta ne ya katsema ta tunanin da take tare da miƙo mata yar ƙaramar laya

"Wannan ita ce ƙarshen magana, ki maƙalata a cikin gashin kanki kada ki kuskura ki rabu da ita duk rintsi."
Ya ƙarasa maganar tare da jaddada mata.

"Baba In ta faɗi mi zai iya samuna."
Cewar Hajiya Murja.

"Kada ma kiyi kuskuren bari ta faɗi domin in ta faɗi akwai gagarumar matsala."
Cewar Mahaifinta.

Jin yadda mahaifinta ke nanata akwai matsala cikin tsakiyar gashi ta tura layar, ganin mahaifin Hibba ya tafi nemo Malamin da zai yi mata rr
rukiya, ya sanyata yin bankwana da mahaifin nata.

Tafiya take amma sam hankalinta bai kan driving ɗin da take, Ubangiji ne kaɗai ya kaita gida lafiya, ko parking bata gama ba ganin motar Alhaji yasa ta fito tare da shigewa gidan da sauri.

Zaune ta ganshi shida wani mutumin da kallo ɗaya zakayi mashi ka shaida Malami ne ga dai wani rafkeken rawani a kanshi ya dage sai zazzare ido yake shiga malami.

Hajiya Murja ce ta ƙarasa wurin Alhaji.
"Wannan ne malamin."?
Hajiya Murja ta tambaya murya a ƙasa_ƙasa.

"Shine mana ko bai yi maki kama da malamai ba, to wannan da kike gani shahararren malami ne mai faɗa da duk wasu hatsabiban Aljani da suka gagara."
Cewar Alhaji.

Alama tayi ma Abban Hibba da suje ɗaki akwai magana, dan haka nan suka bar malamin cikin falo.

"Alhaji anya wannan malami ne? Ni fa ina ga kamar malam nan ne masu ci da addini masu karyar malumta alhalin suba malamai bane."
Cewar Hajiya Murja.

"Ki rufe mani baki!."
Abban Hibba ya faɗa a tsawace.

"Kin san iyakar wahalar da nasha kafin a haɗani da Gwari, ki fita idona in rufe bani son shirme, ina hibbar take ."
Ya ƙarasa maganar a fusace.

"Allah ya baka haƙuri, Yanzu na dawo gidan Hibba na can ɗakin ta kaje ka duba."

"Yanzu Murja ni zaki aika? In aikeki ki aike ni, maza kije ki kira Hibba kafin raina ya baci."

Jiki sukuku cike da zullumin shiga ɗakin Hibba Hajiya murja ta nufi kiran ta.

Malam gwani kuwa ganin haɗuwar wannan gida da tsaruwar shi ya sashi sakin baki yana kalle_kalle.
"Kuji fa inda kuɗin mu suke, aikam a kawo itama yar banzar yarinyar in same ta in zane raɗau domin ni nan ko cikakkiyar addu'a ban iyaba, yau dawa tayi nam gani zani samu kuɗi a sama."
Gwani ya ƙarasa maganar tare da gyara tanƙamemen rawaninshi.

Abban Hibba ne ya fito yana mai yima Malam Gwani sannu, babu jimawa sai ga Hibba ta fito tamkar mutuniyar kirki ta neme wuri gefen gwani ta zauna.

Abban hibba ne ya fara magana.
"Ya Malam ga marar lafiyar nan."
Cewar Abban Hibba.

Ɗaga kai Gwani yayi yana kallon Hibba.
"Keee! Ɗaga idonki ki kalle ni bani son sheɗanci ko kuma yanzu in saba maki kamanni domin in ana gaban mu biyayya ake."
Jin abinda Malam Gwani ya faɗa yasa Hibba sakin Wata Shu'umar dariya tare da Kallon Gwani.

"Alhaji wannan sheɗanun jikinta baƙaƙen ne aikin su akwai wahala amma kafin mu fara karatu da bugu zamu fara domin sai sun ji jiki zasu fita."
Gwani ya ƙarasa maganar tare da fiddo wata jibgegiyar dorina irin wadda dogarai ke bugun doki da ita.

"Ai indai zasu fita kada kaji komi ya shehi kaci gaba da aikin ka."
Abban Hibba ya faɗa yana gyara zama domin ganin yadda za'a cirema Hibba Aljanu.

Ganin zasu fara cire Aljannun Hajiya Murja ɗaki ta shige.

Karkace kai Gwani yayi tare da aje rawani gefe ya cire babbar riga itama ya ajiyeta gefe ya ɗauki zabgegiyar doriya ya nihi Hibba dake zaune ta ƙura mashi ido.

Iyakar ƙarfin shi ya ɗaga bulakar nan ya shiga sauketa a jikin Hibba ji kake taaaa!

A ƙalla yayi mata bulala takai Goma amma ko gezau bata yiba sai ƙura mashi ido da tayi tana murmushi.

Tamkar walƙiya haka Hibba ta fizge Bulalar dake hannun Gwani ta kece da wata mahaukaciyar dariyar data haddasama ɗakin girgiza, a guje Abban Hibba ya take ma Hajiya Murja baya suka maido ƙofa suka rufe.

Malam Gwani kuwa tsabar ruɗewa nan ya zube gaban Hibba yayi fiƙi_fiƙi da ido...

---

...Ta bangaren Malam Sule kuwa lafiya ta samu jikin shi tamkar bai taba wata rashin lafiya ba, sai dai bala'in Gaje da kullum ke ƙara gaba.

Zaune yake yana alwallar azahar zai fice masallaci, ganin Gaje tazo tayi mashi tsaye saman kai ya sashi ɗagowa tare da kallon ta.

"Lafiya kuwa Gaje zaki yi mani rumfa saman kai."?
Malam Sule ya ƙarasa maganar tare da ajiye Butar gefen shi.

"Lafiya babu ita ta bangarena bani tare da ita mai ita ma babu acikin gidan nan tun bayan barin waccan lalatacciyar ɗiyar a gidan nan."
Gaje ta karasa maganar tare da riƙe ƙugu tana jijjiga.

"Kul! Kika sake aibanta ɗiyata a gaban idona, domin naga ke har yanzu bakisan Annabi ya faku ba."

"Ai dole ka faɗi haka domin an gama shanyeka ka dauki ɗiya ka kai wama ya sani ko guduwa tayi ta shiga duniya aka fake da wai aure akayi mata."

"Aniyar ki ta biki Gaje Ubangiji bazai bar wannan bakin ya kama Lubna ba, ni bazani sake cewa kiyi hankali ba domin ita dunuyar nan da kike gani Gaje makaranta ce wanda bai zo bama jiran shi take."
Malam Sule ya ƙarasa maganar tare da nufar ƙofar gidan, saurin shan gabanshi Gaje tayi.
"Kaga ba fa zaka fita a gidan nan ba sai ka bani adireshin gidan da Lubna tayi aure domin nagaji da jiran ganin ta taƙi zuwa ni zani je in sa me ta."

"Bakida Hankali Gaje! Ni zani baki Address ɗin gidan Lubna, aikam da kin mutu bakije ba, domin zuwanki gidan ta babu alkhairi a ciki sai sharri."
Malam sule na gama maganar ya nihi hanyar fita.

A guje Kulu ta fito daga ɗaki tare dayin bakin maguji sai dai kafin ta ƙarasa bakin magujin aman ya kubce mata, tamkar zata amayar da abinda ke cikinta haka ta rika bulbula uban amai.

Malam Sule kuwa mutuwar tsaye yayi cike da tashin hankali, domin wannan shine karo na uku da kulu tayi amai a ranar.
"Ki shirya in na dawo masallaci muje asibiti."
Cewar Malam sule.

Bayan ya dawo masallaci har da Gaje aka shirya aka nufi Asibiti, da zuwan su tashin farko awon jini dana fitsari aka turasu suyo.

Ba'a bata lokaci ba result ya fito, dan haka iso likitan yayi masu dasu shigo ciki.

Likitan kallon Malam Sule yayi tare da girgiza kai cike da tashin hankali domin yaga shi a kamala ta mutane shiɗin da gani mutumin kirki ne, amma ya haka wannan result yazo a haka kodai ba result ɗin su bane aka kawo mashi.

Malam sule ne ya gaji da shurun da likitan yayi.
"Doctor babu dai matsala ko, kodai wani abu ne ya faru."?

Girgiza kai likitan yayi tare da miƙa mashi Result ɗin, jiki na kyarma Malam Sule ya buɗe result ɗin, a firgice ya saki takardar tare da furta "Innalillahi wa'inna ilaihirrajiun!"...

---

...Barkewa da dariya Uwar Garke tayi tare da nuna Mariya.
"Ko sharri yana da wakili, wato ke dai kin zama wakiliyar Sharri kin amsa sunanki taurarwa mai wutsiya ganinki ba alkhairi ba, duniya ba zata same maki ishara ba, mugun nufi kullum a cikin shi kike, Mugun halinki shi zai kai ki kabarin ki."
Uwar Garke ta karasa maganar tare da cafkar kwalar Mariya.

"Na tuba, daga yau bazan sake ba Uwar Garke ki gafarta mani ki yafe mani, wayyo Uwar Garke wannan kulkin na hannunki na minene."?
Cewar Hajiya Mariya a tsorace.

"Wannan kulkin da kike gani bana komi bane illa na bugunki yau zaki gane baki da wayo duk azabar da na baki a baya ta yau ta linka ta baya sau dubu dan haka maza kizo ki tsallake maganin nan kin san ance shi sharri ɗan aike ne yau gashi nan ya dawo kanki zaki girbi abinda kika shuka."

Uwar Garke na rufe baki ta shiga kwalfar Mariya da kulkin nan ta ko ina.

Ihun da Leemcy ta jiyo ne ya sanya ta fitowa domin a zaton ta Al'ameen ne ke jibgar Lubna, Uwar Garke da Leemcy ta gani ne ya sanyata jan wani burki daya haddasa mata faɗuwa ƙasa, ganin tashi ya gagareta a firgice da rarrafe ta koma ɗaki ta banko ƙofa.

Ba ƙaramin bugu ba Mariya tasha ga kuma magani data tsallaka babban baƙin cikin Mariya yanzu fa shikenan ita ce zata shiga duniya ba Al'ameen ba.

Dakatar da bugun Uwar Garke tayi tare da kallon Mariya
"Kin wahalar mani da hannu dan haka ki miƙe ki fara tsallen kwado."

Mariya da jikinta ya gama dakuwa a galabaice ta miƙe ta fara tsallen kwaɗo tana yi tana faɗuwa amma haka uwar garke ta tasa ta gaba sai da tayi shi.

Ganin Mariya ta zube yasa Uwar Garke kallonta.
"Maza ki tashi ki wanke zawon da kika bata masu falo dashi."

"Na shiga ukku yanzu Uwar Garke ba za'a yi mani gata a wanke mani zawo ba kamar yadda ake wanke ma wanda zawo ya baremawa, nice zani wanke da kaina."
Mariya ta karasa maganar tana layi.

Jin wannan magana ta mariya Uwar Garke dariya ta kece da ita.
"Ke zaki wanke kayan ki in kuma kina so ni nan zani wanke maki shi tas! Sannan kuma kashedi na ƙarshe kada ki kuskura kice wani abu ya faru dake a gidan Al'ameen, ko da yake ma ke lokacin shigarki duniya yayi domin kin rigada kin tsallaka maganin sai dai muce a shiga duniya lafiya."

Haka murja ta gyara falon tas tare da ficewa a guje ta nufi gida

Duk da ganin Hajiya mariya da mahaifiyar al'ameen tayi a rikice amma batayi tunanin wata matsala ba domin koda wasa Hajiya Mariya bata yi gigin sanar da wani halinda take ciki ba.

Kwana biyu da zuwan Murja gidan Al'ameen aka nemeta aka rasa hankalin Alhaji ba ƙaramin tashi yayi ba domin kuwa duk inda ake tunanin mariya an nemeta amma an rasa ta wasa_wasa sai ga shi an share mako ɗaya amma batare da an ga inda Mariya take ba ko wanda ya gantama ba'a samu ba.

Yau Al'ameen shida su Lubna suka shirya domin zuwa gida su jajantama Mahaifansu.

Hajiya Salima tayi matuƙar jin daɗin ganinsu mu musamman Lubna duk da dai taga alamun rama a tattare da ita, a daƙile Leemcy tayi ma mahaifiyar Al'ameen jaje domin yanzu ta tsani

auren Al'ameen domin ya takura mata yawon da take zuwa ma babu, gefa daya kuma ga bala'in Uwar Garke.

Umartar su Hajiya Salima tayi dasu je falon mahaifin Al'ameen su gaisheshi tare da yi mashi jaje.

Su ukun suka miƙe tare da nufar falon suna shiga suka iske mahaifin Al'ameen shida Alhaji Lamaru suna tattanauwa akan jami'an tsaron da aka baza neman Mariya.

Cikin ladabi Lubna ke gaidasu, da sauri Alhaji Lamaru ya ɗago kanshi tare da kallon Lubna, wani gumi ne ya shiga wanke mashi jiki duk da sanyi A.C dana fanka amma haka ya shiga firfita da hular dake kanshi.

Bayan fitar su ba jimawa Lamaru ya ce yana da wani abu na gaggawa daya taso mashi dan haka shima ficewa yayi.

Hajiya Salima kuwa ganin dare ya fara yasa ta kiran Al'ameen domin su tafi gida.

"Mommy dan Allah wurinki zani kwana kada kice in bishi mutafi dan Allah mommy."
Lubna ta faɗa tamkar zata yi kuka.

"Lubna da mijin ki amma kice wurina za ki kwana, kodai akwai abinda ke faruwa kada ki 6oye mani ki sanar dani."

"Mommy babu komi amma dan Allah nidai gidanki zani kwana."
Lubna ta fada kamar zatayi kuka

Ganin halinda Lubna ke ciki Umurtar Al'ameen tayi ya ɗauki Leemcy su tafi gida Lubna nan zata kwana.

Ko ajikin shi baiji komi ba haka ya dauki Leemcy suka tafi gida.

Ba ƙaramin daɗi Lubna taji ba domin koba komi tasan zata rage zaman kadaici tunda ga Momy kusa

Mahaifiyar Al'ameen bata bar ɗakin da Lubna ke ciki ba sai da ta tabbatar Lubna tayi barci, addu'a tayi mata tare da rufe ƙofa.

Koda gari ya waye hajiya Salima dai taga har rana ta fara Lubna bata zo ta gaida taba tasan akwai abinda ke faruwa, dan haka ɗakin Lubna ta nufa, abinda ya tayar mata da hankali bai

wuce yadda akayi ma ɗakin kaca_kaca an farfasa kayayyakin ɗakin an bata komi sannan kuma babu Lubna babu dalilinta a cikin ɗakin, a guje hajiya Salima ta nufi Toilet nan ma babu Lubna, mahaifin Al'ameen hankalinshi ba ƙaramin tashi yayinba ganin hajiya Mariya ta ɓata ga kuma Lubna ita ma an shigo har gida an sace ta.

"Innalillahi wa'inna ilaihirrajiun! Daddyn Al'ameen mike faruwa damu haka, Mariya ta bace ga Lubna kuma an shigo har gida ba tare da kowa ya farga ba an sace ta, innalillahi wa'inna ilaihirraji'un."
Hajiya Salima ta ƙarasa maganar numfashinta na ƙoƙarin ɗaukewa, ganin halin da take ciki yasa shi nufo ta amma kafin ya iso har ta sulale a ƙasa a sume...

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/15, 3:05 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE3️⃣4️⃣_3️⃣5️⃣*
...A rikice Mahaifin Al'ameen ya ɗaga waya tare da kisan family doctor, ba'a ɗauki lokaci ba sai ga shi ya iso.

Drip aka ɗaura ma hajiya tare dayi mata gargaɗin ta rage damuwa domin jinin ta na gaf da hawa.

Tun bayan tafiyar likitan Hajiya Salima kuka kawai take babu ƙaƙƙautawa, Mahaifin Al'ameen ne ya matso daf da ita.
```

"Salima Ba zaki dena wannan kukan ba haka, Kiyi haƙuri in shaa Allahu Lubna zata bayyana."
Ya ƙarasa maganar cikin damuwa domin shi kanshi al'amarin ya fara damun shi.

"Alhaji dole inyi kuka, Lubna tamkar amana take a wurina yanzu ya zamu ce ba mahaifinta wanda da hannunshi ya damƙa mani amanar Lubna innalillahi wa'inna ilaihirraji'un!."
Ta karasa magana wani sabon kuka na kubce mata.

Miƙewa yayi tare da ɗaukar waya ya kira Al'ameen, ba'afi mintuna sha biyar ba sai ga Al'ameen afujajan ya shigo ɗakin.

A rikice yake bin mahaifan nashi da kallo, gani halinda ya ga mahaifiyar shi ya sashi nufar ta da sauri.
"Mommy lafiya, Mommy mi ya same ki haka."?
Cewar Al'ameen a rikice.

Kasa magana tayi face hawayen dake bin fuskarta.
"Mommy dan Allah kiyi magana, mike faruwa ina cikin ruɗu ku duka kunyi shuru, na roƙe ku mommy kuyi magana."
Ya ƙarasa maganar a firgice.

"Al'ameen!"
Mommy ta kira sunan shi.

Kallon mahaifiyar tashi yake domin ya zaƙu yaji mi take son sanar dashi.

"Al'ameen komi kaga ya faru ga bawa ƙaddara ne ka dauki abinda zani faɗa maka a matsayin ƙaddara, Al'ameen Lubna ta 6ace an shigo har gida an sace ta mun nemeta sama ko ƙasa mun rasa."
Hajiya Salima ta ƙarasa maganar wani kukan na sake kubce mata.

Tamkar rugugin aradu haka haka Al'ameen yaji maganar mahaifiyar ta shi, lokaci ɗaya yaji kanshi yayi wata sarawa ba shiri ya sanya dukkan hannuwanshi biyu ya dafe hanshi, idanunshi ne suka fara ƙoƙarin rufewa
Lokaci ɗaya yaji wani abu daya danne ma shi girji ya yaye wani farin haske ne ya gilma ta idanunshi, daga nan ya yanke jiki ya faɗi.

A tare mahaifan nashi suka antayo da gudu tare da kiran sunan shi amma ina shuru kakeji, tamkar ƙaramin yaro haka mahaifinshi ya sungume shi ya nihi mota.

Hajiya Salima kuwa mantawa tayi da wani ciwo da take domin sawun giwa ya danne na raƙumi.

Ba karamin tashin hankali likitocin suka shiga ba domin harga Allah sudai basu taba ganin

Al'amari makaman cin wannan ba, abinda ke kara tayar masu da hankali shine yadda Numfashin Al'ameen na tafiya lafiya lau amma kuma yayi wata irin suma wadda duk wani ƙoƙari nasu amma sun kasa farfaɗo dashi.

Mahaifan Al'ameen dake tsaye bakin ƙofar ɗakin ganin yadda likitoci ke kai kawo wurin shiga ɗakin yasa hankalinsu kara tashi fatansu shine Allah yasa dai bamu rasa Al'ameen ba.

Fitowar Shugaban likitocin wato Doctor Yazeed ne yana yarfe gumi ya sasu mikewa cikin hanzari suna haɗa baki.
"Doctor ya tashi."?
Suka faɗa a tare.

Jinjina kai likitan yayi tare da Umurtar su dasu biyo shi Office, bayan shigawar su sun zauna bayani ya fara yi masu kamar haka:
"Yaron ku ba zamu ce komi akan shi ba sai dai muce ku dage da addu'a, domin a tsawon shekarun da nayi ban taba ganin an kawo majinyace a yanayin da kuka kawo ɗanku ba, gashi dai yana numfashi amma kuma a sume yake duk wani taimako da muke bayarwa mutum ya farka to mun ba ɗanku amma shuru kake ji, babban tashin hankalin mu shine kada ace yaron ku ya shiga Choma domin indai ya shiga choma cikin biyu za'ayi ɗaya kodai ya rasa tunanin shi (losing memorie) dan haka babu abinda zani ce maku sai dai ku dage da addu'a."
Likitan ya ƙarasa maganar shi tare da tattara wasu file dake gabanshi.

Kukan daya kumce mata ne yasa tayi saurin ficewa da gudu daga Office ɗin, take mata baya yayi.
"Dan Girman Allah Salima ki daina wannan kukan da kike, kina kara tayar mani da hankali ne, dami zanji ga ɓatan Lubna ga na Mariya ga kuma Al'ameen dake cikin mugun yanayi shima."
Mahaifin Al'ameen ya karasa maganar tamkar zai yi kuka.

"Alhaji muna cikin tashin hankali wanda Ubangiji ne kadai zai fidda mu."
Ka sa karasa maganar tayi sakamakon wani sabon kuka daya turniƙeta.

"Na sani Salima, amma addu'a ya kamata kiyi ba kuka ba, Yanzu ki kira Halimatu ki sanar da ita halinda Al'ameen yake ciki."

Da kyar ta iya ciro wayar ta tare da kiran Leemcy, nan ta sanar da ita kaf abubuwan dake faru.

Wani wawan tsalle Leemcy ta daka "ahayye Allah nagode maka dama Big boy yace mani ya shigo gari yanzu zani ci kare na babu babbaka."
Tana gama maganar ta shige toilet tare da fesa wanka tayi wata fitinanniyar shiga tamkar ba matar aure ba kai tsaye Gamji Hotel ta nufa inda Big Boy ke jiranta.

Mahaifiyar Al'ameen kuwa har yamma tana nan ta zuba ido amma Leemcy shuru.

Mahaifin Al'ameen kuwa tun bayan fitar shi yana wurin jami'an tsaro domin tsananta bincike ko Allah zai bayyar ma shi da matar ta shi da kuma sirikar shi, Malamai mahaifin Al'ameen ya samu akaci gaba da addu'o'i a masallatai babu ƙaƙƙautawa...

---

...Takardar Hannun Malam Sule ce ta kubce ta faɗi ƙasa, saurin tarbo malam Sule likitan yayi ganin yana ƙoƙarin zubewa ƙasa.

Kujera mafi kusa dasu Likitan ya zaunar dashi tare da jero mashi sannu, da ƙyar ya cira kanshi tare da kallon Kulu da ido ya rena fata
"Ranar da nike gudu yau gata nan tazo, Gaje kin cuceni kin lalata mani tarbiyyar ɗiya kin kunsa mani baƙin cikin da har in koma ma mahaliccina ba zai taba goguwa ba, innalillahi wa'inna ilaihirraji'un."
Mahaifin Lubna ya karasa magana tare da dafe kanshi.

"Bangane ba Malam! Ka fito fili kayi mani bayanin abinda ke faruwa ka tsaya sai wasu kauce_kauce kakeyi."
Gaje ta ƙarasa maganar cikin ɗaga murya.

"Ubangiji bai yin bacci kuma bai barim ayi zalumci, kinyi ma Lubna fatan lalacewa tayi cikin shege yau Gaje ga ɗiyarki mafi soyuwa nan da ciki na kimanin wata huɗu, bayan ciki yanzu haka tana ɗauke da cuta mai karya garkuwar jiki wato H.I.V."
Malam sule ya ƙarasa maganar cike da ƙunar zuciya.

Zaman yan bori Gaje tayi tare da fara kurma ihu, "Sule ka cuce ni ka ci amanata wayyo Allah na "
Ganin zata tara masu mutane yasa Likitan fara magana.

"Ki dawo cikin hankalinki, yanzu musan yadda zamuyi mu ceto rayuwar abinda ke cikin ta domin bata zo asibiti da wuri ba hakan yayi sanadin ɗan dake cikin ta shima ya kamu da cutar sakamakon ƙin bim dokoki domin da ace tazo asibiti hakan ba zata faru ba, yanzu abinda muke buƙata shine ku sanya hannu a barar da cikin nan domin haifar shi zata zama silar lalacewar rayuwar shi."
Likitan ya karasa magana tare da maida hankalij shi ga Malam Sule.

"Bazan ta6a bari a zubar da cikin nan ba, likita mungode, ku kuma maza ku tashi mu tafi gida."
Ya karasa maganar tare da miƙewa.

"Sule ya kake so ka tona mani asiri ga likita yace a zubar da cikin amma shine zaka ce mu tafi

gida, Sule ashe so kake mu zama abin nunawa ga jama'a."?
Gaje ta karasa maganar tana kuka.

"Ki zama abin nunawa dai! Domin ni Allah yana gani na ba Kulu tarbiyya kece kike rusheta dan haka Gaje wannan kaɗan ne daga sakamakon zalumcin da kika yima Lubna."
Yana kaiwa nan ya fice daga office ɗin.

Gaje da Kulu da suke faman darzar kuka bayan Malam sule suka bi.

Tun bayan isarsu gidan Malam sule ya shige ɗaki zuciyar shi tamkar ta faso ƙirji ta fito, "Allah ya na shedarshi ya bama Kulu tarbiyya irin wadda mahaifi ke ba ɗiyar shi amma haka yake gini Gaje na rushewa, har yau ga inda abin ya kai su, a yanzu yayi alƙawarin bayyana wani ƙullallen sirri da ya jima da boyewa dan haka cikin satin nan ya zama wajibi ya kwashi su Gaje suje Gidan Lubna domin warware wannan sirri.

Kulu kuwa ba cikin jikinta ke damunta ba face cuta me karya garkuwar jiki shikenan rayuwarta tazo ƙarshe, bata da wani amfani yanzu.

Gagarumar nadama ce ta ɗarsu a zuciyar Kulu, tare dajin kaunar mahaifinta domin yanzu ta fahimci shine masoyinta na gaskiya, maganar Gaje ce ta dawo da ita daga duniyar tunanin da ta lula.

"Ki tashi muje dole a zubar da cikin nan."
Gaje ta faɗa a tsawa ce.

"Wallahi babu inda zanje duk wa yayi sanadin shigata wannan halin in ba ke ba, nayi nadamar biye maki da nayi."
Kulu ta karasa maganar hawaye nabin fuskarta.

"Ai ni dama nasan za'a rina (an saci zanin mahaukaciya) wannan nataccen sairayin naki Gaye ni nasan dama zata kai ku ga haka, keda zaki samu mai kuɗi sai ki tsaya ga talaka yanzu ai gashi nan kin kwaso cuta dan haka dole kije a zubar da cikin nan."

"Koda wasa kika bari cikin nan ya zube a bakin auren ki."
Malam Sule dake fitowa daga ɗaki ya faɗa.

A matuƙar firgice Gaje ta dafe ƙirji jin wannan magana da Mahaifin Lubna ya furta...

---

...Gwani fiƙi_fiƙi da ido yayi domin yasan yau ƙaryar shi ta ƙare ya gamu da gamon shi.

"Na rokeki ɗiyar Albarka ki taimaka kada ki taba lafiyar jikina, nasan tsautsayi ne yasa na dan

dake ki amma ki bari yanzu zani fice a gidan nan kada ki taba ni kinji ɗiyar Albarka."
Cewar Malam Gwani dake faman rokonta.

Kecewa da dariya tayi tare da daka ma shi tsawa.
"Ƙarya kake kana cutar mutane alhalin kai malamin ƙarya ne ba kasan komi ba sai cutar mutane da malumtar karya, yau zaka san ka tabo wadda bata afuwa bare yafiya."
Cewar Hibba dake tsaye gabanshi da zabgegiyar Bulala.

"Wayyo ni gwamni na shiga Ukku yau kwaɗayi yasa na faɗa tarkon Aljana, na roƙeki anti Aljana kada ki bigeni, ance in Aljani yayi maka duka baka ƙara lafiya."
Cewar Gwani yana hawayen tsoro.

Hibba kuwa murtuke fuska tayi tare da fara zabgar Gwani iyakar ƙarfin ta, ihun gwani kawai ke tashi a cikin gidan tamkar zai tarwatsa dodon kunnen ka.

Su hajiya kuwa jin ihun Gwani ba ƙaramin sake fitgitar dasu yayi ba nan suka fara rige_rigen Shigewa cikin wadurof.

Sai da tayima gwani Lilis kafin ta, umurceshi ya kwashi babbar rigarshi da rawani ya ranta a na kare.

Jin shiru tayi yawa yasa suka fuskanci Hibba tabar wurin, kofa suka buɗe tare da firfitowa suna maida numfashi.

"Ya zama wajibi in nemo malami na haƙiƙa wanda zai rabamu da wannan bala'in, nifa na gaji domin gaf nike da barin ƙasar nan."
Cewar Abban Hibba yana maida numfashi.

"Tun farko sai da nace maka bai yi kama da Malamin gaskiya ba amma kayi kunnen Uwar shegu dani, gashi nan yanzu ka gamu da darasi ai."
Hajiya Murja ta fada.

"Wannan kuma ai ya wuce yanzu mu samu mu nemi malamin kwarai kawai domin na samu labarin wani babban malami a nan ƙasan mu kadan limamin juma'a ne, yanzu haka wurin shi zan wuce."

"Kayi sauri ka dawo domin ni kullum cikin fargaba nike."

Abban Hibba Ficewa yayi da sauri, Hajiya Murja kuwa ɗan kwalin dake kanta ya cire domin jikinta duk yayi zufa.

A firgice ta miƙe sakamakon layar ta dake bisa kanta data lalubo amma taji wayam, bayan kashedin da mahaifinta yayi mata na kada tayi kuskuren da layar nan zata faɗi yanzu kuma gashi taji wayam babu layar...

________________________________

...idanun ta da suka yi mata matuƙar nauyi ta fara ƙoƙarin buɗewa a hankali.

Ɗakin ta farabi da kallo domin ta tsorata matuƙa da yanayin ɗakin, idon ta ne ya sauka kan ƙafafunta dake ɗaure da wata kakkaurar sarƙa ƙafa da hannuwa, ko motsin kirki ta kasa.

A firgice Lubna takai duban ta ga ƙofar da taji ana ƙoƙarin buɗewa.

Namiji ne ya shigo ɗakin tare da sakar mata murmushi.

A matuƙar firgice Lubna ta kalleshi tare da fiddo ido Lokaci ɗaya bakinta ya fara kyarma amma duk da haka sai da tayi ƙoƙarin furtaa....

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/16, 11:13 AM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

________________________________

*PAGE3️⃣6️⃣ 3️⃣7️⃣*
...Da ƙyar Lubna ta janyo dogon numfashim ta furta: "Baba!"
Cikin wata irin murya me nuna zallar mamaki da aljabi.
```

Kecewa da dariya Alhaji Lamaru yayi tare da nuna Lubna.
"Kada kiyi mamakin gani na domin akan neman ki sai da na koma tamkar zautaccen mahaukaci, na kashe kuɗi na rasa abubuwa masu matuƙar amfanina wurina duk ta sanadin neman ki hatta mata ta sai da na sadaukar, dan haka wani mamaki da aljabi ya fita a ranki, yadda na wahala a samunki dole ne in aikata abinda na jima ina burin samu wato mulki."
Cewar Alhaji lamaru tare da tsayawa tsakiyar Kanta.

Banda kyarma babu abinda Jikin Lubna keyi, ga wani matsanancin ciwon kai daya yi mata dirar mikiya.

"Dan Allah ka fitar dani a wannan wurin, kada ka bari su cutar dani na roke ka."
Lubna ta ƙarasa maganar cikin mawuyacin hali.

Sake kecewa da dariya yayi cike da zallar farin cikin burin shi zai cika.
"In taimakeki kika ce Lubna? In taimake ki ni in tona ma kaina asiri, yadda kika shigo gidan nan mutuwa ce kaɗai zata fiddaki kima bar batama kanki lokaci wurin wata magiya da rokon na."

Kasa magana Lubna tayi sakamakon kanta da taji tamkar ana buga mata Guduma hawaye ne kaɗai ke ambaliya a fuskarta.

Wasu Jibga_jibgan Ƙarti ne suka shigo cikin ɗakin tare da sungumar Lubna tamkar sun ɗauki jinjiri.

Basu direta a ko ina ba sai gaban wani gabjejen Mushiriki wato Boka, ajeta keda wuya duk suka faɗi gaban Bokan suna kwasar Gaisuwa.

Duk inda kuke tunanin halitta mummuna da kallo ɗaya zakayi mata ba zaka kuma ba to Bokan ya wuce nan.

Fuska a tur6une Bokan ya kalli Lamaru
"Ka tabbatar kafin ku ɗauko ta  kun shaƙa mata maganin."?
Bokan ya faɗa da wata Jibgegiyar Murya.

"Mun shaƙa mata shiyasa ma kaji jikinta yayi sanyi ta kasa tabuka komi."
Cewar Lamaru dake Gurfane gaban Bokan.

Wata mahaukaciyar dariya Bokan ya kece da ita.
"Kun yi sa'a da kuka shaƙa mata maganin da ace kunyi kuskuren ɗaukota da kuwa tabbas babu wanda zai tsira a wannan wurin sai Aljanin jikinta ya hallaka kowa amma kunga yanzu nannauyan bacci yayi awon gaba dashi har mu gama aikin mu aikin mu."

Lubna dai idanunta ne kaɗai ke motsi domin ilahirin jikinta ya saki sai hawaye dake ta kai kawo

a kumatun ta.

Kanta ne yayi wata mummunar sarawa, wata irin zabura tayi tare da cije lips ɗinta a hankalin idanunta suka rufe jikinta kuma ya saki.

Wata shar6e6iyar wuƙa Bokan ya ɗauka tare da tunkarar Lubna domin yankon 6aren Fuskarta.

Tamkar yadda zare marar kwari ke katsewa haka Sarƙar dake jikin Lubna ta riƙa katsewa da kanta.

Hannu Bokan yakai da nufin Yaye gyalen daya rufe gefen Fuskar Lubna amma kafin ya kai ga haka wata iska ce me matuƙar ƙarfi ta dake shi sai gashi a ƙasa warwas.

A matuƙar Fusace Bokan ya ɗago da kanshi dan ganin wane me ƙarar kwanan na yayi ma shi abinda tunda yake babu wanda ya taba yi mashi, arba yayi da Uwar Garke Fuskar nan sam babu annuri ta bayya a mummunar suffarta.

"Kuskure na farko da kayi shine ƙoƙarin ta6a fuskar Lubna, duk da ban kasance Musulma ba amma rayuwa bata kamaci mushiriki irinka ba, ka halakar da al'umma da dama wanda kai kanka baka san adadin suba, amma yau komi yazo ƙarshe."
Cewar Uwar Garke dake Gaf da Lubna.

A wulaƙance Bokan ke kallon Uwar garke yana jifarta da kalli me nuna tsantsar reni.
"Yake wannan ƙanƙanuwar Aljana ki sani kinyi matuƙar Kuskuren bayyana gaban Hatsabibin Boka kamata ya zama wajibi a gareni da in koya maki hankali domin ya zama izina ga yan baya."
Yana rufe bakinshi yayi girgiza ya koma wani gabjejen dodo me matuƙar ban tsoro.

A guje yayo kan uwar Garke da mugun nufi, ita kuwa uwar garke ko motsawa bata yi ba daga inda take tsaye, yana isowa wurinta hannuwa biyu ta sanya tare da murɗe mashi wuya nan ya faɗi yana shure_shure rai yayi halinshi nan gawarshi ta kama da wuta ta ƙone ƙur'mus!

Sauran mabiya Bokan nan suka faɗi suna aman jini, Uwar Garke kuwa Juyowa tayi kan Alhaji Lamaru.

"Tir! Da hali irin naku, tun farkon rayuwata na taso ne da matuƙar ƙaunar addinin muslumci domin ganin yadda kuke gudanar da rayuwar ku, a hankali ƙarni bayan ƙarni na fara gane anahin halayen musulmi kune zuwa wajen boka duk abinda addininku ya hana kuna yi ban sake tabbatar da halinku ba sai da na gamu da Lubna lokacin da take jinjira an sadaukar da ita ga hatsabibin Aljani duk saboda abin duniya Tir! Da halayya irin taku."
Uwar Garke ta ƙarasa maganar a fusace.

Alhaji Lamar kuwa ganin yadda Uwar Garke tayi ma shugabansu ya sashi miƙewa da kyar

domin shima jin jikin shi yake tamkar ana hura ma shi wuta.

"Kada ki kasheni zani dauki Lubna in maidata ga mahaifanta lami lafiya ba tare da koda kwarzani ba."
Ya faɗa a matuƙar tsora ce.

"Ka haɗu da Uwar Garke ku rabu lafiya jikinka bai gaya maka ba, ai ƙarya kake."
Uwar garke ta ƙarasa maganar sai ga wata siririyar bulala ta bayyana a hannunta, abinda zai baka mamaki da Bulalar bawai siran tarantakar bace abin duba Aa sak bulalar kaifi gareta tamkar Reza.

Duk inda ta bugama Lamaru sai dai kaga fata ta dare jini ya hau malala .
Duk da Lamaru ba mutumin kirki bane amma kallo ɗaya zakai mashi ka fuskanci ya bugu.
Tsawa Uwar garke tayi tare da fara magana.

"Ka tashi ka ɗauki Lubna mu kaita gida muddun ka sake Lubna ta farka bamu ƙarasa gidaba jikin ka ne zai gaya maka."

Alhaji Lamaru daya gama galabaituwa da ƙyar ya cicci6a tare da ɗaukar Lubna ya saka a gidan baya Nan uwar Garke ta shi yaja mota suka tafi.

"Koda wasa idan kayi driven ɗin daya haddasa ma Lubna baccinta ya katse tabbas abinda nayi maka a baya somin ta6ine, kuma idan mukaje kai da kanka zaka bayar da lamarin abinda ya faru."
Cewar Uwar garke.

"An gama ranki shi daɗe Uwar Garke."
Alhaji lamaru ya faɗa jiki na kyarma.

Suna barin wurin Gidan Bokan ya kama da wuta.

---

...llahirin jikin Hajiya Murja rawa yake domin tasan yau kashinta ya bushe tunda layar nan ta kubce mata.

Ɗaki ta koma taci gaba da bincike tamkar zata yi hauka amma ko alamarta bata gani ba.

Ƙofar ɗakinta taji ta rufe kanta, da sauri Murja ta juyo dan ganema idonta abinda ke faruwa, Hibba ce ta shigo  fuskarta ɗauke da murmushi.
"Ko ba wannan abar kike nema ba."?
Hibba ta ƙarasa maganar tare da nuna ma mahaifiyar ta layar dake hannun ta.

Da kyar Hajiya Murja ta tattaro duk wata jarumtar ta tare da fara magana.
"Hibba mi nayi maki a rayuwa da kike son halaka ni,Hibba nice wadda ta haifeki tayi renonki."

"Na saniii!"
Hibba ta fada cikin tsawa.

"Baki can_canci rayuwa ba ki sani ni nan da kike gani baku yi mani adalci ba kun cuci rayuwata tun kafin zuwana duniya, yanzu haka maganar nan da nike maki Mahaifinki wanda dashi ne kuka haɗa baki aka cuceni yana can na baroshi cikin mawuyacin hali abu ne me matukar wahala ya rayu domin keda shi baku kamaci rayuwa ba, kun tarwatsa mani duk wani farin ciki nawa, kamar yadda Abba ya tafi kiran malami kafin ya dawo kema kwananki ya ƙare."
Tana kaiwa nan ta yima Hajiya Murja wata mummunar shaƙa.

Wani irin kakari ta shiga yi tamkar ranta zai fita lokaci ɗaya idanunta suka fara kakkafewa.

Kecewa da dariya Hibba tayi.
"Ba zani bari malamin nan ya iso ba domin yana zuwa ni nasan asirina ya tonu, kafin ya karaso na gama dake na bace daga duniyar mutane babu wanda zai sake gani na."
Tana rufe bakinta aka yima ƙofar dakin wani mahaukacin bugu sai ga ƙofar ta buɗe kanta.

Ihu Hibba ta fara sakamakon shigowar Malamin bakin shi ɗauke da addu'a, zafin da Hibba keji a jikinta ya sanya ta sakin Hajiya Murja itama ta faɗi tana ihu tare da harbe_harbe.

"Malam ka gani ko abinda na fada maka, da bamu karaso da wuri ba da tuni ta hallaka mahaifiyar ta."
Mahaifin Hibba ya ƙarasa maganar tare da miƙama Hajiya Murja ruwa tasha.

"Alhamdulillah tunda mun ƙaraso da wuri Ubangiji ya kawo abun da sauƙi."
Malam Saif ya karasa maganar tare da matsowa kusa da Hibba.

Kallo ɗaya yayi ma Hibba ya kauda kanshi tare da kallon mahaifan Hibba.
"Zan tambayeku amma ina so ku fada mani gaskiyar lamari, da gaske ku kuka haifeta ko kuma dai renonta kuke."?
Malam Saif ya fada domin gasgata abinda yake tunani.

"Mune nan muka haifeta."
Suka faɗa a tare.

"Innalillahi wa'inna ilahirraji'un."
Ita ce kalmar da malam Saif ya cigaba da maimaitawa cike da tashin hankalin abinda ya hango tattare da Hibba.

"Tabbas akwai abinda kuka aikata can baya a rayuwar ku domin al'amarin Hibba akwai rikitarwa."

Goshin Hibba ya dafe tare da karanto wata addu'a, lokaci daya ta fasa wata irin ƙara tare da komawa ta sume.

Wayar malamin ce ta hau ruri, yana cirota ya sunan wanda yayi kiran ya bayya jikin screen ɗin wayar.
"Alhaji Sufyan garkuwan marayu."
Da sauri Malam saif ya ɗauka tare da mikewa.

"Innalillahi wa'inna ilaihirrajiun!" shine abinda Malam Sufyan yaci gaba da nanatawa.

Kashe wayar yayi tare da kallon mahaifan Hibba.
"Kuyi haƙuri bazani iya karasa maku aikin nan ba amma kada ku yi kuskuren kunna wani abu daya danganci kiɗa a cikin gidan nan domin dai_dai yake da farkawar Hibba, wani aiki ne ya taso mani wanda ya zame mani wajibi in ƙarasa shi."
Malam saif ya faɗa yana ƙoƙarin barin ɗakin.

"Kada kayi mana haka, zani baka maƙudan kuɗaɗe indai ka tsaya ka ƙarasa mana aikin mu."
Mahaifin Hibba ya faɗa cikin hanzari.

Murmushi Malam Saif yayi tare da kallon mahaifin Hibba.
"Ban fara karatun ruƙiya domin in tara kuɗi ba, in ka lura ba abin alfahari ba ina da kuɗi dai_dai gwargwado kai shedane domin cikin motata muka shigo gidan ka, ALHAJI SUFYAN GARKUWAN TALAKA, mutum ne me matuƙar daraja a wurina mutum ne da shine sanadin zama na malami shine wanda ya fiddani har jami'an dake a madina nayo karatu, ya ginani na zama mutum, yanzu haka ɗanshi dake fama da rashin lafiya Al'ameen ya farka har an sallame su daga asibiti, suna gida ɗan yana wasu abubuwa na miss behaving, shin yanzu so kake mutumin daya yi mani wannan halarcin in ƙi zuwa gare shi a lokacin da yake neman taimako na."

Jikin Mahaifin Hibba sanyi yayi.
"Malam da Allah zani iya neman wata Alfarma a gareka."?
Mahaifin Hibba ya faɗa.

"In babu damuwa mu biku can gidan in ka gama yima ɗan nasu sai ka duba Hibba, wallahi Malam in ka barmu mu kaɗai tare da Hibba akwai gagarumar matsala."
Mahaifin Hibba ya karasa maganar cikin murya me ban tausayi.

Shuru Malam Saif yayi domin ya gano maganar Abban Hibba haka take, barin su da Hibba akwai gagarumar matsala, dan haka dukkan su suka rankaya suka nufi gidan su Al'ameen.

Al'ameen kuwa tun bayan daya farka yaga babu Lubna ya zama tamkar zararren mahaukaci duk wani kayan alatu dake cikin falon ya farfasa su.

Hajiya Salima kuwa ganin yadda tilon ɗanta ya zama tamkar mahaukaci wuri ta samu ta zauna wani kuka na kubce mata.

Motar su Uwar Garke ita ta fara tsayawa dan haka a guje Lamaru ya sungumi Lubna suka yi cikin gidan su Al'amee.

Suna shiga sai ga Motar Malam Saif shida mahaifan hibba sun shige gidan suma da Hanzari....

🚶🏻‍♀️🚶🏻‍♀️ AN KUSA FARA FAƊAN ƘARSHE, YANZU CHAKWAKIYAR ZATA FARA🚶🏻‍♀️ WADDA MUKA BARI BAYA TABBAS TA LAFTA MISSING

MUJE ZUWA🚶🏻‍♀️

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/18, 8:53 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE3️⃣8️⃣_3️⃣9️⃣*
...Suna shiga falon juyowar da Hajiya zatayi idonta ya sauka cikin na Lubna dake a halin suma riƙe a hannun Alhaji lamaru.

A guje Hajiya Salima ta kira sunan ta tare da jijjigata, Lubna da Al'ameen yaji an ambata ne ya sashi juyowa yayo kanta yana kiran sunan ta.
```

Cike da mamaki suke kallon Alhaji Lamaru da baƙuwar matar dake tsaye suna kallon_kallo.

Ruwa mahaifin Al'ameen ya shafama Lubna nan ta fara sauke ajiyar zuciya a hankali, mutanen dake cikin falon ta fara bi da kallo ɗaya bayan ɗaya tana sauke ajiyar zuciya, Al'ameen kuwa tamkar zai maida Lubna ciki wata irin ƙaunarta yaji ta ɗarsu a zuciyar shi.

Cike da mamaki Mahaifin Al'ameen ya kalli Alhaji Lamaru tare da furta.
"Sannu da ƙoƙari aminina nagode matuka da bayyanar Lubna ta dalilin ka, shin ina ka samota? Kuma ya naga jikin ka duk a jigace shin wani abu ya faru ne, kuma ina ka samo waccan matar."?
Cewar Mahaifin Al'ameen cike da ƙaguwar jin inda aka samo Lubna.

Fiƙi_fiƙi da ido Lamaru yayi yana satar kallon Uwar garke da ta rikiɗe ta koma matashiyar kace me matuƙar kyau da kwarjini a fuskar maza.

"Zaka yi bayani ko sai jikin ka ya gaya maka."?
Uwar Garke ta faɗa cikin tsawa.

In inar da Lamaru ya fara cike da tashin hankali, sallamar Malam Saif ce ta maida hankalin mutanen falon ga masu ƙoƙarin. Shigowa.

Tamkar wadda aka tsunkula haka Lubna ta mike tare da kurma wani ihu tana nuna Hibba da hannu, kafin ayi yunƙurin riƙo Lubna tuni Hibba da ke tsiƙe a hannun mahaifin ta takubce ta zundumo da gudu zuwa wurin Lubna.

Rungume juna suka yi cike da zallar farin ciki tare da sakin wata mahaukaciyar ƙara  data haddasama mutanen falon toshe kunnuwan su.

A fusace Al'ameen ya miƙe ganin Lubna ta rungume wani wanda ba shi ba, duk da mace ce Lubna ta Rungume amma zuciyar Al'ameen tamkar ta ƙone tsabar tafasa da take.

Yun ƙurawa Al'ameen yayi zai fizgo Lubna, da Sauri Malam Saif ya ruƙo hannun shi tare da girgiza mashi kai.

"Kada kayi gigin tabata domin waccan da kake gani ta rungume yau kimanin wasu shekaru rabonta da ita muddin kace zaka rabasu yau kwanan ka sun zo ƙarshe, wadda kake kani rungume da Lubna ba kowa bace face Al'jana!."

A firgice Mahaifin Hibba da Kuma Mahaifiyar ta suka ja da baya tare da furta;
"Malam Aljana fa kace."
Suka faɗa a tare.

Al'ameen kuwa daskarewa yayi domin ya rasa wannan wane irin rikitaccen Al'amari ne haka.

"Kwarai kuwa Aljana ce, hajiya ya kamata ku bayyana sirrin da kuke boyewa domin tunda kuka kirani inda haɗa ido da ɗiyarku nagano ba jinsin mu bace."
Malam Saif ya faɗa tare da kafe mahaifan Hibba da idon.

"Malam ni na haifi Hibba nina rene ta taya zaka ce mani Hibba ba mutum bace Aljana ce."
Hajiya Murja ta fada hawaye nabin fuskarta.

"Ƙarya kike makira munafika mara imani ki fadi gaskiya domin yau asirin kowa sai ya tonu babu boye_boye."
Uwar Garke ta faɗa a fusace fuskar ta fara sauyawa.

Nan fa kallo ya koma kan uwar Garke, murmushi malam Saif yayi tare da furta.
"Baiwar Allah miya shigo dake cikin bil'adama bayan kema tun bayan shigowata na fuskanci Jinnu ce."
Malam Saif ya ƙarasa maganar cikin tattausar Murya.

Wani wawan tsalle mahaifin hibba dake kusa da uwar Garke yayi ya dira bayan Malam Saif domin ya lura kila yau rabin mutanen falon Aljanune.

"Tabbas malam ni ba mutum bace ni Aljana ce, cikin Aljanun ma hatsabibiya wadda ko yan uwana shakkata suke, labarin nada tsayi amma ina so Hibba ta juyo ta kalli murja domin ta tunano abinda ya faru a shekaru ashirin da biyu da suka gabata."
Uwar Garke ta ƙarasa maganar tare da ƙalawa Lubna dake Rungume da Hibba har yanzu suna faman gurnani kira.

Juyowar da Lubna zatayi suka haɗa ido da mahaifiyar Hibba, Gaban Hajiya Murja ne yayi mummunar faɗuwa lokaci ɗaya jikinta ya fara ciri abubuwan da suka faru a shekaru ashin da biyu suka fara dawo mata cikin kwalwa tamkar yanzu abun ya faru, da kyar ta cira hannunta dake kyarma ta Nuna Lubna tare da sulalewa ƙasa sumammiya.

Duk wanda ke wurin tabbas kanshi ya ƙulle domin wannan al'amari ya matuƙar tayar da hankula, taro ya koma na Aljanu mutane se sumewa suke kowa kanshi ya rigada ya kulle.

"Malam kayi mani izini inje in kwato mata ta "
Cewar Al'ameen jikin shi na ciri.

"Muddun ka kusanci Wurin can ba za'a ɗaukoka a raye ba, domin Lubna da kake gani Aljanin dake jikinta a halin yanzu ya hau kanta ita kuma a halin yanzu tana halin suma, waccan kuma da kake gani rungume jikinshi ba kowa bace face matar shi."
Malam Saif ya ƙarasa maganar tare da kallon Mahaifinta dake kusa da Matarshi yana shafa

mata ruwa.

"Alhaji miya same ka baka bani amsa ba kuma ina ka samo Lubna."?
Mahaifin Al'ameen ya ƙarasa maganar tare da kafe Lamaru da ido.

"Dama..... Dama..."
Lamaru ya fara in ina.

"Zaka fada ko sai na murde maka wuya."
Uwar Garke ta faɗa a fusace.

Tsabar firgici diriricewa yayi tare da fara masu bayani.
"Ni ne nasa aka sace Lubna har cikin gidan nan."
Lamaru ya faɗa murya na kyarma.

A firgice Alhaji Sufyan ya kalli Lamari cike da mamaki, Al'meen kuwa badan yakai zuciya mesa ba da sai ya shaƙe Lamaru tun kafin aje ko ina.

"Kafin yarana suyi nasarar dauketa sunsha fama domin sai da Aljanin dake jikinta ya kashe mutum biyu daga cikin yarana kafin su shaƙa mata magani su sace ta, mun ɗauki Lubna ne domin a yanki rabin fuskarta ayi mani aiki in samu hayewa kujerar gwamnan garin nan amma yanzu komi ya ruguje bokan mu ya mutu Kungiya ta ruguje kowa ya mutu nima kuma nasan ban tsiraba domin yanzu haka azabar da nikeji cikin jikina bata misaltuwa."
Lamaru ya kasara maganar yana soshe_soshe.

Tsabar mamaki mahaifin Al'ameen kasa motsawa yayi daga inda yake Hajiya Salima kuwa mutuwar tsayetayi cike da zallar mamaki, kafin su an kara Al'ameen ya yi kukan kura ya shaƙi Alhaji lamaru ya ci gaba da bugu

Ganin zaiyi kisan kai da kyar malam Saif da Mahaifin Lubna suka banbare Al'ameen a jikin Lamaru.

Tamkar yunwataccen zaki haka Al'ameen ya zame masu da kyar Salima ta shawo kanshi ya fara dawowa cikin hayyacin shi.

Tamkar ranta zai fita haka Hajiya Murja ke darzar kuka tana kallon Hibba da aka ce mata aljana ce, gefen ɗaya kuma ga kwanda zai fashe yau wanda ta tabbata warin shi sai ya addabi kowa.

Falon yayi tsit babu sautin dake tashi se shasshekar Kukan Hajita Murja.

Tamkar za'a 6alle ƙofar falon haka aka harbo ta kaf mutanen dake cikin falon hankalinsu ya

koma ga masu ƙoƙarin shigowa falon.

Gaje ce a gaba tana ƙwalama Lubna kira tamkar zata fasa dodon kunnen mutanen dake cikin falon.

"Matsiyaciya kina ina ki fito yau sai na kashe auren ki ko baki so, au ashe kece nan tsaye kina jina kikayi shuru."
Gaje ta ƙarasa maganar tare da nufar Lubna dake Rungume da Hibba har yanzu.

Hannu ta kai da nufin fizgo Lubna, da sauri Mahaifin Lubna dake biye da ita a baya yayo kanta domin hanata abin kunyar da take niyyar yi, amma kafin ya iso wurinta tuni Aljanin dake amfani da gangar jikin Lubna ya kaima Gaje wani karbi da ƙafa.

Sai da ta wuntsila Tayo ƙasa sai gata gaban Uwar garke.

"Banyi niyyar muguntaba amma dole ko mari ne sai kinsha yanzu basai anjima ba."
Uwar Garke na rufe baki Ta shiga wanke Gaje da mari ta ko ina.

Ɗago kan da Uwar Garke zatayi idon ta ya sauka cikin na Malam sule dake tsaye, da matuƙar mamaki ta miƙe tare da Furta "malam Suleman!"

Shi kuma ya furta
"Uwar Garke."
Jikin shi na kyarma domin yasan yau abinda yazo ya bayyana anyi a sa'a yau zasu warware boyayyen sirrin da suka boye shekaru ashirin da biyu da suka shuɗe.

Su duka mutanen dake cikin falon miƙewa suka yi cike da zallar mamakin wannan rikitattun al'amura dake faruwa.

Miye haɗin Uwar garke da Malam sule?

Hibba da Lubna suna da alaƙa?

Miye alaƙar Murja da Lubna.

Da gaske Hibba Aljana ce bayan ga mahaifiyarta nan Murja?

Shin soyayyar gaskiya ce ta fara tsakanin Al'ameen da Lubna shida bai ƙaunar baƙar mace?

Ina labarin Leemcy?

Domin samun waɗan nan amsoshi kuyi mana SUBSCRIBE.👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻

https://youtube.com/channel/UCFefdlP2piaSVv-IAANrzBQ
👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽
KAINUWA TV DON NISHADINKU PLS KUYI LIKE & SUBSCRIBE👏🏼👏🏼👏🏼

Sai mun hade

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/19, 9:01 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE4️⃣0️⃣_4️⃣1️⃣*
...Duk zafin buguwar da Gaje tayi haka ta miƙe tare da nuna Malam sule da yatsa;
"Dama amanata kake ci ni zaka yaudara Sule ina kasan wannan matar, yau ni Gaje na shiga ukku na lalace wayyo Allah na."
Gaje ta karasa maganar cikin kururuwa.

Murmushin takaici yayi tare sa kallon Gaje.
"Komi zaki faɗa ki faɗa domin tabbas yau zan fasa kwai sirrin dana daɗe ina boyewa yau zani toneshi dan haka ki natsu ki saurare ni."
Mahaifin Lubna ya fada tare da samun wuri ya zauna.

Dukkan mutanen dake cikin falon sunyi shuru suna saurarar abinda zai faru domin yau kam kawunan su sun gama kullewa.

Lubna da Hibba dake tsaye nan suka fara ƙokarin guduwa, a firgice Malam Saif ya watsa masu wani ruwan addu'a sai gasu ƙasa warwas suna maida nunfashin wahala tare da sakin wata
```

razananniyar ƙara.

"Kuyi sauri ku samo wani abu a daure su."
Malam Saif ya fada tare da watsamasu ruwan addu'ar ta ko ina.

Wata kakkaurar iggiya aka ɗaure su da ita ta yadda ba zasu sake yunƙurin guduwa ba.
"Kunyi kuskuren da bazai taba gyaruwa ba,in gama bautama su tuƙuru na tsayin shekaru ina jikinta yanzu kuma kuce zaku fidda ni tabbas in na kubuta babu wanda zai rayu a cikin ku."
Lubna ta faɗa da muryar maza.

"Kaji tsoron Ubangijin daya halicceka ka bar Jikin wannan baiwar Allah, ka sauka a kanta domin ta fuskacin abinda muke tattaunawa a yanzu."
Malam Saif ya faɗa.

"Duk da ina saman kan Lubna amma tana ganin duk wani abu dake gudana a wurin nan maganace kaɗai bata iyawa."
Aljanin jikin Lubna ya faɗa

Malam Saif
Juyowa yayi tare da kallon su ɗaya bayan ɗaya.
"Dukkan ku na fuskanci kamar matsalarku iri ɗaya ce dan haka inaso ku sanar dani abinda ke faruwa koda zansan hanyar da zanbi dan gujema aikata ba dai_dai ba."
Cewar Malam Saif.

Malam sule ne ya fara magana.
"Kamar yadda kuka ga na shigo gidan nan, zuwa na yana da matuƙar dalili domin nazo me in warware abinda ya faru shekaru ashirin da biyu da suka gabata, kamar yadda kuka sani nida hannuna na bayar da auren Lubna gareku shine yasa na ɗauki alƙawarin warware maku zare da abawa a yau, Lubna dai ba ɗiyata bace bamu muka haifeta ba."
Malam Sule ya ƙarasa maganar tare da duƙar da kanshi ƙasa cike da jimamin abinda ya faɗa.

Dukkan wani me rai dake wurin sai da ya girgiza dajin wannan magana banda Hajiya Murja dake faman rusar kuka.

Gaje kuwa wata zabura tayi tare da miƙewa taci kwalar malam Sule.
"Wallahi ƙarya kake, kada ƙiyayyar da nike nunama Lubna ta jaka kace bamu muka haifeta ba, Sule ka faɗa masu gaskiya."

Ganin riƙon da Gaje tayima Malam sule yasa Malam Saif banbareta, Mahaifan Al'ameen kuwa tsabar mamakin waɗan nan abubuwa dake faruwa kasa magana suka yi.

Al'ameen shi yama rasa mike mashi dadi matar shi itace babu iyaye kenan ɗiyar tsintuwa ce,

innalillahi wa'inna ilaihirrajiun.

"Malam Sulaiman bakayi kama da mutumin da zai yi maganar da babu gaskiya a cikin ta ba, ina me gama ka da zatin Allah ka sanar damu gaskiya shin ba ku kuka haifi Lubna ba."?
Malam Saif y ƙaraaa maganar cike da zallar mamaki.

"Ina me rantsuwa da sunan Allah bamu muka haifi Lubna ba hatta Gaje batasan cewa Lubna ba diyar ta bace wannan sirri mu biyu kaɗai muka sanshi daga Uwar garke sai luma ni."

Kawunan su sake ƙullewa suka yi taya za'ayi mutum ya haifi ɗiya ace kuma bashi ya haifeta ba bayan ko makwafta suna shedar Gaje ita ta haifi Kulu da Lubna a rana ɗaya, amma wannan al'armari akwai sarƙaƙiya.

Fashewa da kuka Hajiya Murja ta sake yi.
"Alhaji ka yafe mani ka gafarta mani bandan mugayen halayena ba dan girman Ubangiji, Lubna dai ba ɗiyar Kowa bace face ɗiyarka ni kuma ni na haifeta da cikina."
Ta ƙarasa maganar tare da sake rushewa da sabon kuka.

Ruɗu, cushewar kai, rashin fahimtar abinda ke faruwa sune suka ziyarshi ilahirin jama'ar dake cikin falon nan mahaifin Hibba a razane ya miƙe tare da maimaita abinda Murja ta furta.

Malam Sule kuwa kallon marar hankali yake ma Murja domin ya lura kamar bata da ishasshiyar lafiya in ba haka ba taya za'ace daga ganin ɗiya tace ɗiyar su ce.

Hatta malam Saif wannan karon ya kasa firta koda kalma daya ce domin tunda yake bai taba fuskantar al'amari makamancin wannan ba.

Gaje kuwa kukan kura tayi tare da shaƙe Murja.
"Ƙarya kuke yi wallahi ina ƙaunar Lubna tsanarta da nayi bashi ke nuna bani sonta ba, in haifi ɗiyar amna ku Canza zance kuce ɗiyarku ce, yau komi ko ku a cikin gidan nan."
Gaje ta karasa maganar cikin ƙaraji.
Da kyar aka banbare gaje a jikin Hajiya Murja.

"Ina rokonku kafin in sanar da wannan boyayyan sirri daku ɗauko mahaifina ayi komi a gabanshi domin shine silar faruwar komi."
Rufe bakin hajiya Murja yayi dai_dai da shigowar mahaifinta da kallo ɗaya zakayi mashi ka gane yana jin jiki.

"Murja mun shiga ukku asirinmu ya tonu kwanan mu yazo karshe, Hibba ta illatani nasan bani ƙara kwanaki a duniyar nan."
Mahaifin murja dake kokarin shigowa ya faɗa.

Gani falon cike da mutane yasa Mahaifin Murja jan birki tare da kallon ɗiyar tashi.

"Murja su waje nan, domin me gadi ne yace mani kunzo gidan nan shin murja wani abu ya faru ne, mi Hibba keyi a ɗaure nan wurin."

"Baba abinda muka binne tsawon shekaru ashirin da biyu yau nida kai na zani tone shi, dama hausawa sunce rana dubu ta barawo rana ɗaya ta me kaya."
Murja ta karasa maganar tare da matse hawaye.

Jin abinda ɗiyar tashi ta faɗa baisan lokacin da yayi zaman yan bori ba domin yasan yau ƙaryar shi ta kare abinda ya aikata daga shi se diyar shi yau da Ubangiji ya tashi tona asirin shi seda aka tara taron jama'a sannan kowa zai ji abinda ya faru.

"Kamar yadda na fada maku labarin ya farane tun kafin aure na da mahaifin Hibba."

A SALIN LABARIN
Dafar ko dai Sunan mahaifina Alhaji mamman mahaifiyata kuma Sa'adiyya, tun bayan haihuwata mahaifana basu sake samun haihuwa ba tun suna saka rai har suka fidda tsammani nan suka tallafeni tare da nuna mani gata wanda ba kowa ke samun irin shi ba.

Mahaifina Alhaji mamman mutum ne me matukar arziki kuma dan siyasa wanda jam'iyyasu ta tsayar dashi matsayin shugaban kasa.

Duk da wannan dukiya da Allah yaba mahaifina amma kwadayin mulki bai sa ya hakura da kujerar nan ba sai ma dagewa da yayi wajen himmar ganin ya mulki ƙasar nan.

Mahaifiyata ko kaɗan bataji daɗin wannan mulki da ake ƙoƙarim liƙama mahaifina ba, tayi iyakar ƙoƙarinta ganin ta hana faruwar wannan abu kamasan cewar ita gani take mahaifina kwankin shi sun fara ja kamata yayi a samu matashi a ba wannan kujera domin ita sam bata kaunar milki ko alama, ranar data tunkari mahaifina da wannan maganar ranar ne naga zallar bacin rai tattare da mahaifina domin kuwa saida ya wanke mahaifiyata tas har kuka sai da tayi jin yadda yayi mata cin mutumcin da bai taba irin shi ba, nikam ko a jikina domin nafi ƙaunar mahaifina fiye da mahaifiya ta saboda mahaifina bai kwabata nare kyara abinda nike so shi nike yi.

A na cikin kacaniyar neman kujera kwatsam maza biyu suka fito neman Aurena Alhaji Jadda sai kuma Malam nura wanda ya kasance talaka ne amma akwai addini.

Tun bayan fitowar su neman aurena na lura hankalin mahaifiyata ya karkata ga Nura, inda ni kuma ganin na rayu cikin nera mi zamyi da auren talaka, mahaifina kuwa abinda nike so shi yake mani dan haka ya fatattaki Nura yayima Jadda Umarnin ya turo, ba'a dauki lokaci me tsayi ba aka sa mana rana da jadda.

Tabbas mahaifiyata tayi matuƙar baƙin cikin rashin miji me addini da nayi, amma ganin babu yadda zatayi yasa ta hakura tare da yi mana fatan zaman lafiya.

A kwana a tashi lokacin aurena yazo anyi biki wanda ba'a taba yin irin shi ba a kaf zuri'ar mahaifina, biki ne na ɗiyan manya biki na kece reni anyi wasa da kuɗi tamkar abun banza.

Tunda nike bantaba jin jikina yayi sanyi ba kamar sa'in da za'a ɗauki amarya mahaifiya ta ke mani nasiha.

"Murjanatu yau ita ce rana ta ƙarshe da zaki fita a hannun mu mumiƙa ki gidan mijin ki, murjanatu kiji tsoron Allah ki dena biyema mahaifinki ke mace ce rayuwa kuma rayuwar mace akwai kalubale a cikin ta, kada ki dauka rayuwar da kika yi a cikin gidan mahaifinki ita za kiyi a gidan wani, domin gidan da zakije ƙarƙashin wani kike, yau ita ce rana karshe da zaki rabu da me takura maki wato ni murja jikina yana bani tamkar wanna wata wasiyya ce nike maki domin inaji a jikina lokacin komawa ta ga mahaliccina yayi murja na yafe maki duniya da lahira Ubangiji ya tsare mani ke a duk inda kike."
Mahaifiyata ta karasa maganar tare da goge guntun hawayen dake fuskar ta.

Wani kuka ne da banyi niyyar yi ba naji ya kubce mani nadamar abinda nike ce ta lullube ni tare da rungume mahaifiyata ina kuka.

A ranar nayi kuka wanda ban taba yin irinshi ba tamkar raina zai fita haka aka miƙani gidan Mijina wato Alhaji Jadda.

Nakai kimanin watanni huɗu maganar Umma nayi mani yawo cikin kai, duk na canza nayi sukuku hatta aminiyata hajita Turai ta fuskanci halin da nike ciki. Ita ce ta ƙara zugani cewar bakomi bane face bankwana, nan na shashantar da maganar naci gaba da hidimomina.

Ƙalubale na farko dana fara fuskanta shine kwata_kwata Jadda bai da ilimin addini irin mutanen nan ne masu zallar boko da suka daɗe cikinta, sai naga duk rashin ilimina to na fishi sau dubu.

A wata safiya da bazan taba mantawa ba a cikin tarihin rayuwata, shine tunda asuba Jadda ya tayar dani mukayi sallah abinda bai taba yiba, bayan gama sallar naga ya kafe ni da ido da yaga zamu hade ido sai ya kauda kanshi.
"Ki shirya muje gida."
Wannan ita ce maganar daya faɗa mani tare da ficewa.

Ban kawo komi a raina ba ganin tunda nayi aure banje gida ba na dauka gaida su Umma zamuje yi, da murnata na shirya gari nayin haske muka dauki hanyar gida.

Tunda muka shawo santar gidan mu nike ganin mutane jifa_jifa suna kallon mu tare da girgiza kai, ban ƙara tsinkewa ba sai da muka shiga farfajiyar gidan mu naga mutane cike sunyi

jigum_jigum suna alwala.

Cike da mamaki na fito na nufi hanyar dakin Umma domin sanin mike faruwa, wani wawan birki naja ganin mahaifiyata an nannaɗeta cikin likafani fuskarta ce kaɗai a buɗe.

Tamkar zautacciya haka na fara girgizata ina kiran sunan ta.
"Umma ki tashi bazaki mutuba ki barni, karya kuke Umna bacci take ya za'ayi ma ta mutu ta barni umma ki tashi ki gaya masu baki mutu ba."
Na karasa maganar tare da fashewa da kuka.

Matan dake cikin ɗakin kuwa banda kuka babu abinda suke, ganin tamkar na fita a hayyacina yasa ƙanwar Umma janyeni.
"Murja sai hakuri wanda ya fimu ƙaunar Sa'adiyya ya ɗauki abinshi, Ubangiji Mungode maka Sa'adiyya Allah yasa can ta fiye maki nan."
Wannan maganar da inna Hassu tayi ji nayi kaina yayi wata sarawa nan na yanke jiki na faɗi.

Kai tsaye asibiti aka wuce dani, ban farka daga sumar da nayi ba sai da aka dawo daga kai mahaifiyata.

Jikina naji yayi mani wani irin nauyi wani abu ne ya tokare mani zuciya wasu hawaye ne suka balle a fuskata.

"Dan Allah Murja ki kiyi hakuri kodan abinda ke cikin ki likita yace jininki ya hau,ga kuma Juna biyu dake gareki har na kimanin watanni huɗu."
Cewar Inna Hassu ita ma hawaye nabin fuskarta.

Kwana na biyu a asibiti aka sallameni, tashin hankalin da nike ciki ba karami bane domin gani nike tamkar Umma bata mutuba da naje gida zani ganta amma ina wanda ya mutu bai taba dawowa har abada.

Sai da akayi sadakar bakwai mahaifina yace in koma gida domin laulayim da nike.

Tun bayan mutuwar mahaifiyata nike cikin wani irin ƙunci marar misaltuwa kewar ta nike matuƙa tare da tariyo maganganun da take gaya mani ashe da gaske wasiyyace daga ita ba zamu sake haɗuwa ba."
Koda yaushe hawaye ne ke gudana a fuskata ga laulayin ciki da nike fama dashi, Jadda shine me kwantar mani da hankaki a duk lokacin da yaga ina cikin damuwa domin ya kwallafa ranshi akan cikin nan dake jikina.

Haka kwanaki suka yita shuɗewa har yau cikina nada kimanin watanni takwas.

Kiran mahaifinane ya shigo wayata da sassanyar marecen lahadi.

Jin yace in same shi gida ko drive ban ɗauka ba haka naja mota sai gida.

Ganin halin damuwa da mahaifina ke ciki yasa ni fara tambayar shi.

Dogon Numfashi yaja tare da zama bisa kujera ya fara magana.
"Sanin kanki ne kece ɗiya kwalli ɗaya da muka mallaka, na soki fite da komi a rayuwa ta, na nuna maki gata wanda ba kowane ɗa bane ke samun irin shi,a yanzu ina da yaƙinin duk abinda nace ina so zaki iya mallaka mani domin ba zaki so in fadi wannan kujera da nasa gaba ba,buƙata ce nike da ita wadda duk duniya kece me iya yi mani ita a matsayinki na ɗiyar da nike gani inji sanyi a cikin raina."
Mahaifiya ya ƙarasa maganar tare da kafe ni da ido.

Cike da zaƙuwar jin buƙatar mahaifina na amsa mashi komi ye zanyi.

Abinda naji ya faɗa ne yayi sanadin Miƙewata tsaye ba tare dana shirya ba a matuƙar firgice, ƙaton cikin dake gabana ne yayi wata murɗawa tamkar ɗan dake ciki zai faso ya fito waje,ba shiri na sanya hannuwa na biyu tare da dafe ciki na....

👇🏻👇🏻👇🏻Kada a manta da yi mana subscribe

https://youtube.com/channel/UCFefdlP2piaSVv-IAANrzBQ
👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽
KAINUWA TV DON NISHADINKU PLS KUYI LIKE & SUBSCRIBE👏🏼👏🏼👏🏼

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/21, 12:12 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*
```

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE 4️⃣2️⃣ 4️⃣3️⃣*
...Ƙafafun na danaji sun kasa ɗauka tane yasa ni saurin zamewa bisa kujera amma har yanzu abinda ke ciki na be daina motsiba.

Wannan magana da mahaifina ya gaya mani tayi masifar tayar mani da hankali domin a kona mafarki banyi tunanij jin makamancin abinda naji yanzu ba.

"Alfarma guda ɗaya dana nema a wurinki ita ce ba zaki iyayi mani ba Nurjanatu."?
Mahaifina ya fada tamkar zai zubda hawaye.

"Ka gafarceni abinda ka nema ba me samuwa bane rayuwa ce sunkutukum kake nema in salwartar, yakai mahaifina idan na mallaka maka abinda ke ciki na ya zanyi da mahaifin shi wato Jadda, kace in babu shi tabbas bazakaci zabe ba, Shin kasan tsayin lokacin da Jadda ya ɗauka yana tanadi kuwa muddin muka salwantar da rayuwar ɗashi ko kuma ɗiyar shi wallahi baba ina cikin tashin hankali."
Na karasa maganar tare da fashewa da kuka.

"Yanzu Murja wannan ita ce sakayyar soyayyar dana nuna maki, da abinda zaki saka mani kenan, jinin ki ɗaya da zaki salwantar saboda ni amma ba zaki iya ba tabbas kin bani kunya, to ki sani muddun kika ce ba zaki mallaka mani abinda ke cikin ki ba Murja daga yau na datse duk wata alaƙa dake tsakanina dake."
Mahaifina ya ƙarasa maganar rai a matuƙar bace.

Cike da tashin hankali naji gabana yayi wata mummunar faɗuwa lokaci ɗaya hawayen dake kai kawo a fuskata suka tsaya.

"Na rene ki tun daga yarintarki har girmanki amma ni zan nemi buƙata a wurin ki kihana, yau na fahimci baki ƙaunata Murja."

"Zanyi komi kake so, amma ya zamuyi da Jadda daya kwallafa rai a kan wannan cikin."?
Na faɗa cikin hanzari domin a lokacin zuciyata ta bushe na yarda in sadaukar da jaririna domin mahaifina ya cika burin shi.

Wani farin ciki marar misaltuwa ne ya ziyarci mahaifina ji yayi tamkar ya goyani domin yasan burinshi ya gama cika.
"Ina Alfahari dake Murjanatu, idan watan haihuwarki ya tsaya zani bukaci jadda ya barki ki dawo gida zan samo cikin dangina wata ta riƙa kula dake domin in kina kusa dani ne kaɗai burin mu zai iya cika, in aiwatar da abinda nasa gaba batare da munfuskanci wata matsala ba."

Jin wannan jawabi na mahaifina se nayi na'am dashi lokaci daya naji ƙaunar da nike ma abinda ke ciki ta kau domin nasan yana zuwa duniya rayuwarshi zata shiga cikin haɗarin da mutuwa ce kawai hutu a gare shi, gida na koma cike da shirya irin ƙaryar da zani shiryama Jadda.

Kasancewar shi mutum ne ɗan boko bai wani ƙiya ba lokaci daya ya yarda inje gida in watan haihuwata ya kama, nikam jin ya amince wani farin ciki ne ya lullubeni.

A kwana a tashi babu wuya wurin Allah domin yanzu watan haihuwata ya kama inda na rika wata irin rashin lafiya tamkar me naƙuda, haɗa kaya na nayi Jadda ya miƙani gida cike da farin cikin magajin nashi ya kusa zuwa duniya, tsohon ɗakina da nayi rayuwa cikin shi lokacin ina budurwa nan mahaifina yasa aka gyara mani, nida wata tsohuwa da bansan inda mahaifina ya samota ba.

Kulawa ta musamman mahaifina ke bani domin ganin na sauka lafiya ya, Nikam banida burin daya wuce in sauka lafiya in rabu da wannan cikin domin nasan indai haihuwa ce yanzu na fara, dan nayi kyauta da wannan ta farko ba wani abu bane.

Wani yammaci nida mahaifina muna zaune muna hira nike cewa
"In na sauka lafiya, shin ya zamu yi da Jadda idan ya buƙaci ganin abinda aka haifa."?

Dogon Numfashi mahaifina yaja tare da fara magana.
"Na gama shirya komin domin hatta gawar jariri tuni nasa anyi mani booking kina haihuwa za'a kawota domin wannan al'amari ba ƙaramin shiri nayi mashi ba kedai Ubangiji ya sauke ki lafiya." Mahaifina ya faɗa.

Ba'a ɗauki wani lokaci me tsayi ba ciwon naƙuda ya kamani, wannan tsohuwa ita ta kula dani tare da bani duk wani temakom gaggawa da ake buƙata, tun safe nike abu ɗaya har la'asar, na wahala tamkar bazan rayu ba, hankalin mahaifina yayi matuƙar tashi ganin yadda ake abu ɗaya tun lokaci me tsayi, kamar yadda ya buƙata ina haihuwa tsohuwar nan me kula dani ta gyarani jaririyar kuwa kamar yadda ya gargaɗeta bata taba ta ba.

Wani tunani ne ya rika yi mani yawo cikin kwalwa.
"Ke Murja yanzu ɗiyarki wadda kika sha wahalar haihuwar ta ita zaki salwantar saboda abin duniya, abinda kike ƙoƙarin aikatawa yanzu fa matsayin kisan kai yake, shin kinada tabbacin zaki sake haihuwa idan kin salwantar da wannan, haƙƙin Mahaifinta zai barki ki zauna lafiya kuwa."?
Naji wata zuciya na gargaɗi na kada in aikata haka.

"Allah me tausayin bayin shin shi ne, ki aikata daga baya baya seki tuba."
Wata zuciya ta fada mani, shigowar Mahaifina ce ta katse mani tunanin da nike.

Ganin ga Jinjirara nan cikin jini ko gyarata ba'ayi ba yasa Mahaifiya sanya hannu ɗaya ya dagota, wani sabon kuka ne jinjirar ta ƙyaƙyace dashi, kukan da kana jinshi kasan kukane da take buƙatar jin gumin mahaifiyar ta take bukata a shayar da ita tamkar yadda ake ma ko wane jariri, amma ita tun bayan zuwanta duniya haka aka barta cikin jini a ƙasa a yashe sanyi na shiga jikinta.

Saman wani ƙaramin benci Mahifina ya sanya jinjirar tare da daukar wani zane ya rufeta.
"Kina da buƙatar ganin ɗiyar ki kafin ƙaddararta ta risketa."?
Naji Mahaifina ya faɗa.

Samun kaina nayi da dirowa daga saman gadon tare da nufar jinjirar na buɗe fuskarta, kyakkyawa da ita sak Ni ta biyo wurin kyau amma baƙin mahaifinta ne ta ɗauko ,kururu take tamke tamkar taci babu hannun ta ɗaya yana cikin baki tana ta tsotsa, abin mamaki idanunta bude suke tar! ganin wani abu na ƙoƙarin ɗarsuwa a zuciyata yasa nayi saurin barin wurin tare da hayewa saman gado wani abu me kama da nadama na ƙoƙarin ɗarsuwa a zuciya ta.

Wata farar Kwalba naga mahaifina ya fiddo daga cikin Aljihu tare da nufar Fuskar jinjirar.

Cikin ɗaga murya naji mahaifina ya fara magana.
"Yakai Hatsabibin baƙin Aljani kayi sani cewa mun cika maka burinka wannan jinjirar ta zama mallakin ka, muma ka cika mana namu burin."
Yana kaiwa nan ya buɗe kwalbar tare da danna bakin ƙaramar kwalbar cikin hancin jinjirar, wata mahaukaciyar ƙara jaririyar ta kwala tamkar ana yankan naman jikinta, idanun tane suka rufe lokaci daya barin Fuskarta ya fara rikiɗewa yana komawa na maza.

Murmushin Farin ciki mahaifina ya saki domin yasan wannan alamace ta Aljanin ya koma ƙarƙashin ikon su, yanzu zasu milke shi.

"Taso kiyima ɗiyar ki kallon ƙarshe, domin kana daga cikin mutanen da keda damar ganin fuskarta a halin yanzu.

Wata mummunar faɗuwar gaba ce ta ziyar ceni sa'in da nayin arba da Fuskar jinjirata data koma rabi ta namiki rabi ta mace, saurin ja da baya nayi tare da furta.
"Baba mi hakan ke nufi."?

Murmushi yayi
"Yana nufin daga yanzu har zuwa karshen rayuwar ta a haka zata rayu, ba zata taba warkewa ba."
Ya karasa maganar tare da kafeni da ido.

"Bani sonta dan Allah kada ka bari ta rayu, a jefar da ita inda ba zata taba rayuwa ba."
Na fada a rikice domin a lokacin na tsorata matuƙa.

A gabana mahaifina ya kira wani amintaccen yaron shi ya miƙa masu jinjirar da Ke faman bacci ne ko suma domin jikinta tamkar ta mutu nike gani, ficewa suka yi da ita, nan mahaifina ya ɗauko gawar jariri sabuwar haihuwa tare da mika mani a matsayin wadda zamu mikama Jadda cewa abinda na haifa ya mutu.

Koda su Cika aiki suka fito da jinjirar kai tsaye, wata babbar kwalbatin dake cikin wata Unguwar da mazauna cikin ta akasarin su talakawa ne naga sun nufa, kwalin suka jefa cikin kwalbatin tare dayin gaba abinsu.

Jadda kuwa Jin ɗanshi ya mutu seda ya zubar da hawayen baƙin ciki domin ya kwallafa ma ranshi soyayyar yaron.

Mahaifina kuwa duk da beda wasu masoya masu yawa cikin al'umma amma shine wanda ya lashe zaben shugaban ƙasar, munyinfarin ciki mara misaltuwa da wannan mataki da mahaifina ya taka.

Ban koma gida na ba seda nayi kwana arba'in sannan nakoma gidan Jadda, Rabo me gaggawa Rabon da shine har gobe nike kira Rabon wahala shine samun cikin Hibba da nayi ban yima da komawa gidan Jadda ba.

A wannan karon hattani wata irin soyayyace nike nuna ma cikin domin duk wani buri namu to ba shakka yana kan cikin nan, tun yana da wata bakwai muka bar ƙasar n muka nufi India domin can nace zan haihu.

Zuwan mu india shine asalin faruwar komi shine mafarin labarin, kamar yadda muke zaune a hotel tun bayan zuwan mu ƙasar, zaune nike bisa kujera ina cin tuffa, Jadda kuwa ya fita ya dawo.

Ƙofar da naji ana kwankwasawa ce ta sanyani tashi domin a tunani na Jadda ne ya dawo, turus! nayi sakamakom tozali da nayi da wata mata wadda kana ganinta kasan haifaffiyar kasarce, kallo daya nayi mata naji gabana yayi wata mummunar faɗuwa domin wani irin gashi ne da ita tun daga saman kanta har kasa yana jan ƙasa, ga wasu fararen kaya jikin ta tamkar fatalwa idanunta kuwa jajur tamkar garwashin wuta.

Bankaɗeni tayi tare da shigowa dakin tana me fashewa da wani irin kuka daya haddasa ma ɗakin fara girgiza.
"Kece wadda ta rabani da farin cikina, kece wadda tayi sanadin zamana cikin kaɗaici ita kuma take rayuwa cikin farin ciki, na dauki alƙawari daga yanzu har zuwa ƙarshen rayuwarki zaki yita ne cikjn tashin hankali da kuma zullumi."
Matar na kaiwa nan kafin in an kara ta zama hayaƙi tare da shigewa jikina, daga lokacin ban sake sanin mike faruwa ba sedai ganina nayi kwance Jadda na jero mani sannu.

Tun daga wannan lokaci na daura aure da mafarkin matar nan tana zo mani zata kashe ni.

Babban tashin hankali shine zuwan Hibba duniya, jaririyar da tasha banban da sauran jarirai, likitocin da suka amshi haihutawa suma sun sha manakin ganin jinjirar da aka ɗora a jikin mahaifiyarta lokacin zuwan ta duniya amma se gani akayi ta mulmulo ta faɗo kasa duk buguwar da jaririyar tayi bai sa ta buɗe baki da niyyar kuka ba, a rikice likitoci suka dauketa tare ta bani ita domin in shayar da ita, nan ma ta datse bakinta taƙi sha tare da kafeni da ido.

Hankalin malaman asibitin nan fa ya tashi matuƙa ganin wanan irin jaririya da aka haifa masu, nikam a halin yanzu na tsorata matuƙa da ganin wannan al'amari.

Madarar shanu ita ce ta zama abincin hibba na tsawon rayuwar ta har i zuwa girman ta, tun tana jaririya take azabtar da rayuwa ta duk duniya mahaifinta kaɗai ke ganin dariyar ta.

Dakatawa tayi da maganar tare da fashewa da kuka, duk wani me rai dake cikin falon jin irin zaluncin da suka aikata seda ya zubar da hawaye, Alhaji Jadda kuwa mutuwar zaune yayi idanunshi ne kaɗai ke zubar da hawaye domin yasan Murja ta gama cutar shi.

"Innalillahi wa'inna ilaihiraji'un."
Ita ce abinda Malam Saif ke memetawa.

"Kun tafka babban kuskure, son duniya yasa kin biyema mahaifinki kun aikata abinda Allah yayi hani dashi, duk saboda mulki wanda yanzu harya gama mulkin gashi nan yana girbar abinda ya shuka, babu tausayi bare imani haka kika salwantar da ɗiyarki da kika haifa, duk dan saboda cikar wani burinku na duniya, Ubangiji ya kiyashemu da aikata makamancin abinda kuka aikata."
Malam Saif ya ƙarasa maganar cike da zallar bacin ran wannan rashin imani da suka aikata ma Lubna.

Mahaifin Lubna sam ya kasa magana hawaye ne kaɗai ke zuba a idanunshi.
"Yau shine aka salwantar da ɗiyarshi aka tarwatsa mata jin daɗin ta aka zama sanadin rasa wani sashe na jikinta, tabbas Murja tayi ma shi cutar da har abada bazai taba yafe mata ba."

Mahaifin Murja kuwa kuka yake tamkar ƙaramin yaro domin yau abinda suka binne yau ya tonu a bainar jama'a.

"Ina me roƙonka da girman Allah Alhaji Jadda kada kayi magana, mu jira muji ta bakin Mahaifin Lubna wato Malam Sule taya ya samu Lubna ya akai ta zama ɗiyar Gaje ba tare da Gaje tasan ba ita ta haifeta ba wannan abu akwai ɗaure kai, gashi dai kowa ya shaida Lubna ɗiyar Gaje ce, dan haka muna saurarenka ka warware mana wannan ƙulli muji gaskiya abinda ya faru shekaru ashirin da biyu da suka shuɗe."
Malam Saif ya karasa maganar tare da kafe Malam Sule da Ido.

Yaƙe Malam Sule yayi wanda ake kira kafi kuka ciwo ya kalli Gaje dake faman Zubda hawaye, girgiza kai yayi cike da takaici ya fara bada labari kamar haka....

🚶🏻‍♀️Uwar Garke bata bada izinin a bada labarin a wannan page ɗin ba🚶🏻‍♀️ Mu haɗe a page na gaba....

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/23, 9:25 AM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
        _Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
        *M.W.A*

 *Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE4️⃣4️⃣_4️⃣5️⃣*
...Dafarko dai suna na sulaiman sai kuma matata Gaje, asalin mu munaten Lubya ne wata annoba a kayi ita ta baro mu da garin mu da acan ne kaf dangin mu suka rasu se yar uwar Gaje guda ɗaya da muka tsira tare, mun dawo wannan gari ne ba tare da mun mallaki komi ba.

Farkon shigowar mu wannan gari ba ƙaramar wahala muka sha ba domin sai da muka shigo ne na fuskancin ba irin rayuwar da muke bace suke, komi nasu na kuɗi ne, nasha baƙar wahala kafin in mallaki gida nawa na kaina har dako sai da nayi dan ganin na samu abinda zamu rufawa kanmu asiri.

Ubangiji ya haɗani da makwafci na kirki me matuƙar tausayin jama'a wadda yasan haƙƙin maƙwaftaka wato Mahaifin Saratu, shine wanda ya jani zuwa cikin kasuwa a hankali ya sanya ni cikin harkokin su na kasuwan ci, ganin yadda nike da kwazo yasanya shi bani babban jari nima na fara sana'ar sayar da hatsi.
```

Ta bangaren Gaje kuwa mace ce masifaffiya marar dađin zama a ƙalla zuwan mu unguwar nan tayi fađa da mutanen da suka haura biyar, Sam gaje bata ganin girmana inyi mata Umarni ta take shi sam ba zata bi ba, bala'i da masifar Gaje harna fara sabawa dasu batun yau ba,kamar ko yaushe yau ma nadawo daga kasuwa a gajiye amma sam Gaje bata dafa koda kwayar hatsiba, cike da Zallar ɓacin rai na kalleta.
"Yanzu Gaje in je kasuwa in dawo amma ace baki dafa abinci ba yanzu ya kike so inyi da yunwar dana kwaso."
Na karasa maganar cikie da takaicin a binda tayi mani.

"Nifa mazan hausawa kuna bani mamaki, yanzu Malam da wannan ƙaton cikin zanji ko kuma da aikin gida, shikenan haka zan tashi in hau aiki ga cikin nan kasan dai wata na ya tsaya harna fara naƙudar tsattsaye, to ni daga rana me kamar ta yau na gama dafa abinci gidan nan har sai na sauka."
Gaje ta ƙarasa maganar tare da murguda ma shi baki cike da masifar dake cinta.

"In yawo ne Gaje babu inda baki zuwa cikin unguwar nan kullum nadawo se nasa an nemo mani ke gidaje, amma abinci da zaki đan dafa daga bakina Sai naki shine yayi maki wahala."
Na ƙarasa maganar ina kallonta.

Miƙewa tayi tare da kallo na.
"In jajen kaza arziƙi ne malam ai sai kayi, ni kaga wucewa ta."
Gaje ta shige đaki tare da bari na nan tsaye a inda nike.

Ganin ba yau Gaje ta fara yi mani haka ba yasa ni hura wuta tare da sulala taliya domun saboda halin irin na gaje Babu arziƙi na koyi Girki.

Abinda zai baku mamaki shine sam Gaje bata addu'ar Ubangiji ya bata yaro nagari ko labari ake sai dai kaji tana fađar,ita kyakkyawa zata haifa kamarta, ta tsani mummunan jariri.

Wannan maganganu na Gaje suna matuƙar bani mamaki domin ni yara na gari wadan da zanyi alfahiri da su nike nema ba wai kyawawa ba.

A wani dare, daren da shine a salin faruwar Komi Gaje ta tashi da wata masifaffiyar naƙuda, ihun da take rarakawa ne tana đura mani zagi sune suka tayar dani daga baccin da nike.

Hankali a tashe na rasa shin ina zani nufa da wannan tsohon daren Makwafcina dai Matarshi taje unguwa shi kađai ne gidan, wata zuciyar ce tace inje in kirawo Yayar Gaje, dan haka cikin hanzari ba tare da tunanin abinda zai iya samuna cikin tsohon daren nan haka na fice gidan afujajan.

Tafiya nike bakina đauke da addu'a domin duhun dare ne sosai bakajin ƙarar komi se kukan

karunuka, ban bar bakina hakanan ba ambaton Allah naci gaba dayi tare da karanto duk wata Addu'ar da tazo baki na.

Ina gaf da ƙarasawa wurin kwalbatin da ta raba mu da gidan yayar Gaje wano sautin kukan Jaririya ya dakar mani kunne, razana naɗan yi domin nasan badai mutum ba sedai Aljani, a hankali na tunkari kwalbatin zani tsallaka bakina ɗauke da addu'a, kukan Jaririyar ne ya tsananta tamkar zai fasa dodon kunne na, abinda na lura shine cikin kwalbatin kukan ke fitowa, tamkar in yi gaba se kuma wata zuciyar tace tsaya in duba, haskawar da zanyi se Ganin abu nayi cikin kwali yana motsi kuma da gani daga ciki sautin kukan ke fitowa.

Dakewa nayi tare da addu'ar Ubangiji ya bani ikon taimakon abinda ke cikin kwalin, dirawa nayi cikin kwalbati tare da rarumar kwalin na fidda.

Buɗewar da zanyi se Ganin Jaririya nayi duk jini sai tsala kuka take, abin mamaki rabin fuskarta ne kaɗai ke kuka rabin kuma a rufe yake da zanin da aka lullu6eta.

Hannu nasa tare da fiddota na riƙe a hannuna cike da Al'ajabin wane marar imani ne ya haifata kuma ya jefar da ita

 Gabas da yamma na duba ko ina amma banga kowa ba, juyowar da zanyi se ganin mace nayi tsaye gabana, gabana ne yayi mummunar faɗuwa addu'ar da nike yi ce na tsanan ta.

Tare da kafe macen dake gabana ido, mace ce da bazata haura shekara Talatin ba sanye take da baƙaƙen kaya.

"Baiwar Allah mutum ko aljan."?
Na samu bakina da furtawa.

"Ni Aljana ce Amma ka kwantar da hankalin ka ba cutar dakai nazo yi ba, Malam Sulaiman da farko dai ni suna na Uwar garke, ba komi bane ya bayyanar dani a wajen nan ba se zummar ɗaukar jinjirar dake hannunka domin ni in reneta, wannan jariraya da kake gani iyayenta sun cuci rayuwarta tun zuwanta duniya zalinci da ban taba gani wata uwa ta aikata ma ɗiyarta ba, abinda nike so in sanar dakai shin zaka iya riƙe wannan jinjira me ɗauke da fuskoki biyu a jikinta."?
Uwar Garke ta faɗa kai tsaye.

Hatta sanar dani da tayi ita Aljana ce bai haddasa mani faɗuwar gaba ba kamar yadda maganar ta ta yanzu ta daki zuciyata; "fuska biyu, to ko mata maza ce ɗiyar.
"?
Na tambayi kai na.

"Kada kaba kanka wahalar tunane_tunane, yanzu zani warware maka zare da abawa, ita dai wannan jinjira da kake gani an haifeta lami lafiya daga baya aka yi sanadin canzawar fuskarta

wato dai ta koma RUWA BIYU rabin mace rabi namiji, shin zaka riƙeta a matsayin ɗiyarka ko kuwa ni zaka bani ita in riketa, amma ka sani in har ka bani ita tabbas zani reneta da wata irin guba wato gubar tsanar mahaifanta gubar rashin tausayi da kuma shirin ɗaukar fansa, shin zaka iya ruƙon ta in bar maka ita."?
Cewar Uwar Garke tana me kafe Malam Suleman da ido.

Kai na ne ya cushe da tunane_tunane, "anya zan bar ta tareni wannan yarinya kuwa ya kamata inyi jihadi ni in reneta a matsayin ɗiyata, to ya zanyi da Gaje anya zata iya renan wannan jinjira."?
Na tambayi kai na.

"Kada ka damu da Gaje, in dai ka amince da renan wannan jinjira to zani temake ka, yanzu haka Matar ka ta sauka lafiya ta haifi mace amma sakamakon wahalar da tasha yanzu haka a sume take, yanzu zamu ɗauki wannan jaririya mu haɗa da ɗiyar ka a matsayin yan biyu Gaje ta haifa, ni zani gyara jariran harma da uwar kafin ta farka daga sumar da tayi, kaga koda ta tashi zata ɗauka cewa yan biyu ne ta haifa, kace mata kai ne kayi aikin gyarata da kuma Jariran, in mukayi haka tabbas jinjirar nan zata rayu ne a matsayi ɗiyar Gaje ba tare da wani yayi kokonton wani abu ba domin dama yan biyu ana haifar wasu ba tare da sunyi kamanni ba, shin wannan shawarar tayi maka."?
Uwar Garke ta ƙarasa maganar.

"Tabbas wannan shawara tayi mani kuma nayi alƙawarin renon ta tamkar Yadda zan reni ɗiyar da aka haifa mani babu wanda zaiji wannan sirrin in shaa Allah har se lokacin bayyanar shi yayi."
Ina gama maganar muka karasa gidana

Kamar yadda Uwar Garke ta fada haka ta kasance ita ce wadda ta gyara yaran tare da Uwar, abun ka da aiki irin na Junnu hatta ruwan xafi ita ta dora mana tare dayi mani bankwana ta bace.

Dogon Numfashin naja tare da kallon Jariran dake gefen Gaje suna sharar bacci domin wadda na tsinto ana cikin yi mata wanka bacci ya ɗauke ta.

"Ko ya Gaje zata ji in ta farka taga wannan ɗiyar."
Rufe baki na keda wuya Gaje ta farka daga Sumewar da rayi.

Kallo na tayi tare da kallon jariran.
"Ni ce na haifesu."?
Ta jeho mani tambayar fuskarta bayyane da farin ciki

"Eh kin samu yara biyu duk mata."
Cike da murna ta diro daga gadonta tare da nufar yaran da aka shirya cikin kayan sanyi.

Wani ihu ta saki tare da yin jifa da jinjirar data fara ɗauka.
"Na shiga Ukku ni Gaje shin Me na haifa haka, yanzu wannan Mummunar halittar diyata ce."
Gaje ta faɗa tare da nuna jinjirar data jefar da hannu.

Niko a firgice na ɗauki jinjirar dake faman tsalar kuka tamkar ranta ze fita.

"Tabbas Gaje bakida hankali kin kasance marar ilimin addini domin duk me ilimi bazai ta6a aikata abinda kika aikata ba, Ubangiji ya kamata kiyi ma godiya da saukarki lafiya da yayi tare da azurtaki da kyautar da ba kowa ne ake yuma ita ba ta haihuwar Ƴan biyu, amma tsabar baki da hankali shine zakiyi mani jifa da ɗiya."?
Na karasa maganar rai na a bace ga kuma jinjirar dake tsanyara kuka.

"Wallahi bani son ta bazan taba shayar da ita ba, ya zama dole a barta ta mutu domin wannan annobace na tsaneta bani ƙaunarta, ka bani ita in murɗe mata wuya kowa ma ya huta."
Gaje ta karasa maganar tamkar zautacciya.

"Baki da Hankali, wallahi koda wasa kika salwantar mani da ɗiya se kin gane wane ne ainahin Sulaiman."
Na faɗa cike da 6acin ran kukan da Jinjirar ke tsanyarawa.

"Ka cuceni da baka kira mani yayata ba da nasan tana ganin abinda na haifa kafin indawo cikin hayyacina zata murɗe mata wuya kowa ya huta."
Cewar Gaje dake ƙoƙarin ɗaukar ɗayar jinjirar.

Kukan da take tsayawa yayi ganin kyakkyawar jinjirarta.
"Wannan ita ce ɗiya ta, ta hannunka kuwa na yafe ta bani sonta bani ƙaunar ta."
Gaje ta fada babu kunya bare tsoron Allah.

"Ubangiji ya ganar dake, amma ki sani abinda zani faɗa maki ki dawo cikin hankalin ki muddun kika bari wani abu ya samu diyata zaki gane shayi ruwa ne."

"Kanka ake ji domin ni nagama magana, ka samu wadda zata shayar maka da ita nikam zama cikin cikina ma da tayi ban yafe mata ba dan haka wannan matsalar ka ce."

Tamkar an watsa mani ruwan darma haka na riƙa ji a cikin zuciyata, dan haka ficewa nayi tare da ajiye mata jinjirar a gefen ta, kai tsaye kasuwa na wuce tare da sawo madarar jarirai me matukar yawa wadda zata ishi jaririyar.

Ƴan barka ne suka fara cika gida, nan fa suka fara watsewa ɗaya bayan ɗaya jin wannan halitta da aka haifi jaririyar da ita, nan fa gari ya hade da an haifi ɗiya me fuskar mace da namiji duk inda na wuce sai an nuna ni ana shine Ubanta, kafin kace mi gari ya haɗe da zantuttukan ƙarya dana gaskiya, Gaje kuwa ji take tamkar ta hallakar da jinjirar, dawowa ta gida abinda na tarar ya tayar mani da hankali domin yadda na aje Jinjirar haka na dawo na taras Gaje bata tabata ba,

daukar ta nayi tare da yi mata huɗu ba da Lubna, ɗayar kuma nasa mata Hawwa'u.

Lubna kuwa madara na dauko domin nasan yunwa ta gama galabaitar da ita amma sai gani nayi dana bata sai ta maido ta, tambayar Gaje nayi ko ita ta shayar da ita, a wulakance ta kalleni tare da fadar Allah ya sawwaƙe ta ba wannan halittar mama.

Ban sake bata madarar ba sai na kyaleta domin a tunanina ƙila wannan Aljana ta bata abinci ne.

A haka har akayi suna mutane wasu basu sake waiwayar gidan ba, Yaya asibi ita ce yayar Gaje wadda ke kara tira Gaje kan cewa ta kashe ta kada ta bari ta girma.

Ganin haka yasa na kashe wasu ayyukana dan ganin na lura da yadda Lubna ke rayuwa.

A wata rana da bazan taba mantawa ba lokacin na dan fita kasuwa in sawo ma Lubna madarar ta data ƙare, tun kafin in gama siyayyar naji gabana na faɗuwa, babu shiri nayo gida affujajan.

Ɗakin na shige tare da kwalama Gaje kira, zaune na isketa tana ma Kulu wanka.
"Ina lubna."
Ita ce tambayar dana jefama Gaje.

Banza tayi dani tamkar bataji mi nike fada ba, sai da na sake daka mata tsaka kafin ta fara magana.

"Karfa ka cika mani kunnuwa da surutu, gani nayi ruwan wankan ta ya tafasa kai kuma baka nan shine na ɗauketa na sakata cikin tukunyar kaga in kazo sai ka tsamota ka wanke ta nasan lokacin ta jiƙu."

Wata mummunar faɗuwar gaba ce tayi mani dirar mikiya, lokaci daya naji jiri na ƙoƙarin kayar dani.
"Kin sakata cikin tukunyar ruwan zafi fa kika ce."?

"Haka nace ko kunnuwanka sun fara samun matsala ne bakaji magana ta dai dai ba."
Gaje ta fada cikin gadara.

A gigice nayo waje har ina tuntube da tudunka bakina na furta.
"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un."
Tare da nufar ƙatuwar tukunyar dake saman murhu tana tafarfasa...

*A yi mana Subscribe 👇🏻👇🏻*
https://youtube.com/ channel/UCFefdIP2piaSVv-IAANrzBQ

👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽
Idan kuka latsa zaibude saiku latsa inda aka rubuta *SUBSCRIBE da jan rubutu*
*Aslm dan Allah yan uwa ga YouTube channel dina nan kumin subscribe za muna maku posting na magunguna kala kala da cooking kala kala da karatu tuka da novels masu zafi.👏🏼👏🏼👏🏼👏🏼👏🏼*

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/25, 10:22 AM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE4️⃣6️⃣_4️⃣7️⃣*
...Tamkar zautacce haka na rarumi murfin tukunyar tare da jefar dashi gefe, abinda na gani cikin tukunyar ya matuƙar bani mamaki, Lubna ce kwance saman ruwan tana sharar bacci abinta, hannu nasa tare da ɗaukota ina me yin hamdala ga Allah.

Rumgumeta nayi sosai a jikina bansan lokacin da wasu hawaye suka ɓalle mani ba.
"Ubangiji kai kasan mi kake nufi da wannan baiwa taka Allah ka shiga cikin lamuranta ka kawo mata sauƙin al'amura ya Allah, ka sanya ta cinye wannan jarabawata ta."
Na ƙarasa maganar tare da shigewa ɗakin.

A wulaƙance Gaje ta kalleni cike da mamakin ɗiyar dake hannun na bata ga ta ƙone ba.

"Kina mamaki ne da ikon Allah?, kinga muguntar da kikayi bata yi tasiri ba shine kike mamaki, to wannan kaɗan daga cikin ikon Allah kenan, babu abinda zance maki duniyace Gaje wanda
```

be zo bama jiran shi take."
Na ƙarasa maganar tare ds Sanya Lubna cikin ɗan ƙaramin Net na jarirai."

"Oho dai in ma mayya ce sai dai ta cinyeka amma ni Gaje jini na yafi ƙarfin nata."
Gaje ta karasa maganar tare da barin ɗakin.

Tabbas Gaje tayi nisa batajin kira se dai in bita da addu'a, kayan Jikin Lubna na cire tare da canza mata wasu, baccin ta take har yanzu bata farka ba.

Bazan manta ba bayan sallar magriba ina daga tsakar gida zaune in ba Lubna madarar jarirai na fara jiyo ihun Gaje, yunƙura nayi da niyyar in kai mata ɗauki amma kafin in ƙarasa har ƙofar ta rufe kanta.

Cike da tashin hankali nike hallon ɗakin da gaje ke kurma ihu ga kuma ƙarar sautin bulalai nan dake tashi ta ko ina.

An ɗauki ƴan daƙiƙu kafin ɗakin ya buɗe kanshi Gaje ta fito a guje tana soshe_soshe jikin nan yayi jajur sawun bulala kaɗai kake hangowa.

Kallo ɗaya nayi mata tare da shigewa ɗakin in na barta domin nasan wannan aikin Uwar Garke ne, ina jinta tana kuka tana surfa bala'in cewa na  ga irin bugun da akayi mata ko in tambaya, kuma tasan wannan mayyar ɗiyar dake hannu na ce ta aikata haka.

Shuru nayi da ita domin ni bani biye Gaje in naga tana saida hali, haka muka ci gaba da rayuwa cikin gidan nan da daɗi babu daɗi ina tsaye kan iyalina ba tare da Gajiyawa ba duk da irin rashin mutumci na gaje.

A haka har aka yaye Kulu ita kuma Lubna dama tun tana da wata takwas ta fara tafiya da ƙafafunta, wannan tafiya fa da mutane suka ga tanayi ta jawo cece kuce nan suka ci gaba da kiran ta ɗiyat Aljannu wasu kuma suce mayyace, ban damu da duk wani abu da mutane ke fada ba nidai alƙawari na ɗauka duk rintsi zani riƙe Lubna tamkar ɗiyar da nahaifa.

Duk duniya babu wanda Lubna ta yarda dashi daga ni se Ɗiyar makwafcina wato Saratu, Saratu na daga cikin mutanen da basu taba nuna kyama ga Lubna ba, duk duniya ita ce ƙawa ɗaya tilo wurin Lubna wadda hatta iyayenta sunsha kama ta su buga akan ta rabu da Lubna amma abun yaci tura domin kafin ta gama kuka bugun da aka yi mata zata sulale ta dawo wurin Lubna.

Suna da shekaru Uku a duniya na sanya su makarantar Allo ita da Kulu, tashin farko Kulu ta ƙi zuwa inda duk lokacin da zan kai su Kulu zata gudu daga gidan ne in na tambayi Gaje ba'asi se tace ita ma bata san inda take ba, baƙin cikin wannan turba da Gaje ke daura kulu yana matuƙar yi mani zafi domin nasan ba hanya bace me ɓullewa.

Nida kai na nike Shirya Lubna kamar ko yaushe in rufe mata rabin Fuskarta domin tun tashin ta tama saba da lullulin ta take fita, bazan taba mantawa ba wata ranar Laraba kamar yadda makarantun allo keyin hutu haka na bada kuɗin hutun Lubna bayan na kaita makarantar na juyo, kasancewar ita da Saratu suke dawowa yasa ban maida hankali wurin zuwa in ɗauko ta ba har lokacin tashi yayi, afujajan naga Saratu taja dogon Birki tamkar numfashin ta zai fita.

A rikice na fara tambayar ta miya faru, amma kash! Halin da take ciki  ta kasa furta koda kalma ɗaya ce.

"Baba wasu mutane daban san su waye ba sun tare Lubna."
Wanna ita ce maganar da Saro ta samu damar furtawa.

Bansan lokacin da na miƙe da gudu nabar ƙofar gidan cike da tashin hankalin abinda zai iya faruwa da Lubna, tafiya nike amma sam bani ganin gabana burina shine inyi tozali da amanar da aka bar mani.

Cincinrin don mutane nagani sun zagaye wani  abu kowa na tofa albarkacin bakin shi, tunkaro wurin da nayi ne naji jama'ar wurin na furta "Yawwa ga Mahaifinta nan." gabana ne yayi wata mummunar faɗuwa.

Buɗe mani hanya aka yi na riƙa ratsa taron jama'ar dan ganema idona abinda ke faruwa, wani wawan birki naja cike da zallar tashin hankali ganin Lubna kwance ƙasa kamar gawa.

Rungumeta nayi Tare da furta "Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un Lubna mi ya same ki."?
Na faɗa cike da tsantar tashin hankali.

"Wani mutum ne ya kama hannunta suka nufi wata hanya, ga abinda Saro ta fada mana ya yanki gashin kan ɗiyar ka ganin shi da mukayi tare da ita  nuho shi ne yasa ya gudu ba muyi nasarar kamashi ba, abinda zamu fada maka ka kula da ɗiyar ka Ubangiji ya jarabceta da lalura wadda muna kyautata zaton mutumin nan tsafi zai yi da wani saahe na jikin Lubna Allah ya toni asirin shi bamu kama shi ba."
Wani mutum dake gaf da Lubna ya faɗa.

Daukar Lubna nayi tare da nufar gida ilahirin jikina na kyarma, wuri na samu tare da kwantar da ita ruwa na ɗebo a hankali na rika shafa mata shi a fuska doguwar ajiyar zuciya taja  a hankali ta fara buɗe idanunta tare da sauke suna kai na.

"Sannu Lubna! Ubangiji ya baki lafiya."
Bata ce uffan ba sai kallo na da take faman yi.

Duk da Gaje tasan abinda ya faru amma kallon arziƙi ban isheta ba se ma waƙar ta da takama yi ta kallon mu.

Tabbas an yanki gashin Lubna domin ga inda aka yanka nan na gani, tun daga ranar nasa a raina zani linka kula da Lubna, shekaru suna karuwa lokaci na kara ja a yanzu kimanin shekarun Lubna goma sha biyar ita da Kulu.

Wahala ta duniya babu wadda Gaje bata ba Lubna ba komi na gidan nan Lubna ce mai yin shi tun abin na damu na har ya dena domin Nasan Gaje bata da imani tun ƙuruciyar Lubna, duk wani abu da zan hana asa Lubna tofa gaje shi take ƙoƙarin ganin ta sanyata, Lubna takanyi kuka tamkar ranta ze fita ganin yadda mahaifiyarta ta tsane ta, nine me koƙarin kwantar mata da hankaki amma Gaje kam tayi nisa

Munyi faɗan da bamu taba yiba akan tura Lubna debo ruwa amna Gaje taki kiyayewa, sam bani ƙaunar ɗibar ruwan nan domin ina sane da cutarwar da yaran unguwar keyima Lubna gami da ci mata mutumci amna Gaje ta gagara denawa.

Kulu kuwa sam bata aikin komi domin tun tana karama Gaje ta gama dasa mata tsanar yar uwarta.

A wani yammacin Alhamin ina bayan la'asar dawowata daga kasuwa zaune nike ƙofar gida domin zaman gidana ya xame mani ƙarfen ƙafa bani da damar shiga in zauna kafiya se Gaje ta tayar mani da hankali, Lubna ce ke share gidan tamkar yadda ta saba, tsautsayi Gaje tazo wuce wa kura ta dirar mata a kafa, ɗauke Lubna tayi da wani mahaukacin mari tare shaƙar wuyanta.
"Mara tarbiyya mara ɗa'a wato keda Uban naki kun haɗa kai yana koyar dake yadda zaki rika ƙuntata mani cikin gidan nan, to karyar ki tasha ƙarya yau zaki gaya mani dalilin watsa mani ƙasa a kafa da kikayi."

Haƙurin da magiyar da naji Lubna nayi ce ta sanya ni shigowa gidan afujajan, sai dai ina shigiwa Lubna ta fasa wata kara sakamakon gama mata kai da bango da Gaje tayi, nan ta sulale kara jikinta na wata irin kyarma.

Takaici shiya hanani tanka ma Gaje domin nasan in nayi magana bakina zai iya furta kalmar da ba'a so dan haka shuru nayi tare da nufar Lubna.

Mutuwar tsaye nayi ganin Lubna nayin abinda tunda take bata taɓa yiba, wata irin birgima cikin ƙasa kanta kuma yayi sama tana wasu irin surutai gami da shure_shure.

A lokacin abu daya raina ya bani shine in rufe gidan domin ga dukkan alamu babu lafiya, dawowar da zanyi kunnuwa na suka fara jiyo mani ihu Gaje tana kakarin mutuwa.

A guje na kasara shigowa gidan, Lubna ce ta shaƙe Gaje da hannu ɗaya ta ɗageta sama, duk yadda nayi ƙoƙari kwatar Gaje amma abun yaci tura domin Lubna ta zama tankar yunwataccen zaki da kayo kanta zata nufoni tare da kawo mani mugun hari, Gaje kam tsabar azaba ta Sume.

A ranar naga tashin hankalin da ban taba ganin irin shi ba, domin duk wani kayan amfani dake tsakar gidan nan seda Lubna ta farfasa su, ƙoƙarin guduwa daga gidan da naga tanayi shine ya sanya nayi saurin ruƙota gam a jikina, amma ina Lubna tayi wani irin ƙarfi tamkar na rike garwashin wuta haka naji.

Duk addu'ar da tazo bakina haka na riƙa karantowa tare da tofe Lubna, wani nannauyan bacci ne ya ɗauketa.

A hankali na fara bin gidan da kallo ganin irin 6arnar da Lubna tayi, tabbas rayuwar ta na cikin hadari ubangiji ya baki ikon cinye wannan jarabawa.

Makwafta kuwa kaf abinda ya faru suna ji, Bugun ƙofar gidan da naji anayi ce ta sanya ni tashi na buɗe.

Mahaifin Saratu mutumin kirki shine shi na gani tsaye cike da jimamin abinda ya faru, gaisawa mukayi tare da shigowa daga cikin soron gidan.

"Malam Sule ni ko ba zaka haɗa ma Lubna neman temako dana gargajiya ba."?
Malam garba ya fada.

"Eh to! Nima nayi tunanin haka amma  ni abinda nike gudu kada inje su fara yi mani jaye_jaye shine abinda nike gudu."

"Kada ka damu wannan malamin addini ne kuma ɗan uwa na ina tunanin insha Allah matsalar ka tazo ƙarshe."

Nikam jin yadda malam Garbe ke fadar malamin nan na yadda muje in Allah ya kai mu.

Koda Gaje ta farka na ɗauka wani sabon hauka zata 6alke dashi amma se naga sabanin haka domin tana samu ta farka ɗaki ta shige ba tare da tace ma kowa komin ba

Lubna kuwa har magriba saratu na kusa da ita amma sam bata farka ba, ganin dare ya fara yasa nace saratu ta tafi gidan su da safe tazo taga yadda jikin ta ya kasance.

Zaune nike a gefenta ina me ƙara tofa mata addu'o'i hannunta ne ya fara kyarma a hankali ta fara buɗe idanunta tare da sauke su a kaina, sannu na hau jero mata.

Ƙoƙarin tashi take, hannu tasa tare da dafe kanta dake barazanar tarwatsewa.
"Baba miya faru dani."?
Lubna ta fada cikin wahalalliyar murya.

"Bakomi Lubna ki kwanta kiyi bacci jikin ki ya samu hutu."

Bata musa ba haka ta nemi wuri ta kwanta amma jikinta sam babu daɗi, ga rafin ruskarta da take ji tamkar ana zuba mata tafashasshen ruwan zafi.

Asubar fari na sanar da Gaje inda zamuje da Lubna buɗar bakinta sai cewa tayi.
"Duk ma inda zaka da ita kaje, nida take neman rayuwata, in ma kun tafi Allah ya haɗata da ajalinta kowa ya huta."

"Bakin ki ya koma maki, Ubangiji ya shiga tsakanin Lubna da muguwar fatan da kika yi mata."
Na karasa maganar tare kiran Lubna muka fice.

Kai tsaye gidan Malamin muka nufa, bayan mu gaisa mun sanar dashi abinda ke faru bukatar ta bude fuskarta yayi.
"Malam ganin fuskarta ba alkhairi bane kamar yadda na sanar dakai babu me ganin fuskarta ya kwana a raye."
Na fada cikin ladabi.

Magunguna ya bamu tare da wasu addu'o'i yace mu dawo bayan kwana biyu, godiya mukayi tare da kamo hanyar gida.

Lafiya lau ta fara aiki da magungunan babu wata matsala, ashe wasa farin girki wannan shine mafarin duk wani al'amari da zai biyo baya.

Kwana ɗaya da amso maganin da asubar farko Malam Garba ya kira ni yake sanar dani abinda yayi ƙololuwar tayar mani da hankali, fitowar da zanyi tsakar gida na jiyo iyalan Malam garba wasu na rafka salati wasu kuma sun fara ihu, a gigice na bude gida tare da ficewa ko takalmi babu ƙafata....

A ci gaba da Subscribe👇🏻👇🏻👇🏻
https://youtube.com/channel/UCFefdIP2piaSVv-IAANrzBQ
👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽👆🏽
Idan kuka latsa zaibude saiku latsa inda aka rubuta *SUBSCRIBE da jan rubutu*
*Aslm dan Allah yan uwa ga YouTube channel dina nan kumin subscribe za muna maku posting na magunguna kala kala da cooking kala kala da karatu tuka da novels masu zafi.👏🏼👏🏼👏🏼👏🏼👏🏼*

*MEEN@RT...✍🏻*
[8/30, 9:28 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE4️⃣8️⃣_4️⃣9️⃣*

```Assalamu alaikum masoyana na nesa dana kusa na fili dana boye ina me ƙara baku hakurin jina shuru da kuka,yi kwana biyu  jiki da jini na ɗan yi ciwo amma yanzu Alhamdulillah masu kira da masu turo saƙo duka na gani ina matuƙar godiya da nuna soyayyar ku a gare ni nagode matuƙa Allah ya bar zumunci```

...Tsabar firgice da ruɗewa da nayi ko sallama banyi ba haka na afka gida, Malam Garba cike da tashin hankali na fara tambayar shi lafiya

Da runannun idanun shi ya ke ta kallo na bakin shi ya kasa furta koda kalma daya ce, Zulai matar malam Garba i ta ce tayi mani wata fincika hawaye na fita a idon ta.

"Hankalin ka ya kwanta Kasa Mayyar ɗiyar ka ta halaka mani yayana Allah ya isa tsakanin mu da kai kun cutar dani, tun da naji malam yace zai raka ka wurin yayana nasan mayyar ɗiyar ka se tayi ajalin shi."
Zulai ta ƙarasa maganar tare da fashewa da kuka.

"Baki da hankali Zulai! Mijin wata zaki cima kwala a gaba na, wannan wane irin rashin tarbiyya ne, shin baki yarda da ƙaddara ba, kina ji dai aka ce yayanki ruwa ya faɗa ya mutu."
Malam garba ya ƙarasa maganar tare da banbare zulai daga shaƙar da tayima Malam sule daya daskare tamkar Butun-butumi.

"Shi yaro ne da zai faɗa ruwa ace ya kasa fita, wannan wata ƘULLALLIYA ce, (Sunan littafina

na gaba.) aka shirya mana kuma hukuma ce zata rabani da iyalan malam Sule se an bi mani kadin kashe mani ɗan uwa da suka yi."
Ta ƙarasa maganar tare da fashewa da kuka.

Ganin Zulai zata tara masu jama'a yasa Malam Garba kamo Hannun malam sule suka fito waje.

"Dan Allah kayi haƙuri kada maganganun Zulai su dameka nasan tana cikin zafin rashin yayan ta ne da tayi, kada ka zargi ɗiyar ka ni nasan lokacin Malam ne yayi shiyasa ya rasu sedai muyi mashi fatan samun rahamar Ubangiji, yanzu kaje mu shirya domin mu samu halartar jana'iza."
Malam Garba ya ƙarasa maganar cikin sigar rarrashi.

Haka na dawo gida ba tare da na iya furta ma garba koda kalma ɗaya bace, kafin a shirya Gawa har labari ya bazu cewa Lubna ita ce wadda ta Lashe kurwar Malamin.

Kafin a ɗauki wani dogon lokaci tuni labari ya bazu a gari kowa da yadda yake bada labarin

Dawowata gida nan na tarar da abinda ya kusa sanya ni ƙaramin hauka, ashe bayan tafiya ta labari har ya isa kunnen Gaje cewar Lubna tayi kisa, bugun da na iske Gaje tayi ma Lubna a ranar seda na zubar da hawaye domin a halin suma na Iske Lubna tamkar matacciya

Abinda ban taba tunani a mafarki zan aikata ba shine na aiwatar ma gaje, wani wawan Mari na dauke ta dashi cike da ƙunar zuciya.

Gaje kuwa tsabar mamaki daya kasheta kasa motsawa tayi daga inda take face kallo na da take cike da bayyanan nen mamakin abinda nayi mata.

"Ni zaka mara? Akan wannan mara tarbiyyar ɗiyar taka zaka ɗaga hannun ka wanke ni da mari, Ni zaka mara Suleman saboda waccan ɗiyar taka da ta zame ma mutane annoba, kamar yadda ka ɗaga hannu ka wanka mani mari ina roƙon Allah yasa Lubna ta zama ajalin ka, kamar yadda ka ɗaga kannu ka wanke ni da mari ina fatan Allah ya sa Lubna ta illataka kafin mutuwar ka ta riske ka."
Gaje ta ƙarasa maganar tare da shigewa ɗaki a matuƙar fusace fuu tamkar kububuwa.

Sanin in dai Gaje ce zata aikata fiye da haka yasa banbi ta kanta ba Na fara ba Lubna taimakon gaggawa, Saratu ce ta fado gidan ciki da tashin hankali domin ita ma yanzu ta dawo daga gidan gaisuwar tana ƙoƙarin sanar da Malam Sule abinda ke shirin faruwa, domin iyalan mamaci ne suka yi dandazo tare da tunkaro wadda tayi sanadiyyar mutuwar Ɗan uwansu wato Lubna, amma tashin hankalin da ta iske Lubna a ciki yasa ta kasa furta koda kalma ɗaya ce ta fara kuka tana rirriƙe ƙawar ta ta data fuskanci lallai ciwon ta ne zai tashi.

"Saratu ki fice daga gidan nan na roƙeki Ciwon Lubna ne ya tashi kada ta ji maki ciwo."
Malam Sule ya ƙarasa maganar da karyayyar murya.

"Babu inda zani je, ba zani tafi in bar Lubna cikin wannan halin ba ka gafarce ni na roƙe ka, Alƙawari na ɗauka koda Lubna zata zama ajalina bazan taba barin ta ba."
Saratu ta ƙarasa maganar hawaye na bin fuskarta.

Kafin su ankara tuni Lubna ta yi kukan kura ta watsar dasu gefe ta miƙe tana waige_waige, fuskarta kuwa tamkar wata amarya an nannade ta se rabin fuskar ne kaɗai bayyane, Gaje ce ta fito jin muryar saro cikin gidan, a fusace Gaje ta taho da niyyar balbale saro da masifa amma ganin Lubna da tayi tamkar wata zakanya yasa Gaje fallawa da gudu zata koma ɗaki, wani wawan burki Gaje taja gani uwar Garke ta bayyana ƙofar ɗakin tana kyalkyata dariya, babu yadda Gaje ta iya haka tayi tsaye domin tayi imani ƙara Lubna ta azabtar da ita da dai ta faɗa hannun Uwar Garke.

Wata mashahuriyar shaƙa Lubna tayi ma Gaje tare da ɗageta da hannu ɗaya ta shiga bugawa da ƙasa, ɗaukar Gaje Lubna tayi tare da bugata bisa babbar tukunyar ƙasa wadda suke zuba ruwa, kururuwa gaje keyi tamkar Zata fasa dodom kunnen jama'ar dake wurin.

Kulu ce ta fito jin ihun mahaifiyar tata, ganin ciwon Lubna ya tashi yasa Kulu juyawa tare da sheƙawa a guje, Uwar Garke ce ta cafko ƙafar Kulu me kama da kafafun sauro taci gaba da jibga, sudai Su Malam Sule da Saro sun ga Kulu na ihu amma basu ga mike faruwa da ita ba, malam Sule ne kaɗai me ƙoƙarin ceton  Gaje daga Hannun Lubna amma Saro cewa tayi sam ba zata ce ci Gaje ba.

Duk yadda Malam sule yaso ya kwaci Gaje amma abun yaci tura domin da ya zo amsarta Lubna zata taso ma shi tare da kawo mashi mugun hari.

Dole yana ji yana gani haka Lubna ta ci gaba da jibgar Gaje babu ji babu gani, hayaniyar mutane ce ta fara ziyartar mutanen dake cikin gidan meda hankalin su ga ƙofa.

Mutane ne ɗauke da makamai Maban-banta suke tururuwar shigowa gidan Malam Sule a matuƙar fusace domin yau alƙawari suka ɗauka Lubna se ta baƙunci lahira kamar yadda ta yi sanadin mutuwar ɗan Uwan su.
Jiki na ciri mahaifin Lubna ya sha gaban cincirindom mazan dake neman ƙarasawa in da Lubna take.

"Bayin Allah lafiya zaku shigo mani gida ba tare da neman izini na ba, mi kuke nema da bazaku nemi izini a wuri na ba."?
Cewar Malam Sule cike da bacin rai.

"Ka aje wannan annobar a gidan ka har zaka yi tunanin lafiyace zata kawo mu, kamar yadda ka haiho annoba tayi sanadin mutuwar ɗan uwan mu to muma nan ba se munjira wata hukuma ba mune nan zamu ɗauki doka a hannun mu ta hanyar aika waccan Mayyar ɗiyar taka inda ta aika ɗan uwanmu."

Wani ƙaƙƙarfan mutum ya ƙatasa maganar cikin fushi.

"Sai dai ku fara kashe ni kafin ku isa gareta."
Saratu ta fada tare da shan gaban su.

Cike da 6acin ran abinda Saratu tayi suke kallonta, kenan batada kishin yayan mahaifiyarta da aka kashe har take wannan iƙirarin, wani zazzafan mari mutumin ya ɗauke ta dashi.
"Sakarar banza mara kishin ɗan uwan mu, kina bani hanya ko se munbi ta samanki mun wuce."
ƙanin mamacin ya fada rai a matuƙar bace.

Haka suka riƙe mahaifin Lubna dake ƙoƙarin haka su cimma burin su gefe guda shida Saro suka tunkari Lubna da ta gama jibgar Gaje.

Uwar Garke kuwa wani murmushin mugunta tayi domin tasan yau tabbas zata yi ƙeta irin wadda bata taba yi ba, mutumin dake ƙoƙarin fizgo Lubna yana gaf da isa gare ta wata mahaukaciyar guguwa me matuƙar Karfi ta turniƙe gidab lokaci ɗaya aka kece da mahaukaciyar dariya...

Babu yawa mu haɗe gobe in shaa Allah.

*MEEN@RT...✍🏻*
08133562798
[8/31, 6:47 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
```

https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE 5️⃣0️⃣_5️⃣1️⃣*

...Guguwar nan haka ta turniƙe gidan ko tafin hannun ka baka iya gani, sannu a hankali ihun mutane ya fara cika dodon kunnen su Malam Sule.

Bulalai ne suka bayyana ba tare da kaga ne bugun ka ba sedai kawai kaji saukar su ta ko ina, nan fa maza suka fara kururuwar neman temako makaman dake hannuwan su duk suka zube nan suka fara neman hanyar guduwa cike da nadamar shigowa gidan su Lubna domin basu yi tunanin hatsabibancin ta ya kai haka ba.

Uwar Garke nan ta shiga laftarsu suna zabga ihu, an ɗauki lokaci me tsayi kafin ƙurar guguwar ta fara lafawa sannu a hankali aka fara hango mutanen dake yunƙurin kashe Lubna baje a ƙasa suna mai da numfashin wahala, da dai suka ga guguwar ta lafa a guje suka riƙa ficewa a gidan ɗaya bayan ɗaya.

Tun daga ranar mutane ke matuƙar tsoron Lubna domin sun ji lokacin da take laftar mutanen nan suna ihu, Gaje kuwa ta ɗauki lokaci tana shakkar Lubna kafin ta manta abinda ya faru ta koma baƙin halin ta, abinda zai baka mamaki shine koda wasa yan uwan mamacin basu tada zancen bugun da akai masu ba balle kuma wani yayi ƙoƙarin ɗaukar mataki.

Tsagaitawa Malam Sule yayi tare da kallon su Malam Saif da suka tsura ma shi ido cike da zallar mamakin wannan al'amari gami da tausayin rayuwar Lubna, ruwa aka bashi ya kora tare da ci gaba da bada labarin.

"Tun daga ranar mutanen garin da kuma makwafta da sunji ciwon Lubna ya tashi haka suke kulle gidajen su ba tare da ansa mu mai ƙarfin imanin da zai kawo mana ɗauki ba, nasha tunkarar Malamai da dama da batun ciwon Lubna amma da sunji labarin abinda ya faru da ɗayan malamin nan kai tsaye suke bijirewa su ƙi taimako na, nasha baƙar wahala akan Lubna wadda badan na jajirce da addu'a ba da tuni na rasa rayuwa ta, ni ne kaɗai wanda Lubna zata raba taji sanyi a zuciyar ta amna banda Gaje ko alama batasan miye soyayyar Uwa ba, ta rayu cikin kaɗai ci da zallar damuwa, A wannan rana a dai_dai wannan lokaci na sauke nauyin dake kai na, na faɗar gaskiyar lamari, Lubna waɗan nan sune iyayenki na ainahi."
Malam Sule ya ƙarasa maganar hawaye nabin fuskar shi na rabuwa da wadda yana ji a jikin shi zai iya sadaukar da rayuwar shi saboda ita.

Wuri yayi shuru bakaji sautin komi sai shasshekar kukan Murja da kuma Gaje, Hajiya Salima kuwa a ranar tayi kukan da bata ta6ayin irin shi ba, domin tunda take bata ta6a jin labari me matuƙar ban tausayi ba kamar wannan, tabbas Lubna abar tausayi ce tun tana jinjira rayuwar ta ke cikin garari.

Al'ameen kuwa ji yake ina ma zai samu dama kuma ace kisa ba haram bane, da kuwa tabbas babu abinda zai hanashi kashe Gaje domin ko a tarihi bai taba ganin marar imani kamar ta ba, wani irin tausayi hadi da ƙaunar Lubna ne yaji suna ƙara baibaye zuciyar shi,alƙawali ya ɗauka na kulawa da Lubna tare da rayuwa da ita koda ace fuskarta ba zata dawo dai_dai ba, Baƙar mace face kuma kai baka son baƙar mace."
Wani sashe na zuciyar shi ya tunatar dashi, wani tsoki yaja domin sai yanzu ya fuskanci baƙar mace ba abar wulaƙantawa bace, baƙar mace tana ɗauke da wani kyau da baiwa ba kowa ke fahimtar shi ba.

Alhaji Jadda kuwa jin yadda jinin jikinshi tayi rayuwa cikin ƙunci da kuma zallar baƙin cike bata san miye gatan uwa ba, ji yayi zuciyar shi tayi baƙiƙirin a matuƙar fusace ya dubi Hajiya Murja.
"Kin cutar dani cutarwa mafi muni, Murja Jini na ɗiyar dana haifa ku ka salwantar saboda cikar burin ku, Murja kije keda Allah bazan taba yafe maki ba har abada, kije na sake ki saki biyu."
Alhaji Jadda ya ƙarasa maganar cike da bacin rai

Kaurewa mutanen wurin suka yi da salati cike da muwar jim abinda mahaifin Hibba ya furta.

"Subhanallah! Malam Jadda bai kamata ace kayi saurin ɗaukar mataki cikin fushi ba, kowa yasanan cutar dakai amma haƙuri shi ya kamata kayi komi da kaga ya samu bawa da sanin Allah, Murja ta tafka babban kuskure wanda tunda nike bantaba jin in da Uwa ta ɗauki ɗiyar da ta haifa jiM kaɗan bayan haihuwarta ta bada ta kyauta domin cikar wani burin su, babban abinda ke bani mamaki shine yadda murja ta reni Aljana ba tare da ta sani ba, domin kowa ya sani mutum bai iya haihuwar ɗan Aljani."
Cewar Malam ya me maida duban shi ga Murja da take darzar kukan nadamar sakin da mijin ta yayi mata, yanzu da wani ido Lubna zata kalle ta, anya ta yima Lubna adalci kuwa?anya Lubna zata kalleta a matsayin mahaifiya a gare ta.

Mahaifin Murja kuwa tsabar rikicewa miƙewa yayi tare da fara sabbatu domin tuni sakamakon abinda ya aikata ya fara samunshi.

Hibba dake Kusa da Lubna ce ta fara magana kamar haka;
"Kada kayi mamakin jin na rayu a gidan Murja ba tare da an gane ni, tun bayan rabani da mijina da suka yi na wanzu cikin baƙin ciki da zallar damuwar wannan cuta da akayi mana da rana tsaka sun ɗauke mani mijina tare da sanya shi aikin da bai da yadda zai yi domin su haɗa shi da babban Bokan da ko a ƙasar Indiya yayi fice, da rana tsaka suka raba soyayyar dake tsakanin mata da miji tare da bari na ni ɗaya ina rayuwa tamkar bani da kowa, bincike na fara domin gano waɗan da suka aikata mani wannan zalumci amma duk binciken da nayi ban garo in da aka kai mani miji ba domin bokan yayi aikin da koda zani zagaye duniya ina neman shi bazan taba ganin shi ba sai da na gano waɗan da suka aikata mani haka wato Murja da mahaifinta, ina shirin baro indiya ne na samu labarin saukar su Murja ƙasar indiya, nayi farin ciki domin ko ba komi aikin da nike burin aiwatarwa zai zo mani da sauƙi.

Shiri nayi na musamman tare da shammatar Bokan da yayi aikin naga bayan shi domin

alƙawari ne nayi tunda aka raba ni da farin cikina nima sai na raba kowa da farin cikin shi, kai tsaye hotel ɗin da su Murja suka sauka na nufa cike da farin ciki na ɗaukar fansar da zanyi a kanta, cikin ƙanƙanin lokaci nayi nasarar shiga jikin Murja tare da burin hallaka abinda ta haifa ni kuma in maye gurbin shi, ranar da Murja ta tashi da naƙuda a ranar na ha shaƙe wuyan abinda ta haifa tun kafin ya iso duniya, na shammaci malam asibiti tare da maye Gurbin ɗiyar da murja ta haifa da ni, tun ranar nayi ma Murja illa domin na lalata mahaifarta ta yadda har abada ba zata sake haihuwa ba sai dai taga haihuwa wurin wasu, ganin yadda Murja ke masifar son abinda ta haifa nan naji lallai na samu hanyar da zani azabtar da rayuwar ta kamar yadda suka cutar da tawa rayuwar, na ɗauki lokaci mai tsayi ina cutar da Murja tare da bata tsoro domin nasan kota sanar da mahaifina bazai yarda ba, na kashe mutane da dama domin duk wanda naga yana ƙoƙarin tona mani asiri kauda shi nike, kai ne malami na farko da ya katse mani aiki ba tare da na ɗauki wani mataki ba, ka dakatar dani daga kashe Murja da nike niyyar yi domin badan kazo da wuri ba da tuni Murja ta baƙunci lahira."
Hibba ta ƙarasa maganar tare da jifar Murja da wani kallo me wuyar fassaruwa.

Malam Saif ne ya fara magana.
"Duk da an cutar dake amma kema kin cutar da waɗan da basu ji basu gani ba, Murja ita ce wadda tayi maki laifi shin ina za kije da Haƙƙin Alhaji Jadda da bai ji ba bai gani ba amma kina kashe mashi ɗiya, in Murja tayi maku laifin Shin miye laifi Jadda da kuma mutanen da kika riƙa karkashewa."?
Cewar Malam Saif cike da jimamin wannan lamari.

"Ko mi ya faru Murja da Mahaifin ta sune sanadi, bil'adama basu da tausayi suna da mugun hali yate da shiga gonar da ba tasu ba, ko yanzu da miji na ya bayyana ban fidda rai da sai naga bayan Murja."

Murmushi Uwar Garke tayi domin tasan wace ce Gul hatsabibiyar Aljana da ta zarta mijin ta hatsabibanci.

Aljanin jikin Lubna ne ya fara magana.
"Koda baku buƙata ba zani bar Jikin Lubna amma dole ne ina fita jikin ta Mamman zai haukace ba za'a jima ba zai mutu domin wannan shine sharaɗin da aka gindaya mashi kafin biyan buƙatar shi."
Aljani Gullam ya faɗa.

Wata zabura Hajiya Murja tayi jin abinda Aljanin ya faɗa
"Ni Murja na cuci kai na, na cutar da Mijina da kuma ɗiyata duk dan saboda cikar wani buri namu na duniya."
Murja ta ƙarasa maganar tare da fashewa da kuka.

Babu wanda yabi takan Murja domin kowa yasan abinda suka shuka ne zasu girba.

Malam Saif dubar Aljanin Lubna yayi.
"Ka cutar da jinjirar da bata ji ba bata gani ba, kuma bayan haka ka nakasa mata fuska ta koma rabi ta na miji shin fuskar ta da ka lalata zata iya dawowa dai_dai."
Cewar Malam Saif.

"Tabbas Fuskarta zata dawo dai_dai domin nayi haka ne bada son rai na ba a yadda akayi yarjejeniya dani Lubna a matsayin mallaki na take, Malam kai Mutum ne me matuƙar adalci dan haka zani fita daga jikin baiwar Allah nan ba tare dana cutar da ita ba jikin ta zai dawo tamkar yadda na ko wace mace yake, sannan kuma nida mata ta zamu amshi addinin ku."

"Allahu Akhbar!"
Mutanen cikin falon suka yi kabbara a tare.

"Na matuƙar jin dadin wannan al'amari Godiya ta tabbata ga Ubangijin mu me rayawa da kuma kashewa Haƙiƙa  Allah gafurun rahimun ne ku musulumta da kyakkyawar niyya Ubangiji me gafara ne zai gafarta maku dukkan wasu zunuban da kuka aikata madamar kuka musulumta da niyyar ba zaku sake aikata abinda kuka aikata a baya ba, kuyi tuba ta haƙiƙa."

"Malam ni na aikata kisa da dama shin Ubangijin ku zai gafarta mani."?
Hibba ta faɗa.

"Ubangiji Me gafara ne madamar kika yi taubatunnasuha Allah zai yafe maki."

Uwar Garke ce ta fara magana ita ma.
"Malam a baya nima ina kallon musulmai ne da baƙin fentin da su Alhaji Mamman suka shafa masu, amma a yanzu na fahimci a cikin ko wace al'umma akwai mutanen banza da kuma na kirki, ina so in shiga addininku domin ya jima yana burgeni."

Murna farin ciki sune suka saka Malam Saif hawayen farin ciki, domin bai manta hadisin Manzon Allah da yake cewa wa mutum ɗaya ya musulumta ta dalilinka ya fi alkhairi da abaka jayen raƙuma.

A tare ya laƙana masu kalmar shahada suka me me ta, suna ya buƙaci kowanen su daya zaba inda Hibba ta zabi Aisha mijin ta kuma ya zabi musa, uwar garke kuwa shuru tayi domin ita har ga Allah tana son sunan ta.

"Shin malama musulumce suna na za'a iya ci gaba da kirana dashi ba tare da an sauya mani

ba."?

Murmushi Malam Saif yayi.
"Eh to amma mafi aa la ki zabi wani sunan duk da dai sunanki bai da aibu amma mu in kakaji ance Uwar garke ana nufin kodai kana da wani garken dabbobi to babbar cikin su ita ake kira uwar Garke."
Malam Saif ya faɗa.

"Na za6i LUBNA domin ina ƙaunar sunan kamar yadda nike ƙaunar me sunan."
Babu musu nan aka laƙana mata Lubna.

Aisha da Musa kuwa nasiha malam Saif yayi masu dasu nemi Malami a cikin Aljannu ƴan uwansu su nemi ilimi a wurin shi, haka suka yi godiya tare da neman gafata wurin Alhaji Jadda yafe masu yayi nan suka bace daga wurin.

Lubna kuwa Wani bacci ne yayi awon gaba da ita.

A yadda Malam Sule keji yau babu wanda ya kai shi murna da farin cikin samun lafiya da Lubnar shi tayi.

Kofar falon ce aka banko da ƙarfi tamkar za'a karya ta, duk mutanen dake cikin falon duban su ne ya koma ga masu ƙoƙarin shigowa.

Mahaifan Leemcy ne rirriƙe da Leemcy da kallo ɗaya zaka yi mata ka tabbatar bata cikin gayyacin ta, Dariyar gefen baki Uwar Garke tay domin tasan yau asirin abinda suke boyewa zai tonu....

*MEEN@RT...✍🏻*[9/2, 12:01 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*
```

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE 5️⃣2️⃣ 5️⃣3️⃣*

...Cike da mamaki suke kallon Mahaifan Leemcy da ke ƙoƙarin kwantar da ita bisa ɗaya daga cikin kujerun falon, ganin yadda ido ya dawo kansu yasa Mahaifiyar Leemcy fashewa da kuka.
"Dan Allah ku ceci rayuwar ɗiya ta, yau kimanin kwanaki biyu kenan da shigarta wannan hali duk wani magani da zamu yi mata a banza domin yadda take ko motsi bata yi."
Mahaifiyar Leemcy ta ƙarasa maganar ta mai share hawayen fuskarta.

Hajiya Salima kallon su tayi cike da matuƙar mamaki domin ita sam tama manta da cewa Al'ameen ɗinta na da wata mata bayan Lubna, to mi ya samu Leemcy ta dawo haka tamkar gawa."?

Al'ameen kuwa tsabar takaicin ganin Leemcy yake ji, kallo ɗaya yayi mata yaji wata iriyar tsanarta ta ɗarsu a zuciyar shi, to mi ma ya kai shi ya auri Leemcy yarinyar da ta gama zubar da mutumcin ta a kwalta."?
Ya hau tambayar kanshi.

Malam Saif kuwa Kallon ta yayi cike da mamakin domin da gani kasan Aljannu ne suka bugeta.
"Mi ye musammabin abinda ya faru da ɗiyar ku har ta samu kanta cikin wannan halin."?
Malam Saif ya jefa ma Mahaifin Leemcy tambayar.

"Ranar wanka dai ba'a ɓoyon cibi, ka haifi Ɗa amma baka haifi halinshi ba, tun bayan auren Halimatu bamu sake sanin halin da take ciki ba domin muna ganin yanzu kaf nauyin ta yana ga mijin ta, mun ɗauka har cikin ranmu cewa Aure ya kimtsa Halimatu ashe abun ba haka yake ba, sam bata bar mugayen halayen da take yi ba, da yammacin marecen jiya ne aka kiramu da Number Halimatu cewa muzo wani babban hotel na garin nan ɗiyar mu na cikin wani hali, a gigice muka kwasa nida mahaifiyarta muka nufi Hotel ɗin, a yanayin da muka iske Halima yayi matuƙar muni domin batasan wanda ke kanta ba mimmiƙe kamar Gawa muka iske ta, tambayar ma'aikatan wurin muke me ya same ta yaushe tazo hotel ɗin, nan suke sanar damu ita da wani sauratin ta ne suka kama ɗakin a ƙalla sunyi kimanin mako guda a Hotel ɗin, yau da safe ne wanda ya kama ɗakin yaje ya biya mu kuɗin zaman da yayi a ɗakin abun mamaki muna zuwa ɗakin sai muka iske wannan baiwar Allah tamkar gawa bata san wanda ke kanta ba, faɗin tashin hankalin da muka shiga a wannan lokacin ɓata lokaci ne, Mahaifiyar ta kuka ta fashe dashi domin tasan wannan na daga cikin abinda take gudu ma shagwaɓa Halima da nayi, cike da takaicin cin amanar aure da Halima tayi muka kwasheta muka nufi asibiti amma a banza Ƙin amsarta suka yi domin sun lura ba ciwon asibiti bane, duk wani malami da muka kira a banza

domin kuwa babu abinda ya sauya, munyi yun ƙurin sanar da Al'ameen halin da ake ciki amma muna tsoron irin hukuncin da zai ɗauka na jin matar shi na tarayya da wani a can hotel, munje gidan Al'ameen bamu same shi ba shine muka yanke shawarar kawo ta nan gidan domin muna da tabbacin Al'ameen na nan."
Mahaifin Leemcy ya ƙarasa maganar cike da jimamin wannan al'amari.

Shuru kake ji falon yayi domin wannan al'amari ya zama ruwan dare mace ta riƙa cin amanar auren ta saboda rashin tsoron Allah.

Cike da zallar mamakin hali irin na Leemcy Hajiya Salima ke kallon ta "kenan shi yasa da ta kirata ta sanar da ita halin da Al'ameen ke ciki ko zuwa bata yi ba, ashe tana can tana sheƙe ayar ta, Ubangiji ka ƙara shirya mana zuri'a."
Hajiya Salima ta ƙarasa maganar zucin.

Al'ameen Kuwa wani malolon baƙin ciki ne ya tokare mashi zuciya.
"Matar da yake aure ita ce A hotel ita da wani suna gantalewa? Nikan mi ma ya kai ni na auri Leemcy."?
Ta tambayi kanshi.

Mahaifin Al'ameen ne ya fara magana.
"Amma Halima bata kyauta ba ta cuci rayuwar ta, domin ba kowa ta cuta ba sai kanta, shiyasa ake so a duk inda kake ka kasance mutumin kirki yanzu da mutuwa Halimatu tayi a halin da take ciki tace ma Allah mi, ta mutu tana zina alhali da auren ta wa'iyazubillah! Ubangiji ka tsaremu da aikata duk wani abu daya saɓa maka, kun yi sa'a domin kuwa wancan da kuje gani Malami ne in da rabo Halimatu zata iya warkewa."
Mahaifin Al'ameen ya ƙarasa maganar tare da kallon Malam Saif.

Umurtar mahaifiyar ta yayi da ta matso kusa ta riƙe ɗiyar ta.
"Malam kada ka wahalar da kan ka domin nice nan na bigeta."
Uwar garke ta ƙarasa maganar tare da matsowa kusa da Leemcy, hannu tasa ta shafi fuskar Leemcy, jikin Leemcy ne ya fara motsi kafin ta fara atishawa sai kuma ta Buɗe idanunta ta fara bin mutanen falon da kallo ɗaya bayan ɗaya, tozali tayi da Uwar garke dake gabanta zaune, wata irin zabura  Leemcy tayi sa'i ɗaya ta fara kurma ihu tana ƙoƙari bangaje mahaifiyar ta ta fice ɗakin.

"Innalillahi, la'ilaha illalahu, Amanar rasulu, li'ilafi ƙuraishi, Uwar Garke yau ni na shiga uku jama'a kuzo ku cece ni wayyo Uwar garke zata sabauta ni wayyi hu_hu jama'a."
Leemcy ta cika falon da ihu tamkar zata tarwatsa dodon kunnen jama'an dake falon.

"Ki natsu ki dawo cikin hankalin ki, waye ya aike ki yawon banzar ki da had zaki cika ma mutane kunnuwa da iface_iface."
Mahaifiyar Leemcy ta faɗa rai a matuƙar bace.

"Aljana ce, wallahi Aljana ce ku taimake ni ku barni in fice daga gidan nan, baku san wace ce uwar Garke ba ne."
Leemcy ta ƙarasa maganar jiki na kyarma.

"Baiwar Allah ki kwantar da hankalinki, a yanzu Uwar Garke ba zata cutar dake ba domin tana cikin jerin mu na musulmai."
Malam Saif ya faɗa.

"Wannan ya zama darasi a gare ki domin da ace da ƙarar kwana da tuni kin mutu bayan gama sabon Allah da kika yi alhalin kina da auren ki, wannan wane irin bala'i ne shiyasa ga mu nan fitintunu sun addabi Al'ummar mu ta ko ina, kina musulma ɗiyar musulmai amma kina aikata abinda ko wasu marasa addini ba zasu aikata shi ba."
Nan malam Saif ya shiga yima Leemcy nasiha me shiga jiki da ma duk wanda yake zaune a wurin.

Kuka sosai Leemcy keyi domin tunda take bata taɓa jin nadama makamanciyar wannan ta shigewa ta ba, juyowa tayi da runannun idanun ta tare da zubewa bisa guiwowin ta, tana me fuskantar Al'ameen.
"Ni me matuƙar laifi ce, laifin da in dai baka yafe mani ba tabbas zani haɗu da fushin Ubangiji, na roƙeka da Girman Allah ka yafe mani ko da zani ga da kyau a rayuwata, tabbas nayi abubuwa da dama dan ganin na aure ka, bani so ayi tone_tone nidai yafiyar ka nike nema."
Leemcy ta ƙarasa maganar tare da fashewa da kuka.

"Na yafe maki, muma Ubangiji ya gafarta mana, amma zama tsakani na dake ya ƙare domin bazan iya ci gaba da zama dake ba, ko da ace na zauna dake tofa zargin ki zan riƙayi kuma shi zargi yana kashe aure, dan haka kije na sake ki saki Uku."
Al'ameen ya ƙarasa maganar tare da Kallon Leemcy.

"Innalillahi wa'inna ilaihirrajiun."
Ita ce kalmar da mahaifan Leemcy suka furta cike da tashin hankali.

Leemcy kuwa taji daɗin sakin nan domin koba komi sun rabu da Uwar garke rabuwa ta har abada.

Cike da jimamin wannan ɗanyen hukunci da Al'ameen ya yanke Hajiya Salima ta fara magana.
"Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un Al'ameen har saki har Uku a gaban idon mahaifan ta."?

"Kiyi haƙuri, wallahi bazan iya ci gaba da zama da Leemcy ba."
Al'ameen ya ƙarasa maganar kanshi a ƙasa.

"To alhamdulillah domin ta wannan hanyar sakin shine maslaha, muddun zargi ya shiga

tsakanin ma'aurata yana kashe aure ne, sai dai muce Ubangiji yasa haka shine mafi alkhairi."

A tare suka amsa da Ameen.

Mahaifin Hajiya Murja kuwa tuni ya fara zabga ihu yana tona ma kanshi asiri duk wasu abubuwa daya aikata nan ya riƙa bayyana su yana zabga ihu.

Mutane da dama sun tausaya mashi amma da suka tuna ance kowa ya sai rariya yasan zata zubda ruwa, Murja kuwa kuka take tamkar ranta zai fita cike da nadamar abubuwan da suka aikata.

Mahaifan Leemcy bankwana suka yi tare da ficewa daga gidan, Malam Saif magungunan da za'a riƙa ba Lubna ya sanar dasu, tare dayi masu fatan alkhairi shima ya fice.

Idanuwanta ne suka fara motsi kafin ta fara ƙoƙarin buɗe su, tamkar wata baƙuwar duniya haka ta riƙa jujjuya idanun ta tana sauke su ga mutanen falon.

Cikin hanzari Hajiya Salima, Alhaji Jadda da kuma Malam Sule suka ƙarasa wurin Lubna dake ƙoƙarin tashi.

Masha Allah ita ce kalmar da duk jama'ar wurin suka furta yayin da suka yi tozali da Lubna da ainahin kyawunta ya bayyana, baƙa ce amma ko cikin baƙaƙen ita me kyau ce, fuskar nan ubangiji ya ƙawata mata ita da dukkan wani nau'i na kyau abun sai da ace masha Allah.

Al'ameen kuwa mutuwar zaune yayi domin kyau irin na Lubna tabbas bai ta6a tunanin za'a samu wata mace a cikin matan ma baƙaƙe da irin wannan kyau ba.

Yadda taga sun tunkaro ta ne yasa ta fashewa da kuka tare da faɗawa jikin Hajiya Salima, domin kaf abinda ya faru Lubna naji, taji komi taji yadda mahaifiyar ta tayi mata.

"Lubna yanzu ba lokacin kuka bane lokaci ne na farin ciki da miƙa godiyarki ga Allah daya nuna maki samun lafiyar ki, kuka ba naki bane."
Malam Sule ya faɗa cike da kaunar Lubna.

"Zo gare ni ɗiyata, zo in ji gumin jikin ki, kin rayu ba tare da ni ba, an rabamu tun kina jaririya, in ba yanzu ba bantaba sanin cewa ina da wata ɗiya a duniyar nan ba."
Alhaji Jadda ya karasa maganar tare da goge guntun hawayen da yaji sun gangaro mashi.

Daga ita har Jadda kuka suke cike da so da ƙauna wanda ke tsakanin ɗiya da Uba.

Murja ko tamkar ta6a66iya haka ta zube a gaban Lubna tana roƙon ta cewa ta yafe mata.

"Na cutar dake, nasan da wuya ki kalkeni a matsayin mahaifiyarki saboda irin cutar da nayi maki

babu wata mahaifiya a faɗin duniya da ta ta6a yima ɗiyarta irin ta."
Kasa karasa maganar Murja tayi sakamakon kuka da yaci ƙarfin ta.

"Ke mahaifiyata ce kuma na ɗauki wannan abun a matsayin ƙaddara ta, na yafe maki Ubangiji ya yafe mana."
Cewar Lubna tana kuka.

Jikin Murja ne ya sake yin matuƙar sanyi, cike da zallar nadama ta kama mahaifinta dake ta hauka suka fice tana zubda ruwan hawaye.

Gaje Kuwa roƙon Lubna ta riƙayi hawaye na bin fuska.
"Nasan bani da bakin da zan roƙeki akan ki yafe mani domin na cutar dake mafi munin cutarwa, Ubangiji ne ya fara nuna mani sakayya keda na banzatar nike ma fatan lalacewa sai gashi nan ɗiya ta ce ta lalace,dan girman Allah ki yafe mani badan halina ba."

Lubna me matukar sanyi hali ce dan haka babu bata lokaci ta yafe masu.

Malam Sule shida iyalin su bankwana suka yi zasu fice, nan fa Lubna ta tubure sai ta bisu, da kyar malam Sule ya shawo kanta ta haƙura ba zata bisu ba.

Alhaji Jadda ma koda zai tafi baiyi yunƙurin tafiya da Lubna ba nan ya barta wurin Hajiya salima.

Hajiya Salima kuwa tamjar zata maida Lubna cikin ciki haka take ji, ƙaunar yarinyar na ƙara shigarta.

Duk yadda Al'ameen yaso su haɗu da Lubna amma abun yaci tura, sa'ar daya samu ita ce Lubna na shiga kitchen yayi saurin tare ƙofar kitchen ɗin.

Juyowa tayi cike da mamakin wannan sabon hali daya bullo dashi.

"Amincin Allah ya tabbata ga matar Sunnah."
Al'ameen ya faɗa yana me jingina da bango

Lubna kuwa mamaki me ya kasheta
"Ko ba matar Sunna ba? Shin wai kama manta da wadda kake tsaye gabanta ne, Baƙa mummuna me mafi sunin halintta wadda ka tsana mafi munin tsana, shin mi kazo yi wurin wannan Baƙar halitta kuma mummuna, kamar yadda ka gujeni lokacin da nike cikin mummunar halitta haka nima yanzu zani murtsuke wannan auren naka in je in aure kyakkyawan namiji Fari sol kuma santalele."
Lubna ta karasa maganar tana me Yin fari da ido.

Wani mahaukacin kishi ne ya lullu6e zuciyar Al'ameen ji yayi tamkar ana zuba mashi ruwan

darma a zuciya, a fusace ya haɗe Lubna da bango tare da shaƙe mata wuya.

"Ƙarya kike, a gaba na kike ambatar zaki murtsuke mani aure kije ki auri wani banza, ƙarya kike yi Lubna."

Ka karin wahala Lubna ta fara, Hajiya Salima kuwa a guje tayo kanyar kitchen ɗin ita da Uwar Garke da ta bayyana yanzu suna rige_rigen shigewa kitchen ɗin...

*MEEN@RT...✍🏻*
[9/5, 9:16 AM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE5️⃣4️⃣_5️⃣5️⃣*

....Fizga ɗaya Uwar Garke tayi ma Al'ameen ta fincike shi daga shaƙar da yayi ma Lubna.

Cike da zallar mamaki Hajiya Hajiya Salima ta fara magana.
"Al'ameen anya kana da hankali? Ɗiyar mutane zaka shaƙe ka haɗe da bango shin kisan kai kake so kayi? Mi ya haɗaku har haka."?
Hajiya Salima ta ƙarasa maganar cike da ɓacin rai.

Lubna dake hannun Uwar Garke numfashin wahala ta riƙa medawa.

Al'ameen kuwa har lokacin idanun shi jajur suke tamkar gauta, ga wani ɗaci da yaji yana taso
```

mashi ya haɗe ilahirin maƙoshin shi dan haka ya kasa furta koda kalma ɗaya ce.

"Za kayi mana bayani ko sai ranka yayi mummunan ɓaci."?
Hajiya Salima ta fada a fusace.

Lubna ya kalla da har yanzu bata ƙarasa dawowa cikin hayyacin ta ba sannan ya fara magana.
"Har ni yarinyar nan zata kalla tace zata murtsuke aure na taje ta auri wani, ina matsayin mijinta."
Ya ƙarasa maganar a fusace.

"Amma tabbas baka da hankali, to in ma Lubna tace haka ai dole ka aiwatar yarinyar da taci wuyarka dama can ba sonta kake ba sai yanzu zaka wani shaƙeta, to ka bude kunnen ka da kyau kaji in dai Lubna tace ta gama zama da kai dole ka sawwaƙe mata."
Hajiya Salima ta karasa maganar tare da wurga ma shi harara.

Uwar Garke ce ta karɓe zance.
"A wane daliline zaka shaƙe mani ɗiya kana neman rabata da duniya? Kai Al'aminu tsaya kaji har yanzu a Uwar Garke ta nike yanzu ma kawai kawaici nayi maka amma da jikin ka ya jima da gaya maka, haka kawai kasamu Lubna ka shaƙe, to kayi na ƙarshe  dan kaɗan daga cikin aikina ne in maka kamun kazar Kuku a wurin nan, Al'ameenu ka fita idona in rufe."
Uwar Garke ta ƙarasa maganar tare da ficewa da Lubna daga kitchen ɗin.

Take masu baya Al'ameen yayi a fusace yabar gidan, rarrashin Lubna suka hau yi domin cewa tayi gidan Malam sule zata koma da kyar suka shawo kanta ta amince zata zauna.

Jim kaɗan Sai ga Saro ta bayyana a gidan, a ranar sunyifarin cikin da basu taba yin irin shi ba domin saro tayi murna sosai da samun lafiyar Lubna tamkar ta zuba ruwa ƙasa tasha.

Ko kaɗan Lubna bata yi gigin sanar da Saratu abinda ya faru yau tsakaninta da Al'ameen ba, Sai ma saratun ce kece mata ita dole ne yanzu taja aji ta dan gasa Al'ameen ta yadda zai gane kuskuren shi na baya.

Murmushi Lubna tayi domin harga Allah tana matuƙar ƙaunar Al'ameen shiyasa ba zata iya bashiwata wahala ba sakamakon son da take mashi, kauda maganar Lubna tayi tare da yima Lubna batun Bilal.

"Baba ya amince ma Al'ameen yanzu haka an kawo kuɗin Aure na, nan da wata hudu, amma ji nike anya zani iya rayuwa da Bilal, yaro ne mara natsuwa sam kanshi rawa yake."
Saratu ta ƙarasa maganar.

"Saratu ke shaida ce, yadda rayuwar ta baya ta kasance da Al'ameen amma yanzu komi ya

canza, Saratu haƙuri zakiyi domin Bilal na matuƙar ƙaunar ki, zaki iya canza shi ta hanyar yi ma shi addu'a tare da kuma nuna ma shi hanyar gaskiya da kuma nusar dashi abinda bai da amfani, mai haƙuri shike dafa dutse."
Jikin Saro ne yayi sanyi nan taji tabbas zatayi iyakar ƙoƙarin ta wurin ta canza Bilal, yinin ranar haka suka yini suna fira Ta yaushe gamo, sai gaf da magriba saro ta tafi.

Bayan tafiyar ta ne Hajiya Salima ta iske Lubna har daki, ganin ta da tayi ne yasa Lubna matuƙar jin kunyar ta domin tasan sam bata kyauta ba abinda tayi ma Al'amin domin koba komi ya kamata ace yaci darajar mahaifiyar shi.

Zama Hajiya Salima tayi kusa da Lubna tare da fara magana a hankali.
"Lubna!"
Hajiya Salima ta kira sunan ta a hankali.

Lubna kuwa kanta a ƙasa ta amsa.

"Banji dadin abinda ya faru ɗazu ba, Lubna keda Al'ameen duk ɗaya na ɗauke ku, in kina da matsala ni mahaifiyar ku ce kada ki boye mani komi wallahi koda ace baki son Al'ameen saki kike buƙata nice wadda zani tilasta shi ya sake ki, Lubna ina maki soyayyace ta tsakani da Allah, shin kina buƙatar Al'ameen ya sawwaƙe maki."?
Hajiya Salima ta karasa maganar tare da kafe Lubna da ido.

Lubna kuwa gabanta ne yayi mummunar faɗuwa domin har ga Allah tana son mijin ta bata fatan rabuwa dashi, sake tambayar ta da Mahaifiyar Al'ameen tayi a karo na biyu ne yasa tayi saurin girgiza ka alamun tana son mijin ta.

Murmushi Hajiya Salima tayi tare da kamo hannun Lubna.
"Ke yarinyar kirkice wadda bata da butulci ko kadan, duk da kin samu lafiya amma baki guji ɗana ba, sabanin shi da ya nuna maki zallar kiyayya, Lubna nagode Ubangiji yayi ma rayuwar ki Albarka."

Jim kaɗan sai ga Alhaji Jadda yazo gida tare da buƙatar shi ta abashi Lubna domin dangin shi su ganta, babu musu Hajiya Salima ta shirya Lubna tare da haɗa mata kayanta tayo masu rakiya har bakin mota, mahaifin Al'ameen kuwa bai bar wurin ba sai da Jadda ya bar harabar gidan, cike da kewar Lubna Hajiya Salima ta koma falo ta zauna tayi jugum, wani murmushi ne ya subuce mata domin ta samu hanyar da zata hora Al'ameen ya gane cewa Lubna tana da gatanta.

Al'ameen kuwa duk da suna tare da Bilal amma hankalin shi na wurin Lubna burin shi ɗaya shine ya ganshi ya bayyana gida koda zai yi tozali da Lubna.

Kai tsaye ɗakin mahaifiyar shi ya tura gabanshi na dakan uku_uku, bayan ya gaidata har zai

nufi ɗakin Lubna yaji mahaifiyar tashi ta kira sunan shi, dawowa yayi tare da zaunawa kai a kasa yana susar ƙeya.

"Yanzu Al'ameen abinda kayi ka kyauta kenan? Yarinyar da tayi maka halaccin da ba ko wace mace bace zata iya irin shi ba, amma ace ita zaka shaƙe kana neman nakasa ta? To kayi dai_dai domin na lura baka son farin cikina a gidan nan sai bacin raina, nagode Al'ameen."
Ta karasa maganar tare da haɗe girar sama data ƙasa.

"Dan Allah ki yafe mani Mommy, wallahi banyi da nufin ranki ya baci ba, nayi ne sakamakon bacin rai da kuma kishi daya ziyarce ni, amma bazan kuma ba."
Al'ameen ya ƙarasa maganar tamkar zai yi kuka.

"Ni na haƙura, amma ka sani mahaifin Lubna yazo cikin daren nan ya ɗauki ɗiyar shi ya tafi da ita domin bazai taba bari ka nakasa mashi ɗiya ba, sai ka rubuta takardar ta ka aje mata."
Hajiya Salima ta karasa maganar cikin daga murya.

Wata mummunar faduwar gaba gami da firgici ne suka ziyarci Al'ameen, lokaci daya zufa ta riƙa keto mashi tamkar yana gaban wuta.
"Lubna rayuwata ce Mommy bazan iya rabuwa da ita ba, na roƙeki kada ki bari a rabani da Lubna, na tuba bazan sake aikata abu makamancin wannan ba."
Ya karasa maganar tare da kama ƙafar mommyn ta shi.

Hajiya Salima kuwa wata dariya ce ke neman kubce mata ganin yadda ɗan nata ya kamu da soyayya lokaci ɗaya.
"Dan Allah sakar mani kafa kada ka karya ni, babu abinda zance maka sai kaje ka dage da addu'a domin ran mahaifinta ya ɓaci matuƙa."

"Zani yi amma dan Allah ki tayani, kada a rabani da Lubna ta Mommy."
Al'ameen ya ƙarasa maganar kamar zai yi kuka.

"Zani taya ka Amma kaje ka kwanta kaga dare ne yanzu."

"Bani iya bacci Mommy yau kwana zanyi ina sallah ko Allah zaiji ƙai na yasa Lubna ta dawo gare ni."

Hajiya Salima kuwa cike da mamaki take kallo shi, yaron da rabon da taji yace zai yi sallar dare harta manta amma yau shine da faɗin zaiyi sallar na fila, lallai soyayya tana sauya mutum.

A ƴan kwanakin sam Al'ameen bai cikin natsuwar shi domin kallo ɗaya zaka yi mashi ka fuskanci yana cikin damuwa, Uwa da ɗa sai Allah, Hajiya Salima tausayin ɗan nata ne ya kama ta matuƙa.

Tun bayan tafiyar Alhaji Jadda ɗaya bayan ɗaya ya riƙa bin dangi yana nuna masu Lubna, su kuma takaicin Hajiya Murja ke sawa su rika Allah wadai da abinda ta aikata, babu wanda yakai mahaifan Alhaji Jadda farin cikin ganin Lubna da suka yi mahaifiyar Lubna kuwa tasha zagi gami da Allah wadai rantsuwa suka yi kan cewa babu ɗansu babu maido Murja koda mata sun ƙare a duniya.

Wannan magana tayima Lubna ciwo ba kaɗan ba domin mahaifi a duk inda yake mahaifine, ko alama bata so taga mahaifanta a ware basu tare amma babu yadda zatayi ƙaddara ta riga fata.

Sun ɗauki kimanin mako guda tana wurin dangin mahaifinta inda ake nuna mata zallar gatan da bata taba ganin irin shi ba, amman duk da wannan bai hanata tunanin Mijinta da kuma Malam sule.

A wani yammaci suka Alhaji Jadda yazo ya ɗauki Lubna da kuma kakannin ta suka nufi gidan Malam Sule domin su miƙa godiyar abun arziƙin da yayi ma jikanyar su.

Tunda suka karyo kwanar gidan Lubna ke kallo gidan nasu daya canza suffa ya koma wani haɗaɗɗen Flat house wanda kaf area wurin babu tamkar shi, ita ce farko buɗe kofa ta fito tare da shigewa gidan cike da zumuɗin ganin mahaifin nata, sallamar da tayi ce ta sanya Gaje dake ba Kulu ruwa a baki juyowa da sauri, shi kuma Malam Sule dake cikin tamfatsetsen falon jin muryar yar Lelenshi ya sanya shi fitowa da hanzari.

Faɗawa tayi jikin mahaifin nata cike da kewar shi da tayi, Malam sule kuwa wani farin ciki ne ya ziyarci zuciyarshi domin yayi kewar Lubna matuƙa.

Murna da farin ciki basu bar malam Sule ya lura da su Alhaji Jadda ba sai yanzu, a tare suka rankaya suka shige ɗakin, bayan sun gaggaisa ne Mahaifan Alhaji jadda suka riƙa kwararo godiya gami da addu'ar fatan alkhairi ga Malam sule domin sun shaida ba kowane mutum bane zai iya irin abinda yayi masu.

Shi kan shi Malam Sule godiya ya riƙa yi ta irin taimakon da Alhaji yayi mashi, ya gyara mashi gida ya bashi jari me matuƙar gwabi, tsakanin shi da mahaifan Lubna sai godiya, koda Alhaji Jadda zai tafi nan Lubna ta buƙaci da su barta tayi wasu ƴan kwanaki gidan Malam Sule, basu matsa mata ba nan suka barta tare da yima Malam Sule sha tara ta arziƙi.

Mutanen Unguwa kuwa tururuwa suka riƙa yi dan gane ma idon su shin da gaske ake Lubna ta warke, sunyi matuƙar yin mamaki cike da Kunyar abinda suka riƙa yi mata haka suka riƙa fitowa daga gidan, sai gashi wadda suka tsana suke kyara ita ce wadda tayi sanadin da aka gyara masu Unguwar su domin a halin yanzu babu mutum me wadatar Kamar Malam Sule Kaf unguwar, duk da halin da suka nuna mashi a baya hakan baisa ya guje su ba domin Malam Sule mutum ne me hannun kyauta ba shi da Rowa ko a lama.

Gaje kuwa dake jinyar Kulu kuka take cike da nadamar abinda ta aikatama Lubna domin tasan

indai Lubna bata yafe masu ba suna cikin tashin hankali.

Zaune suke cikin Falon Gaje na ba Kulu abinci a baki, juyowa tayi tare da kallon Lubna sai kuma wasu hawaye suka shiga wanke mata fuska.
"Tabbas Alhaki kuikuyo ne, Lubna basai na faɗa ba nasan na cuceki amma dan girman Allah ki yafe mani ashe rayuwa zata iya juya mani baya har haka, sai gashi abinda na shuka duk ya dawo kai na."
Gaje ta ƙarasa maganar hawaye nabin fuskarta.

Ita ma Lubnar kuka take domin tunda tazo taga Halin da Kulu ke ciki take zubda mata hawaye.

"Dan Allah mama ki dai na faɗar haka domin ni tuni na yafe maki nima Allah ya yafe mani."
Lubna ta ƙarasa maganar tare da kamo hannun Kulu.

Da kyar kulu ta tashi zaune da ƙaton cikin ta haihuwa ko yau ko gobe.
"Lubna nasan na cutar dake mafi munnin cuta, alhakin kine ke ɗawainiya dani, na roƙe ki dan Allah ki yafe mani nasan lokacin mutuwa ta ya gabato yafiyarki ita nike nema."
Kulu ta ƙarasa maganar tana hawaye.

"Na yafe maki , ki daina cewa zaki mutu, Kulu ba zaki mutu ba in shaa Allah zaki haihu ki gyara rayuwarki."
Lubna ta ƙarasa maganar cikin ƙarfafa mata guiwa.

Murmushin da ake kira yaƙe Kulu tayi domin ita kaɗai tasan azabar da take ji a jikinta, domin duk wani maganin cutar da ake sawo mata ba tare da sanin kowa ba ashe bata sha sai dai ta boye shiyasa cutar tayi mata mummunar illa a jiki.

Saro ma da yake kullum sai ta shigo duba jikin Kulu nan ta iske Lubna.

A wata safiyar laraba ne Kulu ta tashi da matsananciyar na ƙuda, Malam Sule mota ya ɗauko ya kwashe su sai asibiti, da yake sun san lalurar Kulu nan suka hau bata taimakon gaggawa amna ina jini ne ya fara yo gaba haihuwarta tazo da matsala, duk wani taimako da zasu bata amma ina abun ya fi ƙarfin su,dan haka dole suka shirya yi mata C.S cikin gaggawa, ganin Kulu ta buƙaci a kira mata mahaifanta tayi bankwana dasu yasa likitocin kiranta mahaifan Lubna, suka faɗa Emergency a gigice, kallo ɗaya suka yi mata Lubna ta hau kuka, Gaje kuwa nadama da tausayin tilon ɗiyar ta ne suka sata zubar da hawaye.

Da kyar Kulu ta buɗi baki ta fara magana kamar haka.
"Ba kuka zaku yi mani ba addu'ar ku nike nema, a halinda nike ciki yanzu babu abinda nike buƙata wurinku kamar addu'a, Baba ka yafe mani domin nasan na cutar dakai cutarwa me tarin yawa na saɓama umarninka, naja maka zagi wurin mutane, dan Allah ka yafe mani ko zan samu rangwame ."
Ta ƙarasa maganar a galabaice.

"Na yafe maki Hawwa'u Ubangiji ya tashi kafaɗunki kinji."
Malam Sule ya fada da karyayyar murya.

"Ba zaki mutu ba Kulu, ki daina kiran mutuwa dan Allah."
Lubna ta ƙarasa maganar tana kuka tare da kamo hannun kulu.

"Lubna ke mutuniyar kirkice kina da halacci, Ubangiji ya dawwamar da farin ciki a rayuwar Aurenki, Lubna sai wata rana..."
Tana kaiwa nan jikinta ya riƙa wata jijjiga lokaci ɗaya idanunta suka kalli sama.

Ihu Gaje ta kurma tare da zubewa ƙasa a sume, Lubna Kuwa a guje ta fice ta kira likitoci, ganin sun tattaba ko ina amma ina Kulu ta amsa kiran Allah, farin kyalle suka jawo tare da rufe mata jikinta dashi, suka fice daga ɗakin jiki a sanyaye.

"Innalillahi wa'inna ilaihirrajiun!"
Ita ce kalmar da suka ci gaba da mai_maitawa.

Cikin ƙanƙanin lokaci mutuwar Kulu ta karaɗe ko ina, Malam Sule da kanshi ya sanar da surukan Lubna da kuma Mahaifin ta Alhaji jadda.

Gida fa ya cika sai koke_koke akeyi tare da jimamim wannan al'amari, da misalin ƙarfe biyu aka kai Hawwa'u gidanta na gaskiya, Gaje kuwa ta koma tamkar zautatta babu magana sai dai hawayen dake bin fuskarta.

Hajiya Salima tare suka iso ita da Alhaji Sufyan, fadawa jikinta Lubna tayi tana me sakin wani kuka me tsuma zuciya.

"Hakuri zakiyi Lubna, lokacin ta ne yayi a halin yanzu babu abinda take buƙata sai addu'ar ku."
Nan ta shiga kwantar ma da Lubna da hankali.

Kira ne ya shigo wayar Alhaji Sufyan, mikewa yayi tare dayin nesa da jama'a sannan ya ɗauka, jikin shi me ya hau tsuma yana gama wayar a gaggauce ya kira Mahaifiyar Al'ameen kai tsaye asibiti suka wuce, duk tambayar da Hajiya Salima kema mahaifin Al'ameen amma bai bata amsa ba dan haka taja bakinta tayi shuru.

Emergency taga sun nufa tare da shigewa wani ɗaki, ganin wadda ke kwance saman gadon yasa Hajiya Salima karasawa wurinta cike da farin ciki ta furta "Yaya!"
Jin muryar Hajiya Salima yasa Hajiya Mariya ɗago kanta a firgice.

"Yaya ina kika shige, mun neme ki ruwa a jallo amma bamu ganki ba, kin tafi kin barmu cikin tashin hankali."

Kuka hajiya Mariya ta fashe dashi tare da kallon su.
"Nagode ma Allah daya sanya kafin in bar duniya na sake haɗuwa daku, yau zani warware maku ƙullin da ni na kullashi da hannu na amma komi zaku ji na roƙe ku yafe mani domin ina ji a jikina lokacin mutuwata ya kusanto ni, tun bayan kawo ki a matsayi Amaryar Alhaji nike ƙulle_ƙulle dan ganin na fitar dake daga cikin gidan amma Allah bai rubuta ba sai ma ya kasance duk abinda nayi sai ya dawo kai na, koda na haifi Fadila banso ace mace bace na haifa naso ace ɗa namiji ne na haiho, a kwana a tashi har kika haifi Al'ameen inda tsabar baƙin cikin da naji tamkar in haɗiye zuciya in mutu, nida ke cikin gidan na riga ki jimawa na haifi mace ke kuma daga zuwanki kin haifi ɗa namijj, nan fa na duƙufa bin malamai da bokaye ganin na kashe Al'ameen sai ya kasan ce duk wurin malamin da naje ceman yake basu iya kashe shi sai dai abi wata hanyar, na bada maƙudan kuɗaɗe ganin an lalata mani rayuwar Al'ameen in da kuma cikin ikon Allah sai ga al'amuran Al'ameen sun fara tabarbarewa amma duk da haka ni banso ba domin ba irin wannan lalacewar naso yayi ba, duk wani ƙulli da zanyi akan Al'amen a banza domin basu kama shi, in taƙaice maku magana har bayan auren Al'ameen ban daddara ba duk da bacewar ɗiyata da ta shiga duniya, anan nayi niyyar raba al'ameen da kowa nashi nayi magani dan ya shiga duniya, amma sai ga maganin ya koma kai na nice na shiga duniya, nasha wahala shigata duniya abinda zanci ma gagarata yake nayi bara na kwana a titi daga karshe na samu aikin gidan wani me kuɗi ina masi shara da wanke_wanke suna biyana tare da bani abinci, a wani dare da bazan taba mantawa ba, ina cikin bacci a ɗakin masu aiki muka jiyo ƙarar bindiga, a firgice muka farka muna niyyar guduwa amma ina tuni yan fashin sun fiddo mu tare da mai gidan da matanshi, maƙudan kuɗaɗe suka buƙaci a basu Alhajin na rawar jiki ya kwaso masu kuɗaɗe, nikau da jikina ke ciri a hankali na ɗago kai na karaf idona ya sauka ka Fadila da ta koma tamkar ƙato kannan anyi mashi askin yan fashi riga da wando ne jikinta hannunta ɗauke da bindiga ta auna ni da ita.

Cikin rawar la66a na fara magana
"Fadila kece kika zama haka? Innalillahi wa'inna ilahirrajiun, tabbas sharri ɗan aike ne yau gashi ya dawo kai na, kallo na Fadila tayi a fusace tare da tambayar miya kawoni gidan, Ogan sune daya lura an gane su shida kanshi yasa Fadila ta harbeni a ciki, daga nan bansan mike faruwa ba sai farkawa nayi naga an yi mani aiki tare da sanar dani in kwantar da hankalina domin aikin DA akayi mani me haɗari ne bolet ɗin ya shiga jikina ciwon ya harbi hantata abu ne me matuƙar wahala in rayu, sam a lokacin ba rayuwa ta bace me amfani domin hankalina yana wurin Fadila, koda na tambaye su ceman suka lokacin da Fadila ta harbe ni ƴan sanda sunyi nasarar kawo ma gidan ɗauki inda mafi akasarin ƴan fashin suka  gudu macen kaɗai akayi nasarar harbi loKacin taka ƙoƙarin guduwa."
Kukan da Hajiya Mariya keyi ne ya haddasa mata kasa ci gaba da magana.

Cike da tashin hankalin jin wannan labari Mahaifiyar Al'ameen ji tayi ƙafafunta sun kasa ɗaukar ta, kujerar dake gefen gadon ce ta yi sauri janyo wa tare da zama.

Alhaji Sufyan kuwa banda kallo tsana babu abinda yake aikama  Mariya dashi.

Shar6e majina tayi tare da cigaba da magana.
"Nayi kukan baƙin ciki tare da nadama wadda bantaba yiba domin nasan ƙaiƙayi ne ya koma kan masheƙiya, abinda na aikata ne ya dawo kaina, sai gashi nida naso Al'ameen ya zama ajalinki sai ya kasance ɗiya ta ce ta zamo ajalina, ganin halinda nike ciki yasa na bada address ɗin ka domin in nemi yafiyarku koda zani samu sassauci a wurin Ubangiji, nasan na cutar daku amma dan girman Allah ku yafe mani."
Ta karasa maganar tare da dafe cikin ta da taji tamkar ana yankar hanjinta.

"Mariya kin cutar damu, kin sanyani cikin tashin hankali na gur6acewar tarbiyyar yarona, sai ga shi tun duniya Ubangiji ya fara nuna maki iyakarki,shin miye aibun ɗiya mace dan ka haifeta kace kai dole sai namiji, dukkansu Allah ne ke badawa Fatanmu shine a bamu na gari amma kika manta da wannan kike ƙoƙarin kashe mani yaro, amma babu komi na yafe maki Ubangiji ya yafe mani nima."
Mahaifiyar Al'ameen ta karasa maganar tare da goge guntun hawayen ta.

Mahaifin Al'ameen ne ya kalli Hajiya Salima rai a matuƙar bace.
"Kece har zaki buɗe baki kice kin yafe ma wannan maciyiyar amanar? Matar da ta cutar damu ta tarwatsa mana farin ciki sannantayi sanadin mutuwar ɗiya ta, Mariya na tsaneki ban yafe maki ba, Na sakeki! Na sakeki!! Na sakeki!!"
Mahaifin Al'ameen ya karasa maganar a fusace tare da ficewa daga ɗakin.

Ihu Mariya ta riƙa kurmawa sai kuma ta fashe da dariya.
"Ƙarya kake ban saku ba, kai yama za'ayi ka sakeni, nida keda bokaye da malamai, niface nasa Al'ameen ya lalace."
Sai kuma ta fashe da dariya, tare da ci gaba da tona mata kanta asiri, duk wani abu data aikata nan ta rika fallasa kanta tana wurgida duk wani abu dake saman gadon, ganin yadda ciwon hauka ya sameta dole aka ɗaure ta Alhaji Sufyan ya sanar da danginta kaf abinda ya faru, nan suka shiga tashin hankali tare da nufar asibitin, sai da Murja ta share wata ɗaya tana hauka daga nan kuma tayi mutuwar wulaƙanci.

Gaje kuwa nadama ce ta risketa a lokacin da bata da amfani domin tasan yanzu Malam Sule haushin ta yake ji ga kuma ɗiyarta data rasa saboda son zuciya irin nata, rayuwa kenan yau ga ɗiyar da ta wulaƙantar ita ce ta tallafi rayuwar su ita ce gatan su.

Malam Sule kuwa bazai iya sakin Gaje ba domin inya sake ta wurin wa zata je, amma alƙawari ne ya ɗauka dole ya ƙara aure.

Wayewar garin yau Malam Sule da Gaje sun shiga matsanancin ruɗani da tashin hankali domin kuwa sun nemi Lubna sama ko ƙasa sun rasa, bai kira ya sanar da bacewar Lubna ba sai da yaga abun na neman fin ƙarfin shi domin har azahar tayi babu lamarin Lubna, Mahaifan Al'ameen ya kira domin jin ko Al'ameen ne yazo ya dauke ta, amma sai ce mashi suka yi bata zo ba, nan fa hankali ya tashi, bangarorin biyu suka shiga neman Lubna amma basu sanar da

Alhaji Jadda halinda ake ciki ba.

Koda Al'ameen yaji batan Lubna jiki ya yanke ya faɗi jini ya fara zuba ta hanci da baki, a gigice suka kwashe shi aka nufi asibiti domin a yadda suka ga jikin shi ya saki abu ne me matuƙar wahala Al'ameen ya rayu, tashin hankali biyu ya haɗema Hajiya Salima kuka tare tana mai_maita innalillahi wa'inna ilaihirraji'un Allahumna ajirni fiymusibati wa'akhlifini khairan minha, tana yi hawaye na kwarara a fuskarta.

*A YI MAN UZURI NA JINA KWANA BIYU DA AKAYI SHURU, ASKI NE YAZO GABAN GOSHI 🚶‍♀️🚶‍♀️*

*MEEN@RT...✍🏻*
08133562798
[9/7, 6:39 PM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE5️⃣6️⃣_5️⃣7️⃣*

🥺💔 Ku tanadi ɗan gajeren tsumman ku na goge hawaye da majina.

...Al'ameen dai tun bayan kai shi asibiti da akayi har yanzu baisan inda kanshi yake ba, ga Lubna ita ma har yanzu shuru bata bayyana ba.
```

A bayanin da likitoci suka ma mahaifan Al'ameen sun sanar dasu cewa zuciyar shi ce ta fara kumburi sakamakon wani abu da yake so amma bai samuba damuwar da yake ciki ita ta ƙara haddasa mashi ciwon, jin wannan bayani ya ƙara tayar da hankalin Mahaifan Al'ameen musamman Hajiya Salima.

Bangaren Malam Sule kuwa rokon Allah yasa aketa ti har Allah ya bayyana Lubna, Gaje kuwa duniya ta koya mata Hankali domin kuka ta rika yi Allah ya bayyana mata Lubnar ta.

A yau ne suka shirya Sanar da Alhaji Jadda halinda ake ciki madamar basu ga Lubna ba, Malam Sule da Gaje ne suka ziyarci asibitin da yammacin marece, bayan gama jajanta ma juna ne suke tambayar jikin Al'ameen.

"To! Da sauƙi za'a ce domin har yau bai farka ba."?
Hajiya Salima ta faɗa murya na rawa.

"Ubangiji ya bayyana mana Lubna, shi kuma Allah ya tashi kafaɗun shi."
Gaje ta faɗa.

A hankali suka ji ƙarar turo ƙofar ɗakin tare da shigowa da Sauri, hankalin sune ya koma ga mai ƙoƙarin shigowa ɗakin, a tare suka miƙe tare da furta "Lubna!"

Lubna da jikinta ya ƙara kyau sai sheƙi take yi, ta yi ƴar ƙiba kallo ɗaya zakai mata ka fahimci irin ni'imtaccen kyawun data ƙara, cikin Hanzari Lubna ta ƙarasa jikin gadon Al'ameen tamkar zatayi kuka.

"Lubna ina kika je, kin barmu cikin tashin hankali ga Kuma Al'ameen dake cikin wani mawuyacin hali sakamakon ɓatanki."
Mahaifiyar Al'ameen ta ƙarasa maganar tare da kamo lallausan hannun Lubna.

Malam Sule kuwa da kyar ya iya furta.
"Lubna Allah yasa ba wani mugun abu bane ya faru dake, ɓatanki ya tayar mana da hankali."

"Ku gafarceni ni ce nan na ɗauki Lubna, ba da nufin in bata maku ba."
Jin me maganar Juyawa suka yi da kallon Uwar Garke dake ƙoƙarin shigowa ɗakin.

"Na ɗauki Lubna ne domin ayi mata yan dabaru irin namu na jinnu wanda ba zasu cutar da jikinta ba wurin gyarata domin ita amarya ce, yau nayi alkawarin maido ta domin an gama gyarata, fatan zaku yi mani Uzuri."
Uwar Garke ta ƙarasa maganar tare da zama kusa da su.

Gaje da har yau tsoron Uwar Garke bai barta ba firgice da tashi daga kusa da Uwar Garke ta koma bayan Malam Sule.

"To Alhamdulillah, Muna miƙa godiyarmu ga Ubangiji daya bayyanar mana da Lubna, Allah ya tsare gaba."
Mahaifin Al'ameen ya faɗa.

A tare suka amsa da Ameen.

Lubna kuwa tun da tazo tana tsaye wajen gadon Al'ameen tayi mashi rumfa hawaye sun cika mata ido, a hankali hawayen yayi nasarar kubcewa daga cikin idonta tare da Gangarowa ya biyo ta saman lausasan kumatun ta ya dira saman fuskar Al'ameen, a hankali ya fara ƙoƙarin buɗe runannun idanun shi da suka jima a rufe, sauke su yayi kan Lubna dake tsaye gab da shi, cikin hanzari yayi saurin mikewa zaune.
"Da gaske kece?, da gaske matata ce nike gani ba mafarki bane nike."
Ya ƙara sa maganar yana me kafe Lubna da ido.

"Ni ce ba mafarki ba kake, na dawo gareka bazan ƙara tafiya inyi nisa da kai ba."
Lubna ta fada tare da share hawayen fuskarta.

Su Hajiya Salima dake cikin ɗakin sunyi matuƙar tausaya ma Yaran nasu dan haka Alƙawari suka yi na meda Lubna gidan ta da Al'amen ya ƙarasa warkewa.

Bayan komawar su Lubna gida sai ga Alhaji Jadda yazo ɗaukar ta, godiya Malam Sule yayi ma Allah da Alhaji Jadda ya iske Lubna da ya zasu ce mashi.

Ganin Yadda jikin Al'ameen yayi sauƙi yasa aka rubuta masu sallama a cikin satin.

Dangin Alhaji Jadda da kansu suka shirya Lubna tare da maidata gudan mijin ta, Al'ameen kuwa gani yaje tamkar an sauya mashi Lubnar shi ne sakamakon irin kyau da ta ƙara, so da ƙaunar juna kuwa a wurin su Al'ameen abun yanzu ba'a magana, Al'ameen ji yake sam bazai iya rayuwa babu Lubna ba domin sai yanzu yake gane a baya yayi sakarci.

Ta fannin Lubna ma hake domin ta fahimci irin ƙaunar da Al'ameen ke nuna mata.

Ɓangaren Hajiya Murja kuwa tun bayan barin gidan su Al'ameen har yau Alhaji Mamman hauka yake yana ji ma kanshi ciwo, wani lokacin ma sai an ɗaure shi, kullum Murja cikin tashin hankali take da nadamar Abinda suka aikata, kallo ɗaya zaka yima Alhaji Mamman kaji tamkar ka zubda mashi hawaye ya rame ya lalace ya fita hayyacin shi kullum ciwo sai ƙara gaba yake, domin yau kimamin watan ni huɗu kenan ana abu ɗaya.

Safiyar yau Murja ta shiga tashin hankalin da bata taba shigar irin shi ba domin kuwa wayar gari suka yi suka iske Gawar Alhaji Mamman ƙasan bene ya faɗo wurin hauka da yake ya kashe kanshi, kuka Murja take tamkar ranta zai fita tare da yima mahaifin nata fatan samun rahamar Ubangiji.

Labarin Mutuwar Alhaji Mamman tsohon shugaban ƙasa tuni ta karaɗe ilahirin garin.

Lubna da Al'ameen tuni suka ƙarasa gidan rasuwar inda mahaifansu suka take masu baya, Gaje da Malam Sule suma dasu aka yi jana'izar Inda Alhaji Jadda da dangin shi suka ce babu wanda zai je saboda baƙin halinsune yasa suka fara ganin sakamako tun nan gidan duniya.

Murja kuwa ta fita Hayyacin ta domin Mutuwar Mahaifin nata ta matuƙar tayar da hankalin ta, tayi nadama wadda bata taba yin irin ta ba, Al'ameen kuwa da kyar ya amince yabar lubna ta kwana domin ita ma bajin daɗi take ba laulayi take.

Sai da akayi sadakar Ukku Al'ameen yaje ya ɗauki Lubna, Murja kuwa ji tayi kamar kada ɗiyar tata ta tafi ta barta domin har ga Allah tanajin soyayyar Lubna a ranta kamar mi.

Dangin Hajiya Murja kuwa tun kafin mutuwar Murja ta basu kaf labarin abinda ya faru shiyasa yanzu da suka ga Lubna basu yi mamaki ba.

Tunda akayi sadakar bakwai gida ya koma daga Murja sai Dangin ta domin ba zasu tafi su barta ba har sai ta gama takaba.

Bikin Saro ya matso Lubna ba lafiya domin kuwa ƙarfin hali ne kawai take duk da cikin bai wuce watanni huɗu ba amma wahala yake bata ba kaɗan ba.

Saro kuwa hidima suke ta rabon invitation ga Al'ameen ya hana Lubna zuwa rabon, ko ranar Kamu da kyar ya barta suka je shima cikin mota ya riƙe ta domin cewa yayi babu wanda zai gane mashi mata da irin wannan kyan da tayi, Saro kuwa ta cika tayi dam domin ranta ya baci ganin babu Lubna a cikin taron, ta fannin Bilal shima hakane domin babban aminin shi guda amma ace babu shi bayan tare suka iso wurin.

Sai ana gaf da gama Kamu sannan Al'ameen ya yadda suka fito sakamakon roƙo da magiya da Lubna keyi mashi.

Shigowar su Hal ɗi nan fa idanun jama'a suka dawo kan su musamman Lubna da tayi wani masifaffen kyau domin rigar jikinta irin ta Amare ce wadda ke jikin Saro Al'ameen kuwa kayan jikin shi sak irin na Jikin Bilal ne, tunda suka shigo saro ke aikoma da Lubna da harara.

Murmushi Lubna tayi domin harga Allah tasan ba'a kyauta ma Saro ba amma laifin Al'ameen ne.

Ɗago kan da Lubna zata yi suka haɗa ido da Al'ameen dake aiko mata da saƙon harara, ita kam abun ma dariya ya bata ayi mata laifi sannan kuma a riƙa binta da harara.

"Kinji daɗi yanzu ko, tunda gaki mun fito maza sai binki suke da kallo, in kika sake sai na hanaki fita ko ina."
Ya karasa maganar cikin haɗe fuska.

"Ayi mani laifi kuma a rufe ni da fada ranka shi daɗe."
Ta karasa maganar tare da kumtse dariyar dake ƙoƙarin kubce mata.

A na gama Kamun Lubna tasha mita wurin Saro ba kaɗan ba, da kyar ta samu ta haƙura.

A bakin Motar Al'ameen wasu ƴan mata suka je suka yi tsattsaye sai wannan yau ƙi suke, tunda Lubna ta hango su taji wani abu ya tokare mata zuciya.

Ganib Bilal ya sa Saro mota yasa su Al'ameen suma suka nufi motar su.

"Oga dan Allah tafiya ne ka sauke mu a hanya."
Wata me Suffar Muciya daga cikin matan ta faɗa.

Lubna kuwa tsabar baƙin ciki ji tayi kamar ta shaƙe Yarinyar.

Al'ameen kuwa motocin dake wurin birjik ya kalla babu kowa ciki duk domin ɗaukar mutane gasu nan da yawa, amma waɗan nan matab masu Kama da Muciya suce motar shi zasu shiga.

"A'a wannan motar domin in ɗauki mata ta nazo da ita ga motoci can na ɗaukar ku,kuje ku shige."
Ya karasa maganar tare da buɗe ma Lubna murfin motar.

Ƴan matan kuwa tamkar su shaƙe Lubna haka suka ji.

Rana bata ƙarya sai dai uwar ɗiya taji kunya, a yau ne aka ɗaura auren SARATU tare da ANGON ta BILAL.

Yau Lubna tun safe tana gidan Malam Sule, domin kusan nan Saro tayi zama a lokacin hidimar ta, hatta kayan ɗaki duk Malam Sule ne yayi ma Saro.

Da yamma motocin ɗaukar amarya suka bayyana, Al'ameen kuwa bai bar Lubna ta sarara ba domin Motar shi ya sanya ta suka nufi gidan Amarya.

Masha Allah gidan Amarya ya ƙayatu matuƙa domin zai kai gidan Lubna kyau da haɗuwa.

Ranar walima kam Lubna da Saro sun sha kuka yadda kasan za'a raba su na har abada, duk da unguwar su ɗaya babu wani nisa tsakanin su.

Rayuwa ta kowane bangare tayi matuƙar dadɗi domin Bilal ya canza hali ya dawo mutumin kirki duk wani shirme ya aje shi gefe.

Cikin Lubna kuwa ya shiga wata na tara dan haka ko tafiya bata iya yi komi sai dai ayi mata, babu yadda mahaifiyar Al'ameen bata yi dashi ba akan ya dawo da ita gida amma ya ƙiya.

Babu abinda ke ƙara tayar da hankalin Al'ameen kamar wata magana da Lubna ke fada mashi tunda watan haihuwarta ya tsaya.
"In na mutu ka yafe mani, ina ji a jikina ba zani rayu da abinda zan haifa ba dan Allah ka auri mace ta gari wadda zata kula mani da kai da kuma abinda zan haifa."
Tamkar yayi hauka yake ji idan yaga Lubna na irin wannan maganar.

A safiyar yau ne Lubna ta tashi da matsananciyar naƙuda, Hajiya Salima da Al'ameen su suka kai Lubna asibiti amma har azahar abu ɗaya take bata haihuba duk ta fita hayyacin ta.

Hannu Al'ameen ya sanya domin kuwa C.S suka ce za'ayi mata, Gaje da Malam Sule ne suka bayyana a asibitin hankali a matuƙar tashe.

Ana gama sanya mata kaya za'a wuce da ita ɗakin da za'ayi mata aikin  ta buƙaci a kira mata Al'ameen.

Tsugune yake gabanta ya riƙo hannunta, da ƙyar ta buɗe baki ta fara magana.
"Yau i ta ce rana ta ta ƙarshe da zanyi da kai, mijina na roƙe ka da in na koma ma mahaliccina ka reni abinda na bari kada ka nuna mashi soyayyar da zata sanya ya lalace, Ina sonka ina ƙaunar ka, ka yafe mani kace kowa ya yafe mani, sai wata rana."
Likitocin ne suka yi gaba da Lubna domin ba zasu bari ta ƙara jimawa da wannan cikin ba.

Kowa ka kalla wurin fuskarshi na cikin matsananciyar damuwa.

Ana gab da yima Lubna aiki ta haifo yaranta kyawawa mace da namiji.

Gyarasu akayi tare da lullubesu aka fito dasu tare da nufo su Al'amern.

Murna wurin mahaifanshi abun ba'a cewa komi, sam Al'ameen hankalin shi na ga matar shi dan haka shi ya fara tambayar halin da ake ciki.

Jim! Likitan yayi kafin wata zuciyar ta bashi shawarar ya fadɗi gaskiya.

"Ubangijin daya baku ita ya fiku buƙatar ta, bayan ta haifi yaran nan Allah ya amshi abarshi."
Kafin likitan ya rufe baki tuni Al'ameem ya shaƙe likitan.

"Ƙarya kake, Mata ta bata mutu ba."
Ganin zai jima likitan rauni yasa su Malam sule banbareshi cike da tashin hankali.

A guje Al'ameen ya afka ɗakin cike da tashin hankali, wani wawan birki ya ja sakamakon gawar Lubna daya hanga lullune da farin kyalle saman gado kwance.

A igigice ya nuna ta da hannu tare da furta.
"Lu,,,b,,naaa!"
Ya yanke jiki ya faɗi.

Gigicewa su Hajiya Salima suka yi domin malam sule kallo ɗaya yayi ma Al'ameen ya fahimci da kyar in yana raye.

Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, Kullu nafsin za'ikatul ma'ut! 💔😭

*MEEN@RT...✍🏻*
[9/8, 8:37 AM] Meenat A Yandoma: 👽 *RUWA BIYU!!* 👽
_Free book_

Labari/Rubutawa
Meenat A yandoma

```MANAZARTA WRITERS ASSOCATION``` 📚🖊️
*M.W.A*

*Kungiya d'aya tamkar da dubu, Masu Nazari da aiki da ilimi, burin 'kungiyar a ko yaushe shine ta fad'akar ta Kuma Nishad'antar da Masoyan ta.*🥰
https://www.facebook.com/107980080946102?referrer=whatsa

---

*PAGE5️⃣8️⃣_5️⃣9️⃣_6️⃣0️⃣*

*FINAL* 🤗💃
```

...Ganin yadda Al'ameen ya kafe tamkar Gawa sun kasa ɗaga shi yasa suka kira likitoci, taimakon gaggawa suka fara bashi domin yana cikin wani hali da za'ace sai dai addu'a.

Duk taurin zuciya irin na Maza amma Sai da mahaifin Al'ameen yaji wasu siraran hawaye sunyi nasarar kubce ma shi, ita kam Gaje komawa tayi tamkar butum-butumi, kukan ma ta kasa sai dai Innalillhi wa'inna ilaihirrajiun da take maimaitawa, ga jaririn Lubna dake ta faman shan hannu alamun yunwa yake ji.

Hajiya Salima kuwa wata irin dauriya ce Ubangiji ya sauko mata da ita domin kukan ma sam ta kasa sai dai ajiyar zuciya da take saukewa, Jaririyar dake hannun ta ce ta fashe da kuka tamkar an tsunkuleta, nan fa hankalin kowa ya ƙara tashi fiye da ɗazu, duk yadda Hajiya Salima ke ƙoƙarin rarrashin jaririyar Amma abun yaci tura, domin wani irin Kuka ne take tamkar ranta zai fita, sautin kukan da take ne ya fara yima Al'ameen amsa kuwwa cikin kai, a gigice ya miƙe tare da fizge drip ɗin da aka ɗaura ma shi yana ƙoƙarin dirowa daga saman gadon.

Duk yadda Likitocin suke ƙoƙarin hana mashi fita amma abun yaci tura domin bankaɗe su yayi tare da fitowa daga ɗakin.

Tamkar an wullo shi haka ya afka cikin ɗakin da Gawar Lubna take, ga ɗiyarshi nata tsala kuka an rasa ya za'ayi da ita.

Tamkar me hankali haka ya amshi jinjirar daga hannun Mahaifiyarshi tare da ƙarasawa gaban gawar Lubna, hannu yasa ya janye farin yadin da aka rufeta dashi, nan fuskarta ta bayyana tamkar ka kirata ta amsa.

"Kinyi mani alƙawari zaki rayu tare dani komi rintsi komai wuya, mi yasa zaki tafi ki barmu nida yaranki a lokacin da muje matuƙar buƙatar ki, ki tashi ki rayu damu in kika barmu waye zai kula da yaranki, kinji yadda ɗiyarki ke kuka tana buƙatar ki shayar da ita, kuka fa take, ki tashi ki amsheta, kitashi naceeee."
Ya karasa maganar tamkar zautacce.

Abinda suka ga Al'ameen nayi shine sanya su zubar da hawaye, matsawa kusa dashi Hajiya Salima tayi tare da amsar babyn.

"Bacci take sai ta tashi kaji, yanzu gida zamu je kada ka tayar da ita hutawa take."
Ta karasa maganar tare da ƙoƙarin kauda hawayen dake son kubce mata.

Murmishi Al'ameen yayi domin kuwa har a jikin shi ya yarda matar shi bata mutuba.

Motoci suka ɗauki gawar Lubna da kuma su Hajiya Salima aka wuce da ita gidan su.

Alhaji Jadda kuwa shida dangin shi tuni suka bayyana gidan su Al'ameen cike da tashin hankali marar misaltuwa.

Allah sarki Saro tunda labarin mutuwar aminiyar ta ya risketa har zuwa yanzu hawaye bai yanke ba a fuskarta.

Hajiya Murja kam tana yin ido biyu da gawar Lubna ta yanke jiki ta faɗi, nan aka nufi ɗaki da ita cike da tausaya mata, gida fa ya cika babu masaka tsinke.

Kamar yadda addini ya tanada anso Al'ameen yayima matarshi wanka amma sun san a halin da yake ciki bazai iya wanke ta ba, Hajiya Salima ita ta wanke Lubna da kanta ta shirya ta tare da kiran makusantan ta da suyi bankwana da ita domin gaf ake da sadata da gidan ta na gaskiya.

Kowa yayi bankwana da ita banda Al'ameen dake can ɗakin shi rike da jariran da Lubna ta haifa yana jira ta farka ta anshe su, kiranshi akayi domin sanar dashi gaskiya domin ya yima Matar shi addu'a.

Sororo yayi tsaye gaban gawar Lubna domin bai fahimci abinda suke nufi ba da zasu sanya ma shi Lubnar shi cikin likafani.

"Al'ameen! Kai musulmi ne dan haka yarda da ƙaddara mai kyau ko akasin ta ya zama wajibi a gareka, Lubna ta rigamu gidan gaskiya Ubangijin da ya bamu ita ya amshi abun shi sai dai mu bita da addu'a domin yanzu ita take buƙata, kayi haƙuri ka nuna mazan taka kayi ma matarka addu'a a sada tada gidan ta na gaskiya."
Malam Sule ya ƙarasa maganar cike da juriya.

Al'ameen kuwa matsowa yayi gaf da fuskar Lubna dake buɗe.
"Mi yasa baku yarda dani ba, mata ta bata mutuba ku dubi fuskata ku gani murmushi take mani nace maku bata mutu ba."

Tabbas sun yarda Al'ameen ya haukace domin abinda yake sam mai hankali bazai yishi ba.

Duk juyin duniya anyi amma ya hana a ɗauki gawar Lubna kwatsam kuma sai ga Uwar garke ta bayyana fuskar nan a turɓune babu annuri sam.

Uwar Garke ita ce wadda ta goyama Al'ameen baya cewa Lubna bata mutuba, tun abu yana ƙarami sai ga abu ya girmama mutane sun fara sanin halinda ake ciki, wata mara kunya ƴar uwar Alhaji Jadda ce tasha gaban Uwar Garke.
"Miye alaƙarki da ita da kikazo kika hana a kaita gidanta na gaskiya, nidai nasan kaf cikin dangin mu babuke dan haka bamu son kalar dangi maza ki matsa ma mutane a hanya."
Ta karasa maganar tana jijjiga.

Hannu Uwar Garke tasa taye da kamo Saude ta buga da bango nan Saude ta hau kururuwa.

Wannan al'amari fa ya fara isar dangin Lubna domin mutane na can waje suna jira a fito da gawa amma ace sun hana.

Tun Gawa na cikin Ɗaki sai ga Gawa an fito da ita waje amma Al'ameen da Uwar Garke sun hana a tafi da gawa, suna can suna faɗa sai gani suka yi ƙafar Lubna ta fara motsi, wata mata da ta lura da wannan al'amari a guje tabar gidan tana kowa yayi ta kanshi gawa ta miƙe.

Lubna kuwa farkawar da zata yi ji tayi jikinta ko ina a ɗaure fuskarta ce kaɗai a buɗe, ganin Gawa zaune cikin makara yasa matan ficewa a guje suna bi ta saman mazan dake zaune suna jira a fito da gawa, wasu ma cin shinkafa ya kawo su domin labari ya samesu anyi mutuwa gidan Alhaji Sufyan Garkuwan Talaka.

Suma mazan haka suka riƙa ɗibar hanya a gigice domin abun ya girmama.

Al'ameen kuwa a guje ya karasa wurin matar shi, su hajiya kam sun sha mamaki domin a tunanin su Lubna ta mutu.

Ɗaukar ta ayi tare da shiga ɗaki da ita aka canza mata tufafi tare da miƙa mata jariran ta, banda hawaye babu abinda ke fita a fuskarta, Saro kuwa ji take kaf wurin babu wanda ya kai ta farin ciki.

Nan fa labari ya sake bazuwa cewa Lubna doguwar Suma tayi, dan haka masu zuwa dan suci abinci tuni haushi ya kule su.

Wahalar da Lubna tasha ita ce ta haddasa mata doguwar Suma in banda tana da sauran shan ruwa gaba da yanzu an binneta.

Ba'ayi suna ba sai da Lubna tayi mako biyu da haihuwa ta warware sannan aka shirya ƙayataccen bikin suna wanda ya amsa sunan shi inda namijin yaci Sunan Malam sule wato Sulaiman suna kiranshi (Ayman) macen kuwa sunan mahaifyar Al'ameen aka sa mata SALIMA suna kiranta (Aymana).

Ranar Suna anci ansha anyi sadaka domin nuna godiya ga Allah, Saro kam sune girjin biki domin ranar kaya iri ɗaya suka sa da Lubna.

Malam Sule kuwa har hawajen farin ciki yayi jin yadda Lubna ta ɗauke shi a matsayi mahaifi harta sama yaronta sunan shi.

Duk yadda Al'ameen yaso a bashi Matar shi su koma gida amma Hajiya Salima ta hana domin ta sanar dashi sai Lubna tayi watanni biyu ta murmuje jariran ta sunyi wayau.

Badan ya so ba sai dan baida yadda zai yi haka ya hakura, Leemcy kuwa duniya ta koya mata hankali yanzu ta shiryu mijin aure take nema ido rufe, sai ya kasance duk wanda zai zo ta buƙatar shi ce ta kawoshi, ana cikin haka wani abokin mahaifinta mai mata ukku ya fito, babu jimawa aka sha shagalin biki tare da miƙata gidan mijinta inda matan shi suke domin gida ɗaya aka aje su.

Zama kam babu daɗi sai dai haƙuri domin ƴa'ƴan shi zabga_zabga suk sa'annin ta ne, koda su kaɗai aka barta sun ishe ta gefe ɗaya kuna ga iyayen su, saukin Leemcy ɗaya mijin su na ƙaunarta san haka ne kaɗai yasa take haƙuri da zaman gidan.

Murja Kuwa bayan gama ta kaba raban gado akayi aka bata nata ta koma wurin danginta, nan ta samu ta auri wani direba me mata ɗaya, shima kwaɗayi ne ya kawo shi domin yaji labarin akwai kuɗaɗe hannun ta babu jimawa akayi auren ta tare gidan mijinta.

Kamar yadda Malam Sule yayi alƙawarin ƙara aure haka aka yi domin wata bazawara ya samu da mijinta ya rasu ita ya aure, Gaje kam tayi kukan fili dana ɓoye domin tasan wannan duk laifinta ne domin tasan halin mijinta yana sonta halin tane kawai yasa ya karo auren amma duk da haka yana masu adalci.

Mahaifin Lubna Alhaji Jadda shima dangin shi sun taso shi gaba akan dole ya ƙara aure, shiko har ga Allah yanzu tsoron mata yake domin abinda Murja tayi mashi har yau bai goge a zuciyar shi ba.

Da kyar aka samu ya auri wata jawara dake cikin family ɗin shi ita ma dan dai an yaba da halayen ta.

Ta kowane bangare rayuwa tayi daɗi zama ake na farin ciki da jin daɗi, Saro ma ta haihu ɗan na miji yaci Sunan mahaifin Lubna Sulaiman domin har abada bazata manta da halarcin shi a garesu ba.

Ayman da Aymana sunyi wayau domin kusan ko yaushe suna gidan su Al'ameen ƙarfi da yaji Hajiya Salima ta amshe su, Musamman Ayman shi yafi kaunar zama kusa da kakarshi sabanin Aymana da sai yanzu ta daina kuka in an kawo ta.

Aymana babu wanda ta saba dashi take sakarma fuska kamar Uwar garke sabanin Ayman da tsoron ta yake ba kaɗan ba, Aymana kuwa ta saba da ita har yazo suke zuwa shiyasa sam yariyar bata da tsoro ko alama.

Alhaji Sufyan shiya biya ma Al'ameen da Lubna aikin kujerar Hajj ya hada hada bilal da matar

shi, a tare suka keta hazo domin sauke farali.

Uwar Garke ma ba'a barta a baya ba domin ita da fuka_fukanta ta bisu.

*ALHAMDULILLAH ANAN NA KAWO ƘARSHEN WANNAN LITTAFI NAWA MAI SUNA RUWA BIYU, KURA_KURAN DA NAYINA CIKI UBANGIJI YA GAFARTA MANI, YASA AYI AIKI DA ABUBAWA MASU AMFANI MU HAƊE A LITTAFINA NA GABA ME SUNA ƘULLALLIYA! DAGA JIN SUNAN BA'A CEWA KOMI KU DAI KU BIYONI DA 300 ZAKU SAMU WANNAN LITTAFI.*

*TSAKURE DAGA LITTAFIN ƘULLALLIYA!*

"Aisha mi yasa baki son zuwa asibiti? da galihunki da komi Aisha amma kin zauna gida sai ciwo ya kashe mani ke, ni Yalwa tunda nike ban taɓa ganin inda ciki yayi shekaru biyu ba tare da an haife shi ba ko a zamanin mu daya shuɗe duk daɗewar ciki bai taɓa haura shekara ɗaya ba tare da an haife shi ba, amma ke cikin yau kimanin shekarun shi biyu kenan ba tare da kin haife shi ba, wannan al'amari da ganin shi nasan akwai wata ƘULLALLIYA."
Inna Yalwa ta ƙarasa maganar tare da duban Aisha.

Wadda aka kira da Aisha ce ta ɗago da jajayen idanun ta da kallo ɗaya zakai masu ka fahimci bata samun bacci ko misƙala zarratun.

"inna Yalwa na roƙe ki da ki dena maganar asibitin nan, a duk lokacin da zaki furta asibiti ji nike tamkar ana yankar naman jikina, raɗaɗi gami da azaba suke addabar jikina."

Sarƙewa maganar Aisha tayi lokaci ɗaya ta ƙanƙame jikin inna Yalwa tana kurma ihu.

"Gasu nan_gasu nan kin kira sunan asibiti kin ja mani, zasu kasheni , lokaci ɗaya numfashin ta ya tsaya idanunta suka kakkafe tamkar gawa....

*ƘULLALLIYA!*

Na kuɗi ne akan farashin N300 a tuntubeni ta wannan Number domin naiman ƙarin bayani 08133562798.

*MEEN@RT...✍🏻*
08133562798